QWARIN QASAR HAUSA: NAZARIN NAU'O'INSU DA TASIRINSU GA

ADABIN BAKA DA WASU AL'ADUN HAUSAWA.

NA

ASMA'U SULEIMAN.

SPS/10/MHA/00010.

AN GABATAR DA WANNAN BINCIKE DOMIN
CIKASA WANI VANGARE NA NEMAN DIGIRI NA BIYU
A FANNIN HAUSA (M.A. HAUSA)
A SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA
JAMI'AR BAYERO, KANO.

OKTOBA, 2015.

DECLARATION.

I hereby declare that this work is the product of my own research efforts. Undretaken under the supervision of Dr. Ibrahim Garba Satatima of the Department of Nigerian Languages, Bayero University Kano. The Research has not been presented and will not be presented elsewhere for the award of Degree or Certificate. All sources have been duly acknowledged.

ASMA'U SULEIMAN
SPS/10/MHA/00010.

.....
Signature and Date.

SADAUKARWA.

Na sadaukar da wannan aiki ga mahaifina marigayi Alhaji Sule Unguwar Alqali da fatan Allah ya jiqansa da rahama ya sa Aljannar Firdausi ce makomarsa, amin.

SHAFIN AMINCEWA.

Wannan aiki an gabatar da shi ne ga Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Kano, a qoqarin cikasa wani vangare na samun shaidar kammala karatun Digiri na Biyu a Harshen Hausa (M.A HAUSA). An gudanar da wannan aiki ne a qarqashin jagorancin Dr. Ibrahim Garba Satatima, wanda ya sami amincewar shugabanni kamar haka;

Dr. Ibrahim S.S. Abdullahi. .....

External Examiner. Signature & Date.

Dr. Ahmad Magaji. .....

Internal Examiner. Signature &Date.

Dr. Ibrahim G. Satatima. .....

Supervisor. Signature &Date.

Dr. Aliyu Mu'azu. .....

Head of Department. Signature & Date.

GODIYA.

Ina godiya ga Allah Subhanahu wata'ala da ya raya ni ya kuma ba ni lafiya da cikakken zarafi har na kammala wannan aiki. Godiya ta musamman ga Dr. Ibrahim Garba Satatima wanda a bisa jagorancinsa ne wannan aikin ya tabbata kamar yadda yake a haka. Na qaru qwarai da irin qoqarinsa da haqurinsa da kuma gyare-gyare da shawarwarin da ya riqa ba ni a duk tsawon lokacin da muka yi aiki da shi. Allah ya saka masa da alherinsa ya qara xaukaka, amin

Ina miqa godiya ta musamman ga malamina Dr. Ahmad Magaji, wanda shi ne ya duba wannan aiki a matsayin mai jarabawa na cikin gida (internal examiner) kuma ya saka ni a hanya tare da shawarwari domin ganin wannan aikin ya inganta, Allah Ya saka masa da alheri ya kuma yi masa buxi ga dukkan al'amuransa na rayuwa.

Godiya ta musamman ga Dr. Aliyu Mu'azu, Shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Kano. Na ji daxi qwarai da shawarwari da qarfafa guiwar da ya riqa ba mu har muka kai ga nasara a wannan aiki.

Ina godiya ga duk malamaina a Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero da ke Kano. Na qaru qwarai da irin gyare-gyare da shawarwari da suka bayar wanda ya taimaka aka cim ma nasara wajen kammala wannan aiki. Allah ya ja zamani kuma ya saka maku da alherinsa amin.

Na gode wa mutanen da suka taimaka ta hanyoyi daban-dabam har wannan aiki ya kammala. Godiya ta musamman ga Malam Bishir Aliyu Sallau Safana (Sarkin Aska) wanda ke aiki a Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adu'a, Katsina da Malam Nata'ala wanda ke aiki a Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke Katsina.

Haka kuma ina godiya ga mahaifiyata da maigidana, da 'ya'yana da 'yan uwana saboda haqurin da suka yi da ni a tsawon lokacin da na xauka ina wannan karatu. Haka kuma ina godiya ga dukkan abokan aiki da abokan karatu saboda shawarwari da qarfafa guiwa da suka riqa ba ni a xaukacin lokacin da na gudanar da wannan karatu. Na gode wa duk wanda ya taimaka ta kowace hanya, amma na manta ban ambaci sunansa ba, gaba xaya Allah ya saka wa kowa da alherinsa amin.

QUMSHIYA

Taken Bincike i

Declaration ii

Sadaukarwa iii

Shafin Amincewa iv

Godiya v

Qumshiya vi

Abstract xi

Tsakure xii

BABI NA XAYA.

SHARE FAGE.

1.0. Gabatarwa 1

1.1. Hasashen Bincike 2

1.2. Dalilan Bincike 2

1.3. Manufar Bincike 3

1.4. Iyakancewar Bincike 4

1.5. Naxewa 4

BABI NA BIYU.

BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA.

2.0. Gabatarwa 5

2.1. Kundayen Bincike 5

2.2. Bugaggun Litattafai 9

2.3. Maqalu da Mujallu da sauran Takardu 12

2.4. Naxewa 14

BABI NA UKU.

RA'I DA DABARUN GUDANAR DA BINCIKE.

3.1. Ra'in Bincike 15

3.2. Tattaro Ginshiqan Bayanai a kan Qwari da Adabi da Al'adu 16

3.2.1. Bibiyar Ayyuka kan qwari 16

3.2.2 Ziyartar Wuraren da ake kiwata ko samun Qwari 16

3.2.3 Waxanda aka yi Hira da su 16

3.3. Sauran Bayanai 17

3.4. Naxewa 18

BABI NA HUXU.

QWARI A QASAR HAUSA.

4.0. Gabatarwa 19

4.1. Qasar Hausa da Mutanenta. 19

4.2. Dabbobi da Qwarin Qasar Hausa 21

4.3. Ma'anar Qwari 21

4.4. Muhimman Rabo da Nau'o'in Qwari 24

4.4.1. Qwari na Tsandauri 24

4.4.1.1. Qwari na Gida. 24

4.4.1.2. Qwari na Daji 25

4.5. Qwari na Ruwa 26

4.6. Nau'o'in Qwari 26

4.6.1. Qwari Masu Yaxa Cuta 26

4.6.2. Qwari Masu Zama a Jikin Xan'adam 26

4.6.3. Qwari Masu Zama a Jikin Dabbobi 27

4.6.4. Qwari Masu Haxa Gari 27

4.6.5. Qwari Masu Vata Amfanin Gona 27

4.6.6. Qwari Masu Dafi 28

4.6.7. Qwari Masu Cin 'Yan'uwansu 28

4.7. Siffofin Jikin Qwari 28

4.8. Muhimman Halayen Qwari 30

4.8.1. Yaxuwar Qwari 30

4.8.2. Barbara 31

4.8.3. Haihuwar Qwari 32

4.8.4. Qwai 32

4.8.5. Qyanqyasa 33

4.8.6. Rikixa 34

4.8.7. Reno 36

4.8.8. Ire-iren Abincin Qwari 36

4.8.9. Kariya 38

4.8.10. Zamantakewar Qwari 40

4.9. Amfanin Qwari 41

4.10. Illolin Qwari 42

4.11. Kariya daga Qwari. 43

4.12. Naxewa 43

BABI NA BIYAR.

QWARI A ADABIN BAKA DA WASU AL'ADUN HAUSAWA.

5.0. Gabatarwa 44

5.1. Ma'anar Adabi. 45

5.1.1 Rabe-raben Adabi. 46

5.1.1.1. Adabin baka. 46

5.1.1.2. Rubutaccen Adabi. 47

5.2. Qwari a Labarun Zube. 47

5.2.1. Tasirin Qwari a Tatsuniyar Hausawa 47

5.2.2. Tasirin Qwari a Hikayar Hausawa. 56

5.3. Tasirin Qwari a Zantukan Hikima 59

5.3.1. Tasirin Qwari a Karin Maganar Hausawa 60

5.3.2. Tasirin Qwari a Kirarin Hausawa 65

5.3.3. Tasirin Qwari a Kacici-kacici 72

5.4. Qwari a Waqoqin Baka 73

5.5. Qwari a wasu al'adun Hausawa 81

5.5.1. Ma'anar Al'ada 81

5.6. Tasirin Qwari a Camfin Hausawa 82

5.7. Qwari a Ququwar Hausawa 85

5.8. Naxewa da Sakamakon Bincike 86

5.9. Matsaloli da Shawarwari 89

Manazarta 90

Rataye na 1. Wasu Tatsuniyoyi. 96

Rataye na 2. Wasu Hikayoyi. 110

Rataye na 3.Wasu Karin Maganganu. 112

Rataye na 4. Wasu Camfe-camfe. 114

Rataye na 5. Wasu Waqoqin Baka. 116

Rataye na 6. Tambayoyin Bincike 121

Rataye na 7. Hotunan Wasu Qwari 122

ABSTRACT.

The main objective of this research work titled “Insects in Hausa land: Their Types and Influence on the Traditional Literature and Cultures of the Hausa People” is to widen the knowledge of people on issues related to insects and the Hausa people which include their types, how they reproduce and their influence on the traditional literature and some cultures of the Hausa people. Using simple survey method the study investigated on the great influence of the insects on the Hausa people which make the Hausas to use their names or how they look and their habits in explaining their ways of life. The work focuses on some aspects of Hausa traditional literature which include folktales, fables, praise epithets, Hausa oral songs and some aspects of culture which include superstitious beliefs. The major findings of the study show that insects have great influence on the traditional literature and cultures of the Hausa people as survey shows that the names and habits of insects have been used in many aspects of traditional literature and cultures of the Hausa people

TSAKURE.

Manufar wannan bincike ita ce don a faxaxa ilimin jama’a ta hanyar fito da qwari a mahangar Bahaushe tare da nau’o’insu da yadda suke yaxuwa da kuma yadda suka yi ruwa suka yi tsaki a adabin baka da wasu al’adun Hausawa. Ta amfani da hanyar tattara bayanai aikin ya mayar da hankali a kan nuna yadda yanayin zamantakewa ya sa aka sami alaqa mai qarfi a tsakanin Hausawa da wasu nau’o’in qwari da ke a qasar Hausa har ta sa Hausawa suke amfani da sunayensu da siffofinsu ko halayyarsu cikin kyakkyawan azanci don su bayyana al’amuran rayuwarsu. Aikin ya kalli vangarori uku na adabin baka na Hausa waxanda suka haxa da zube da zantukan hikima da waqoqin baka na Hausa da al’adar Hausawa ta camfi da ququwa. Muhimmin abin da binciken ya gano shi ne akwai alaqa mai qarfi tsakanin Hausawa da qwari wadda hakan ta sa aka yi amfani dasu a vangarori na adabin baka da al’adun Hausawa.

BABI NA XAYA

SHARE FAGE.

1.0. Gabatarwa.

Wannan aiki mai suna “Qwarin Qasar Hausa: Nazarin Nau’oinsu da Tasirinsu a Adabin Baka da Wasu Al’adun Hausawa”, ya qunshi bayanai game da qwari da ke qasar Hausa don su halittu ne masu yawan gaske kuma suna da saurin yaxuwa. Hasashe ya nuna cewa kusan kashi saba’in da biyar cikin xari (75%) na halittu masu rai da ke a duniya qwari ne, sannan kuma da ba su mutuwa da tuni sun gaje duniya. (Encarter Software, 2007)

Masu iya magana kan ce ‘kowane abu mai rai ba ya rasa amfani’. Wannan haka yake domin kuwa duk wanda yake ganin qwari haka nan kara zube, zai xauka cewa haka nan suke zaune a duniya ba tare da wani tsari, ko amfani ba. Qwari na daga cikin halittun da za a iya samu a ko’ina cikin duniya. Akwai su a tudu, da wasu a cikin ruwa masu kamanni daban-dabam. Akwai qwarin da ke bin qasa suna tafiya da qafafunsu kamar tururuwa da gwano da kunama. Sannan akwai masu tashi da fukafukai kamar quda da zirnako da barkonon tsohuwa da sauro da zuma. Haka kuma akwai waxanda sai lokacin damina ake ganinsu kamar su ja-na-kuka da shinge da matar malam da kunamar gero. Daga cikin qwari akwai ‘yan qanana kamar quma, akwai waxanda aka halicce su babu fukafukai sai dai wutsiya da tsayin jiki. Akwai waxanda fukafukansu ke da tsayi har ya rufe masu gadon baya kamar fara da kyankyaso.

Nazarin yana xauke da bayanai a kan amfani da illolin qwari, domin daga cikinsu akwai masu amfanarwa qwarai da gaske, saboda Allah Subhanahu Wata’ala kaxai Ya san iyakacin amfaninsu, kuma dai ai ilimi ya fi qasa yawa. Akwai bayanai da aka kawo game da tasirin qwari ga adabin baka na Hausa inda aka fito da yadda qarfin alaqa ta sa qwarin suka yi naso cikin al’amura

masu yawa na Hausawa ko da yake da ma mun san duk rayuwa zama ce ta cuxe ni, in cuxe ka.

Wannan babin ya qunshi bayani a kan hasashe da dalilai da manufa da iyakancewa na wannan bincike.

1.1. Hasashen Bincike.

Hasashe na nufin kintacen abin da zai faru bayan an kammala wani abu. Saboda haka hasashe na kai tsaye da ake ganin za a cimmawa bayan an kammala wannan bincike ya haxa da:

1. Sanin wasu qwari da ke a qasar Hausa dangane da nau'o'insu da sifofinsu da wasu muhimman halaye dangane da rayuwarsu.
2. Gano irin alaqar da ke tsakanin qwari da al'ummar Hausawa wadda ta haifar da tasiri tsakaninsu, har Hausawa suke amfani da sunayensu ko halayensu ko sifofinsu wajen gina vangarorin adabinsu na baka da wasu al'adunsu.
3. Shin wane irin zama ne tsakanin qwari da Hausawa da ya sa har aka sami irin wannan tasiri mai qarfi tsakaninsu.

1.2. Dalilan Bincike.

Dalili na nufin sanadi ko hujja, ko abin dogara da ta sa aka yi abu. Dangane da haka, kamar sauran makamantan binciken da suka gabata a kan fannoni na ilimi daban-dabam, shi ma wannan ba zai rasa dalilan da suka sa aka gudanar da shi ba. Saboda haka daga cikin dalilan da suka haifar da gudanar da wannan binciken akwai:

1. Binciko da fito da irin tasirin da qwarin qasar Hausa suka yi ga adabin baka na Hausawa.

2. Fito da tasirin qwarin qasar Hausa wajen gina wasu al'adun Hausawa.

3. Fitar da dabarun rayuwa da Hausawa suke koyo daga qwari.

4. Qara nazari da bincike bisa ga abubuwan da magabata da masu nazari suka kawo game da qwari don ba da gudunmuwa wajen faxaxa ilimi da bunqasa shi, sannan a buxe qofa ga sauran xalibai don su xora bincike a kan wannan da ake qoqarin aiwatarwa

1.3. Manufar Bincike.

Idan muka koma kan manufar wannan bincike za a ga cewa bisa la'akari da ayyukan da mutane suka yi a rayuwar yau da kullum, an fahinci kowane mutum yana da manufar da ke cikin ransa wadda ta sa yake aiwatar da abu. Masana da manazarta sun gabatar da ayyuka gwargwado a kan adabi da al'adun Hausawa. Yawanci a waxannan nazarce-nazarce an fi mayar da hankali kan fito da abubuwan da suka shafi al'adun aure da haihuwa da mutuwa da nazarin abubuwan da suka shafi addinin gargajiya waxanda suka shafi sihirce-sihirce da tsubbace-tsubbacen Hausawa. A nan na lura da cewar an kau da kai game da rayuwar sauran halittun da ke raye a bisa qasa, saboda haka manufar wannan bincike ita ce nazartar qwarin da ke rayuwa a qasar Hausa tare da fito da tasirin da suka yi ga adabi da wasu al'adun Hausa gwargwadon hali, saboda haka:

1. Nufin wannan bincike ne ya faxaxa ilimin jama'a ta hanyar fito da qwari a mahangar Bahaushe, tare da nau'o'insu, da hanyoyin da suke yaxuwa da yadda suke kare kansu daga haxari da kuma yadda suka taka rawa a adabin baka na Hausawa.

2. Wata manufar ita ce tantance irin rawar da qwari suka taka a al'adun Hausawa.

3. Binciken zai ba da gudunmuwa wajen adana tarihi, tun da duk abin da aka binciko kuma aka rubuta, matsayin an adana shi ne, sannan manazarta masu yawa za su iya amfana da shi.

4. Binciken zai taimaka wajen fito da amfanin qwari ga al'umma ta hanyar bayyana su gwargwadon hali don jama'a su sani kuma su amfana da ximbin amfanin da suke xauke da su. Yin haka zai amfanar qwarai da gaske.

5. Binciken zai fito da yadda ake nuni cikin rayuwa daga labaru da aka danganta da qwari wadda hanya ce ta ba al'umma tarbiyya a cikin raha da nishaxi.

1.4. Iyakancewar Bincike.

Qwari na da muhimmanci qwarai da gaske a rayuwar al'umma, wannan shi ya sa gudanar da nazari a fannin ke da faxin gaske. Wannan bincike an shirya shi yadda zai kalli nau'o'in qwari daban-dabam waxanda suke a qasar Hausa da tasirinsu ga adabi da al'adun Hausawa, ta hanyar duba yadda yanayin zamantakewa ya sa aka sami alaqa mai qarfi har ta sa Hausawa suke amfani da sunayensu ko siffofinsu ko halayyarsu cikin kyakkyawan azanci don su bayyana al'amuran rayuwarsu. Aikin ya kalli wasu vangarori na adabin baka na Hausa waxanda suka haxa da zube da zantukan hikima da waqoqin baka da kuma wasu daga cikin al'adun Hausawa. Aikin da misalan da za a kawo don kafa hujja zai taqaita ne ga ire-iren qwarin da Bahaushe ya xauka su ne qwari.

1.5. Naxewa.

Wannan babi na share fage ya qunshi bayanai na share fage a wannan bincike. A ciki an kawo hasashe na binciken da dalilan da suka sa aka gudanar da binciken da manufa da kuma iyakancewar binciken. A taqaice babin ya qunshi bayanai na share fage game da binciken.

BABI NA BIYU.

BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA.

2.0. Gabatarwa.

A wannan babi an yi bitar wasu ayyuka madanganta wannan da suka gabata waxanda ake ganin suna da alaqa da wannan bincike, kuma za su taimaka qwarai da gaske wajen haxa aikin in sha Allah.

Masana da manazarta sun gabatar da ayyuka mabambanta dangane da fannoni waxanda suka shafi ire-Kiren halittu da nau'oinsu da halayensu, waxanda idan aka yi nazarinsu za su taimaka wa wannan bincike. Ganin cewa nazarin ya shafi qwari da tasirinsu ga adabin baka da al'adun Hausawa na gargajiya, babin zai mayar da hankali wajen binciko ayyukan da suke da alaqa da su domin samar wa aikin makama. Ire-iren waxannan ayyuka an yi su ne domin samun qarin ilimi a fasalin kundayen bincike a zanguna daban-dabam tun daga digirin farko har zuwa na uku. Wasu ayyukan an yi su ne a bugaggun litattafai, da maqalu da sauran takardu da aka gabatar a fagen ilimi. Duba waxannan ayyuka don samun haske da jagora domin yin nazari abu ne mai matuqar muhimmanci da amfani. A wannan babin za a duba kundayen bincike da litattafai da mujallu da maqalu domin samun taimako da qaruwa.

2.1. Kundayen Bincike.

Gora (1989) a binciken da ya gudanar na kundin neman Digiri na Biyu a Jami'ar Bayero Kano (M.A Hausa), mai take "Camfi a Al'ummar Hausawa" ya fara da kawo ma'anar camfi daga ra'ayoyin masana daban-dabam, sannan ya yi bayani kan asali da yadda camfi ya sami zama a cikin al'adun Hausawa, da muhimmancinsa ga rayuwar waxanda suka yarda da shi. Manazarcin ya kawo misalan camfe-camfe masu yawa.

Alaqar aikin Gora da wannan shi ne daga cikin misalan camfe-camfen da ya kawo har da waxanda suka shafi qwari, sai dai kuma sun banbamta don a wannan nazarin za a duba tasirin qwari ne a adabin gargajiya da wasu al'adun Hausawa.

Sharifai (1990), a binciken da ya gudanar na kundin neman Digiri na Biyu a Jami'ar Bayero Kano (M.A Hausa), mai suna "Take da Kirarin Sana'o'in Gargajiya: Ma'anarsu da Muhimmancinsu ga Rayuwar Hausawa". Manazarcin ya kawo ire-iren sana'o'i na gargajiya da Hausawa ke yi da irin abubuwan da suka qunsa na game da harshe da adabi da al'adu. Manazarcin ya fito da ma'ana da muhimmancin kirari ga rayuwar Hausawa.

Abin da ya alaqanta aikin da wannan shi ne bayanan da suka danganci kirarin da ake yi wa wasu sana'o'in gargajiya. Abin da ya banbamta su kuma shi ne a wannan za a kawo tasirin qwarin ga wasu vangarorin adabin baka wanda ya haxa da kirari amma wanda ya shafi qwari.

Dogara (1992) a kundin bincikensa na neman digiri na xaya a Jami'ar Bayero Kano (B.A Hausa), mai take "Namun Daji a Qasar Hausa: Ire-irensu da magungunan da ake samu daga gare su". Ya kawo bayanai a kan Namun daji iri-iri tare da yadda suke, da wuraren da ake samun su, da ire-iren magungunan da ake samu daga gare su. Binciken ya tavo taqaitaccen bayani kan qwari, ya bayyana yadda siffarsu take da taimakon da ake samu daga jikinsu ta fannin magani.

Binciken na da 'yar alaqa da wannan saboda an kawo bayani kan qwari domin daga cikinsu akwai waxanda ke rayuwa a dazuzzuka dabam-dabam. Sai dai bai ba da karfi kan su ba, domin ba a kan su ake nazarin ba. Wannan kuwa ya shafi qwari ne da tasirin su ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Hassan (1995) ya gabatar da nazari mai suna "Qwari da Muhimmancinsu ga rayuwar al'umma", don neman digiri na xaya a Jami'ar Bayero, Kano (B.A

Hausa). A kundin, manazarcin ya kawo bayani a kan qwarin ruwa da na tudu masu qafafu da masu Jan ciki. Yadda halayyarsu take, da amfaninsu ko rashin amfaninsu ga rayuwar al'umma. Sannan kuma ya kawo ire-iren abincinsu da muhallansu. Aikin na da alaqa da wannan domin ko ya fito da wasu abubuwa da suka shafe shi. Bambancin da ke tsakaninsu shi ne a wannan nazarin za a kawo bayanai a kan al'amura mabambanta da suka shafi qwari. Kamar yadda suke yaxuwa da yadda suke rikixa da yadda suke kare kansu daga abokan gaba da kuma tasirinsu ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Mahe (2008), ya gudanar da bincike mai suna "Duniyar Dabbobi a cikin Al'adun Hausawa" don samun digiri na biyu a Jami'ar Bayero Kano (M.A Hausa). Aikin ya qunshi bayanai kan dabbobi. Manazarcin ya raba dabbobi zuwa gida-gida, daga cikin gidajen akwai qwari. Kundin ya qunshi taqaitaccen bayani kan qasar Hausa da al'ummarta, sai ire-iren dabbobi waxanda suka haxa da na gida da na daji. Sai xan taqaitaccen bayani a kan qwari inda aka kawo ma'ana da rabe-rabensu.

Alaqar binciken da wannan aikin shi ne bayanin da aka kawo kan qwari ta hanyar kawo ma'anarsu a taqaice. Abin da ya raba aikin da wannan nazarin shi ne a wannan za a yi bayani ne kan tasirin qwari ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Isa (2009) a kundin bincikensa na neman digiri na biyu a Jami'ar Bayero (M.Sc Microbiology) mai take "Evaluation of Anti microbial Synergistic. Effect of Black Cumin (Nigella Satava) Seed Extracts and Honey on Some Clinical Bacterial Isolates". Ya kawo bayani a kan qwaron qudan zuma da halayyar rayuwarsa. Ya bayyana irin yadda suke zama tare da halayyarsu ta gama qarfi da qarfe don samun ci gaba.

Alaqar binciken da wannan shi ne bayanan da suka shafi qwaron qudan zuma, sai dai kuma sun yi hannun riga don a wannan za a fito ne da tasirin qwarin ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Sakina Adamu Ahmad (2011), ta gudanar da bincike mai take" Gurbin Qwari a Magungunan Gargajiya na Hausawa" don samun digiri na biyu (M.A Hausa) a Jami'ar Usmanu Xanfodiyo Sokoto. A nazarin ta yi bayani kan qwari da irin magungunan da ake samarwa daga gare su. Nazarin ya fito da magungunan gargajiya na Bahaushe waxanda ake amfani da qwari wajen haxa su. Ya kuma kalli magungunan gargajiya ta fuskar matsalolin da suke warwarewa kamar warkarwa da cutarwa da kariya da biyan buqatun rayuwa.

Aikin Sakina da wannan sun yi tarayya a vangaren bayanai da suka danganci qwari. Wannan kamanceceniya tsakanin bayanan da suka danganci qwari ya zama dole saboda rayuwar zuri'ar qwari iri xaya ce a ko'ina cikin duniya ta fuskar haihuwarsu da rikixarsu da matakan rayuwarsu da tsawon rayuwarsu da amfaninsu da illolinsu. Kuma irin qwaron da ake samu a wani gari na qasar Hausa shi za a samu a wani garin, kuma shi za a samu a wani vangaren da ba qasar Hausa ba. Sai dai ana iya samun bambanci na launin jiki saboda yanayin wurin zama.

Wannan aikin mai suna"Qwari a Qasar Hausa: Nazarin Nau'oinsu da Tasirinsu ga Adabin Baka da wasu al'adun Hausawa" ya yi hannun riga da na Sakina mai suna "Gurbin Qwari a Magungunan Gargajiya na Hausawa". Domin a wannan an yi bayani ne kan yadda zaman tare tsakanin Hausawa da qwari ya jaza yin amfani da sunayensu ko siffofinsu ko halayensu ko yanayin rayuwarsu cikin adabinsu na baka da wasu al'adunsu. Daga cikin vangarorin adabin baka da za a nazarta a wannan aiki akwai tatsuniya da hikaya da kirari da waqar baka a vangaren al'adu kuma za a duba camfi da ququwa.

2.2. Bugaggun Litattafai.

East da Imam (1949), sun rubuta littafi mai suna *Ikon Allah* (littafi na huxu) qwari da tsutsotsi: Labarin halitta iri-iri ta cikin duniya. Littafin ya qunshi bayanai a kan halittu iri-iri na duniya. An yi tsokaci kan qwari daban-dabam, yadda suke rayuwa da ire-iren abincinsu da halayyar zamantakewarsu da sauransu. Sun kawo amfaninsu ga xan'adam da illolin wasu daga cikinsu. Littafin ya tattauna al'amura masu yawa dangane da qwari sai dai bai nuna tasirinsu ba ga Hausawa ta vangaren adabin baka da al'adunsu.

Littafin da Madauci da wasu (1968) suka rubuta mai suna *Hausa Customs* ya yi bayani ne a kan wasu al'adun Hausawa waxanda suka shafi aure da haihuwa da mutuwa da camfi da karin magana. Aikin ya haxu da wannan ta vangaren karin magana da camfi sai dai ba a kevance su ba ga qwari.

Youdeowei (1975), ya rubuta littafi mai suna *Our Common Insects*, littafin na xauke da bayanai kan qwari waxanda ke zaune a gidaje da sauran wurare. Marubucin ya kawo yadda siffar qwari take da tarihin rayuwarsu da amfaninsu. Aikin na da alaqa da wannan a vangaren bayanai da suka shafi qwari. Amma sun bambanta don bai alaqanta qwarin da wata al'umma ba.

Boorman (1981), ya rubuta littafi mai suna *The West African Insects*. A littafin ya yi bincike mai zurfi a kan qwari. Ya bayyana yadda tsarin jikinsu yake da yadda suke rayuwa, rabe-rabensu da dabarun da ake bi idan za a kama su da hanyoyin da za a bi don kare kai daga masu cutarwa daga cikinsu. Alaqar da ke tsakanin littafin da wannan nazarin shi ne bayanai da suka shafi qwari.

Umar (1982), a littafin da ya rubuta mai suna *Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya* ya yi qoqarin fayyace fagen nazarin ta nuna kafuwar al'umma da yadda al'adu ke samuwa. Ya bayyana nau'o'in al'adun gârgajiya da muhimmancinsu. Kuma ya kawo bayani game da adabin baka da rukunnansa da muhimmancinsa ga rayuwar al'umma. Haka kuma ya yi sharhi kan kowane

rukuni na adabin baka tare da misalai don fito da al'adun da suka qunsa. Wannan bincike ya tavo wannan nazari domin ya yi sharhi a kan adabin baka sai dai bai alaqanta adabin da qwari ba.

Stone da Wasu (1991), a littafinsu mai suna *New Biology for Senior Secondary School*, sun yi bayanin rayuwar qwari tun daga haihuwarsu har zuwa mutuwa. Sun mayar da hankali kan rabe-raben qwari da yadda jikinsu yake, yadda suke girma da dangantakarsu da mutane da amfanin gona. Bayanan da suka danganci qwarin shi ya alaqanta littafin da wannan aikin. Sai dai a wannan nazarin za a alaqanta qwarin da adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Muhammad (2003), ya rubuta littafi mai suna *Adabin Hausa. Aciki* ya tattaro bayanai da suka jivanci adabin Hausa irin su almara da qissa da hikaya da zaurance. A taqaice dai littafin ya qunshi wasu sassa na adabin baka da wasan kwaikwayo da yadda za a nazarci rubutattun waqoqin Hausa a taqaice. Alaqar littafin da wannan aikin shi ne abin da ya shafi adabin baka. A wannan kuwa za a fito da tasirin qwari ne a adabin baka na Hausa.

Vines and Rees (1971), a littafin da suka rubuta mai suna *Plant and Animal Biology* sun zavi wasu qwari suka yi bincike mai zurfi a kansu. Sun bayyana zuri'ar da kowane qwaro ya fito, da halayyarsa da wurin da za a iya samun shi da yadda siffar jikinsa take, yadda suke yaxuwa da muhimmancin su. Alaqar aikin da wannan shi ne bayanai da suka shafi qwari. Abin da ya bambanta su kuma shi ne ba su alaqanta qwarin da adabin baka da al'adun Hausawa ba.

Usman (2005), littafin da ya rubuta *Taskar Tatsuniyoyi* na 1-5 na xauke da tatsuniyoyi daban-dabam waxanda aka yi amfani da qwari a cikinsu. Misali, Tatsuniyar gizo da sarki, da sauran irin su masu yawa. A gabatarwar littafin marubucin ya kawo tarihin tatsuniyoyi a duniya. Daga nan ya gangaro zuwa ga shekarar da aka fara rubuta tatsuniyoyi cikin harshen Hausa da ajami da kuma

haruffan boko. Littafin na da alaqa da wannan aikin saboda tatsuniyoyin da ya qunsa. Sai dai a wannan nazarin za a duba wasu rassan adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

Bunza (2006), ya rubuta littafi mai suna *Gadon Fexe Al'ada. A* littafin ya fexe al'adun Hausawa waxanda suka da camfi da bori da qohi da ququwa dangane da yadda ake gudanar da su. Da waxanda suka danganci abubuwan bautarsu da yadda suka yi imani da su. A littafin Malam ya danganta wasu al'adun Hausawa da qwari, ta hanyar fito da ire-iren qwarin da Hausawa suka yarda suna yin qohi, da waxanda ke da ququwa da kuma waxanda suka camfa. Wannan littafin zai taimaka wa wannan aikin domin ya kawo bayanai kan wasu al'adun Hausawa da suka shafi qwari. Sai dai bai tavo sauran sassan adabin baka ba.

Bamalli (2007), ya rubuta littafi mai suna *Bala da Babiya*, Lafiya Uwar Jiki. A ciki ya yi bayanin wasu daga cikin qwari. A Littafin ya kawo taqaitaccen bayani a kan sauro, da quda da irin cututtukan da suke kawo wa mutane, yadda suke yaxa su da yadda za a magance su. Alaqar littafin da wannan aikin shi ne bayanai da ya kawo kan wasu qwari sai dai ba a alaqanta qwarin da adabin baka da al'adun Hausawa na gargajiya ba.

Xanyaya (2007), ya rubuta littafi mai suna *Karin Maganar Hausawa*. A farkon littafin marubucin ya kawo ma'anar karin magana da amfaninta. Ya bayyana yadda Bahaushe ya xauki Karin magana da muhimmanci sosai don ko yara da manya duk suna amfani da ita kuma kowane na yin hakan ne don ya kare ra'ayinsa ko ya lurar da abokin maganarsa. Littafin ya qunshi karin maganganu guda dubu biyu (2000). Abin da ya alaqanta littafin da wannan aikin shi ne daga cikin karin maganganun akwai waxanda suka shafi qwari sai dai aikin ya tsaya ne kawai ga karin maganganu.

Xangambo (2008), ya rubuta littafi mai suna *Rabe-raben Adabin Hausa* (sabon tsari). A littafin ya bayyana ma'ana da rabe-raben adabi. Marubucin ya raba tsakanin adabi da al'ada sannan ya kawo rabe-rabensu a jimlace. Ya yi bayani dalla-dalla a kan azuzuwan adabin gargajiya da na zamani. Wannan littafin zai taimaka wa aikin da ake gudanarwa saboda za a duba vangarorin adabin gargajiya don a fito da tasirin qwari ga al'ummar Hausawa.

2.3. Maqalu da Mujallu da Sauran Takardu.

Idan aka koma vangaren maqalu da mujallu, bitar ta samu binciko waxanda za su taimaka wa aikin. Daga ciki akwai:-

Ibrahim (ba shekarar wallafa), ya rubuta maqala mai suna "Adabin Gargajiya na Hausa kafin da kuma bayan Musulunci" inda ya fito da asalin kalmar adabi da rabe-rabenta. Ya xauki wasu vangarori na adabin baka wato kirari da tatsuniya da karin magana da salon magana da kacici-kacici da waqoqin baka, ya kawo misalan waxanda Hausawa suka yi kafin da bayan zuwan addinin musulunci. Alaqar maqalar da wannan aikin shi ne misalan adabin baka da ya kawo. Sai dai marubucin bai alaqanta adabin bakan da qwari ba.

Qaraye (1978), ya rubuta maqala mai suna "Beyond the Illusive Cobwebs of the Spider' wadda ta fito a mujallar "Studies in Hausa Language, Literature and Culture" inda ya kawo ma'anar gizo wanda ake amfani da shi a tatsuniya kamar yadda masana daban-dabam suka kawo. Ya bayyana halayen gizo na dabara da wayo, sai kuma ya kawo bayani kan gizo-gizo da halayen shi na wayo da dabara. Ya nuna Hausawa sun alaqanta gizo da gizo-gizo ne saboda halayyarsu da ta zo iri xaya. Daga qarshe dai ya nuna cewa, gizo-gizo ba shi ne gizo ba. Alaqar takardar da wannan aikin shi ne bayanin da aka kawo kan gizo da gizo-gizo sai dai aikin bai tavo adabin gargajiya ba.

Tudun Wada (1981), a maqalar da ya rubuta mai take “Tsari da Ma’anar Karin Maganar Hausa” wadda ya gabatar a taron qara wa juna ilimi. A takardar ya bayyana ma’ana da muhimmanci da tsare-tsaren karin magana tare da misalai. Daga qarshe ya xauki wasu daga ciki ya yi sharhi. Daga cikin vangarorin adabin baka da za a duba a wannan aiki har da karin magana amma waxanda suka danganci qwari.

Daba (1997), a maqalar da ya rubuta mai take “Linguistic taboos and Animal Categories as Verbal Abuse Compliment in Hausa” wadda ta fito a mujallar Harsunan Nijeriya. Ya bayyana cewa Hausawa na amfani da qirar jiki ko halayyar qwaro ya shiryar da ita cikin vangarorin hikima don su qwarzonta ko muzanta wani ta hanyar siffanta shi ko halayyar shi da wani qwaro. Ya kawo misalan wasu daga cikin qwarin da Bahaushe ke amfani da sunayensu don su nuna cewa halayyar mutum ko siffar jikinsa na da alaqa da ta qwaron. Alaqar takardar da wannan aikin shi ne dukkansu sun duba Hausawa ne da qwari sai dai a wannan za a faxaxa ta hanyar duba wasu sassan adabin baka da al’adun Hausawa.

Bunza (1999) ya rubuta da maqala mai take “Raxaxi da Zogin Cuta a Ma’aunin Bahaushe (tsokaci cikin waqar kunama ta Garba Mai Tandu)’, wadda ta fito a mujallar Hausa Studies. Marubucin ya fayyace al’amura dangane da kunama da irin sababin da ke tattare da ita. Ba kunamar kaxai ba har da sauran qwari ‘yan uwanta masu cutarwa. Wannan aikin zai kawo misalan waqoqi na baka waxanda aka yi amfani da qwari wajen gina su.

Vavura (2008) ya rubuta wata maqala mai take “Ceto Gizo daga Gizo-Gizon Al’adun Duniya”, wadda ya gabatar a 2nd International Conference on Hausa Studies. Inda ya bayyana cewa dabbobi da qwari sun yi tasiri matuqa a cikin zukatan al’umma. Ya qara cewa lalle gizo-gizo bai tava fitowa ba a cikin kowanne labari ko sau xaya kamar yadda sauran dabbobi ke fitowa. A maqalar

ya kawo hujjojin da suka warware cewa gizo-gizo ba shi ne gizo ba. Ya ce Gizo kalma ce da take fassara wani tunani na Bahaushe da ya siffanta tunaninsa da yake zuwa a cikin tatsuniyoyinsa. A qarshe marubucin ya nuna yadda wasu suke nema su jirkita tunanin ‘ya’yan Hausawa ta hanyar kamanta Gizo da gizo-gizo. Ya ba da ma’anar gizo-gizo qwaro ya kuma kawo ma’anar gizo na adabin Hausa da cewa su biyun abubuwa ne daban-dabam.

Mu’azu, A. H. (2009) a takardar da ya gabatar domin ci gaba da binciken kundin digiri na biyu a Jami’ar Usmanu Xanfodiyo Sokoto mai suna “Gurbin Dabbobi da Qwari a cikin Waqoqin Baka na Hausa”, ya kawo yadda maroqan baka ke amfani da dabbobi wajen dabbantarwa a cikin waqoqin baka. Aikin ya taqaita ne ga waqoqin baka kaxai bai tavo sauran vangarorin adabi da al’adun Hausawa ba.

Waxannan su ne wasu daga cikin ayyukan magabata da suka qunshi ayyuka masu ximbin amfani waxanda za su taimaka wa wannan binciken ta hanyoyi dabam-daban, kuma duk suna da alaqa da shi ko ta kai tsaye ko a kaikaice. Sai dai wannan zai ba da qarfi ne ga tasirin qwari ga adabin baka da al’adun Hausawa, saboda haka za a fito da alaqar da ke tsakaninsu da al’ummar Hausawa wadda ta sa suke amfani da su cikin adabinsu na baka da al’adu tare da misalai.

2.4. Naxewa.

A babin an bayyana ayyukan da suka gabata waxanda suke da alaqa da wannan nazarin. Waxannan ayyuka sun haxa da kundayen bincike da bugaggun litattafai da maqalu da mujallu da sauran takardu waxanda suka taimaka wajen gudanar da nazarin.

BABI NA UKU.

RA'I DA DABARUN GUDANAR DA BINCIKE.

3.1. Ra'in Bincike.

Wannan bincike an xora shi a kan mazhabar Yahaya ta nazarin adabin gargajiya daga littafin Gusau (2008) mai suna 'Dabarun Nazarin Adabin Hausa'. Farfesa Yahaya ya bayyana za a iya duba adabin gargajiya fagen nazari ta fuskar tsari da aiwatarwa da kuma xaixaiku. Matakan da za a yi amfani da su wajen fexe adabin baka na zube sun haxa da Tubalan gini da Tasiri da Masu yi da lokacin yi da Zubi da Tsari da Hikimomin da ke ciki. Wato idan za a fexe adabin baka ana duba su ta hanyar fito da tubalan gininsu kamar mutane da dabbobi da qwari da aljannu da sauransu. Sannan ana duba tasirin abin ga al'umma da waxanda suke yi. Kamar yara ko samari ko dattijai da sauransu. Haka nan ana duba lokaci da wurin yi. Misali lokacin shaqatawa ko lokacin hira. Sai zubi da tsari wanda ke fayyace ko kara zube aka gabatar da adabin ko kuma mai neman ba da amsa ko ra'ayi ne da sauransu.

Haka kuma za a dubi mazhabar Gusau (2008) daga littafinsa mai suna Dabarun Nazarin Adabin Hausa. Inda aka yi amfani da hanyar da ya fito da ita wadda ta shafi dabaru da hikimomin yi wa waqar baka nazari da sharhi masamman a vangaren adon harshe irin su kamantawa da siffantawa da dabbantawa da sauransu.

Haka nan an dubi hanya mai nuni da ra'in Ibrahim daga littafin Gusau (2008) mai suna Dabarun Nazarin Adabin Hausa. Ra'in ya bayyana hanyoyin nazarin al'adun Hausawa da tasirin addinin musulunci a kansu.

3.2. Tattaro Ginshiqan Bayanai a kan Qwari da Adabi da Al'adu.

Duk wani bincike da ake son cimma nasara wajen aiwatar da shi dole ne a samu ingantattun hanyoyi da za a bi don taimaka masa, saboda haka ne aka bi wasu hanyoyi da dabaru don gudanar da shi. Waxannan hanyoyin kuwa sun haxa da:

3.2.1. Bibiyar Ayyuka kan Qwari.

1. Hanyar nazarin zaune, wato nazartar litattafai na xab'i da kundayen digiri da na shaidar kammala manyan makarantun kwalejojin ilimi da makarantun kimiyya da fasaha daban-dabam da maqalu da mujallu waxanda ko dai sun shafi nazari qwari ko kuma suna da wasu bayanai masu alaqa da adabi ko al'adun Hausawa na gargajiya. Waxannan kundaye da litattafai za su taimaka wajen ganin abin da magabata suka yi musamman dangane da inda aikin ya sa gaba. Za a same su ne a xakunan karatu da duk wuraren da hannuwa za su sami kaiwa gare su.

3.2.2. Ziyartar Wuraren da ake Kiwata Ko Samun Qwari.

Wata hanya kuma da ake ganin za ta taimaka wajen ginuwar wannan aiki shi ne, ziyartar cibiyoyin da ake nazarin dabbobi na wasu jami'o'i da manyan makarantu. Za a kai ziyara gidan kiwata dabbobi da gonaki da qauyuka da sauran wurare, don samun bayanai ingantattu game da qwari. Da nazartar qwarin don gane yadda suke a zahiri da wasu muhimman al'amura dangane da su.

3.2.3. Waxanda aka yi Hira da su.

An bi hanyar yin hira da mutane daban- dabam. Misali mafarauta da manoma da masana da manazarta da masu aiki a gidan kiwata dabbobi da sauran jama'a don samun bayanai da jin ra'ayoyinsu game da qwari da tasirinsu ga adabin baka da al'adun Hausawa. Daga cikin mutanen da aka yi hira da su

akwai Malam Ado wanda aka yi hira da shi a garin Ajiwa a ranar 24-04-2013. Da Malam Nata'ala malami a Kwalejin Ilimi ta Tarayya a garin Katsina a ranar 04-03-2013. Da Malam Garba a Kasuwar Tashar Mangwaro a ranar 06-02-2013. Da Malam Lawal Rimaye a garin Rimaye a ranar 03-07-2013. Da Malam Muhammadu Tukur Mafarauci a garin Vatagarawa a ranar 05-02-2014. Da Mr. Okeke Okechukwu Cyril Shugaban Sashen koyar da harshen Igbo a Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke garin Katsina a ranar 04-04-2014. Da Malam Yakubu Safana a garin Safana a ranar 07-03-2014. Da Hajiya Hassu a Unguwar Qofar Qaura a garin Katsina a ranar 04-04-2014 da Malama Umma Nura a Unguwar Sabuwar Unguwa a ranar 13-04-2014. Da Malama Binta a Unguwar Kanti a garin Kankiya a ranar 13-02-2013. Da Hajiya Rabi Liadi a makarantar Kimiyya da Fasaha ta Hassan Usman a garin Katsina a ranar 12-05-2014. Da Hajiya Aisha a qofar Kabuga, Kano a ranar 16-09-2015

3.3. Sauran Bayanai.

An yi amfani da takardun tambayoyi da aka rubuta da harshen Hausa waxanda aka rarraba wa wasu Hausawa a sassa daban-dabam na qasar Hausa. An rarraba waxannan takardu ga maza da mata da matasa da dattawa.

Haka kuma an yi qoqarin ganin an nemi bayanai a duk inda aka ga ya dace idan buqatar hakan ta taso domin cimma manufa. A qoqarin samun bayanan ne na gano cewa ba cikin Adabin Hausawa kaxai qwari suka yi tasiri ba. Sun yi tasiri cikin adabin wasu al'ummu, inda su ma suke amfani da sunayensu ko halayyarsu ko siffofinsa wajen gina adabinsu na gargajiya. Misali daga hirar da na yi da Mr. Okeke, malami a Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke Katsina ya bayyana min cewa a Qabilar Igbo suna amfani da Qwari su gina adabinsu na gargajiya kamar tatsuniya da karin magana da waqoqi. Ya ba da misalin wata tatsuniya mai suna "Mbe na Ududa" a Hausa sunan tatsuniyar shi ne "Kunkuru da Gizo-gizo" (M.O.O.C. 04-04-2014).

A wurin Yarbawa ma haka abin yake domin su ma qwari sun yi tasiri cikin adabin su kuma suna amfani da sunayensu ko kamanninsu ko halayensu wajen gina adabinsu na gargajiya. Misali daga wannan karin maganar “kokoro tonje efa ara efo lowa”, wadda ke nufin “ qwaron da ke cin alayyaho a jikin alayyahon yake”(H.R.L. 12-05-2014).

A harshen Turanci ma haka abin yake don su ma qwari na cikin tubalan da suke gina karin maganarsu. Misali daga ciki akwai:

Ants in your pants—wanda ke nufin qarfen qafa.

Knee high to a grasshopper --- wanda ke nufin xaukar dala bag ammo.

Catch more flies with honey than with vinegar-jifar tsuntsu biyu da dutse xaya.

Bee in your bonnet -iya kamun lude.

3.4. Naxewa.

Babi na uku ya yi bayani a kan ra’i da dabarun gudanar da bincike. An kawo hanyoyi da aka bi wajen tattaro bayanai game da qwari da waxanda aka yi hira da su. Daga qarshe, an kawo sauran bayanai da aka samo game da amfani da sunaye ko halayen qwari daga wasu qabilu.

BABI NA HUXU.

QWARI A QASAR HAUSA.

4.0. Gabatarwa.

Wannan babi ya qunshi bayani a kan qasar Hausa da mutanenta da halittunta. A ciki an kawo bayanai game da Hausawa da halittun da ke kewaye da su a qasar. Haka nan an zo da bayani a kan qwari da wasu al'amura da suka shafi rayuwarsu, ire-irensu da siffofinsu da yadda suke yaxuwa ta hanyar yin Barbara da yin qwai da qyanqyasa da reno. A babin an ambaci nau'o'in qwari da irin zamantakewar da ke tsakaninsu da amfaninsu da illolinsu da hanyoyin da za a bi don kare kai daga masu cutarwa daga cikinsu.

4.1. Qasar Hausa da Mutanenta.

Qasar Hausa ta asali tana a Afirka ta Yamma ne, a farfajiyar da ke tsakanin hamadar Sahara da dazuzzukan da suka doshi gavar tekun Atlantika daga kudu. Kuma ana kiran qasar da sunan Sudan ta Yamma watau tsakanin tafkin Cadi da gwiwar Kogin Kwara a can Yamma (Alhassan, 1982:1).

A wata faxar kuma an bayyana cewa qasar Hausa tana shimfixe ne a Arewacin Nijeriya da kudancin Jamhuriyar Nijar a cikin Afirka ta Yamma. Daga Gabas ta yi iyaka da qasashen Borno, daga Yamma ta yi iyaka da qasashen Dahomey a gavar kogin Kwara. Daga Arewa ta yi iyaka da qasar Adar a cikin Jamhuriyar Nijar. Daga kudu kuma ta yi iyaka da qabilun Gwari da qabilun kudancin Zariya, da na kudancin Bauchi (Ibrahim, 1982:1).

A wannan zamani a iya cewa qasar Hausa yanki ne wanda ya mamaye wasu jihohi kamar Katsina da jihar Kano da arewacin jihar Kaduna da wasu vangarori na jihohin Bauchi da Gwambe da Neja da kuma wasu sassa na kudancin jamhuriyar Nijar. Idan aka tayar da saiti daga Arewa zuwa Kudu, qasar Hausa ta fara daga Azbin zuwa kusurwar Arewa maso Gabas da

tsaunukan Jos daga nan sai ta shararo ta yi yamma har zuwa wurin da kogin Kaduna ya yi babban doro. Daga nan kuma sai ta malalo ta yi Arewa maso Yamma ta yi mahaxa da qaton rafi na kogin Kabi daga wannan wuri sai ta karkata ta nufi Arewa maso Gabas har ta kai Azbin (Birnin Tudu, 2002:1-2).

Idan muka juya kan Hausawa, za a ga cewa su mutane ne waxanda ke zaune a qasar Hausa tun tuni, kuma suna magana da harshen Hausa a matsayin harshen uwa (Ibrahim, 1982:1).

Akwai waxanda saboda qaura da magabatansu suka yi zuwa qasar Hausa sun manta da harshensu da adabinsu da al'adunsu na asali sun xauki na Hausawa, a taqaice sun koma Hausawa a harshe da adabi da al'ada. Misalin ire-iren waxannan mutane sun haxa da Barebari da kambarin Barebari da Barebarin Katsina da Buzaye da wasu Fulani (Sallau, 2000:71).

Bunza (1990), ya bayyana cewa "Hausawa dai mutane ne da suke zaune a qasar Hausa tun farkon ta, kuma suna da zuriya a cikinta har ya zuwa yau. Kazalika suna magana da harshen Hausa, ba su da wani harshe in ba Hausa ba, suna da xabi'u da al'adu irin na Hausawa. Idan sun sava haka to barbarar yanyawa ne" (Bunza, 1990:17).

Adamu, (1997) cewa ya yi "Hausa harshe ne na Hausawa, su kuwa Hausawa wasu al'umma ne da suke zaune a qasar Hausa cikin Yankin Afirka ta Yamma. Kuma su Hausawa mutane ne baqaqe, wato baqar fata ba farar fata ba, ko da yake akan samu 'yan farare jefi-jefi musamman in aka samu auratayya da wata qabila (Adamu, 1997:16).

A bisa la'akari da bayanan da suka gabata, za a iya cewa qasar Hausa a yau tana cikin Afirka ta yamma a Arewacin Nijeriya. Wuraren da aka sani tun shekaru masu yawa da suka wuce sune qasar Hausa sun haxa da Kano da Sakkwato da Katsina da Daura da Zariya da Rano da Biram da Zamfara da Gobir da Arewacin jihar Bauchi. A qasar Nijer akwai Qwanni da Damagaram

da sauransu, inda nan ne mafi yawan Hausawan duniya suke kuma Hausa ita ce harshen da yafi kowane muhimmanci a rayuwar mutanen da ke zaune a waxannan qasashe. Haka kuma a cikin xa'irar da aka xauka qasar Hausa akwai qabilu da ba Hausawa ba waxanda ke zaune suna gudanar da rayuwarsu ta yau da kullum cikin kwanciyar hankali da lumana.

4.2. Dabbobi da Qwarin Qasar Hausa.

Irin yanayin wurin zama na Hausawa ya ba da dama ga wasu halittu na qwari da dabbobi da tsuntsaye su rayu cikinta. Yanayin zaman tare da su ya samar da alaqa da ta kawo tasiri a tsakaninsu, wato sun cuxanya da juna. A saboda haka Hausawa suka san halaye da siffofinsu. Dabba ta qunshi duk wani abu mai rai amma ban da xan'adam da tsire-tsire, sannan kuma za a iya samunta a ko'ina kamar gidaje da ruwa da daji da bisa itace. A taqaice dai dabbobi su ne halittun da xan'adam ke mu'amala da su na gida ko na daji ko na ruwa ko kuma na cikin kogo.

4.3. Ma'anar Qwari.

Akwai savani dangane da ma'anar kalmar Qwaro da abin da ta qunsa a Hausa. Akwai ma'anarta ta gargajiya wato ta asali da kuma wadda aka tsira saboda sauyin zamani. A yau kalmar na iya zama:

(a) Duk wani mutum wanda ke da qoqari da nacin karatu Bahaushe na ce masa qwaro.
(b) Bahaushe yakan kira duk wata qaramar halitta mai cutarwa qwaro, irin waxannan halittu sun haxa da maciji da kunama.

Kalmar qwaro ta xauki ma'anoni dabam-daban dangane da nahiyar

da mutum ya fito da kuma irin halittar da ya xauka ita ce qwaro, amma duk da haka masana sun kawo ma'anoni dabam-daban dangane da halittar da suka xàuka qwaro, wasu daga cikin ma'anonin sun haxa da:

(1). Bargery (1934), cikin littafinsa mai suna *A Hausa-English Dictionary and English-Hausa Vocabulary* ya kawo ma'anonin qwaro guda uku:-

(a*). Duk wani qaramin qwaro ko qananan halittu da ba su da qashin baya.*

(b).Varawo ko wani mugu kamar maye ko dabbobi kamar kada ko kura misali, ruwan nan yana da qwari ko jejin nan da qwari.

(c). Qananan duwatsu da mata ke kitso da shi, ana samunsu qasan ruwa (Bargery, 1934: 691).

(2). A Qamusun Hausa (2006) an bayyana ma'anar qwaro da:-

(a).Wata qanqanuwar halitta dangin su kiyashi ko cinnaka.

(b). Duk halittar da ke cutar xan'adam wanda don haka ake

Tsoron ta, kamar kura ko kada ko maciji.

(c). Boka.

(d). Maye.

(f). Abin da aka tufka da kaba mai launi daban-dabam don ado

A hannu ko xuwawu ga yara.

(g). Wani xan qaramin qarfe da ake maqale lifidi da shi. (Qamusun Hausa 2006:292-293).

Qarin bayanin da zan yi a nan game da waxannan ma'anoni na qwari da aka kawo a sama shi ne, an kira kura da kada da maciji da sunan qwari ne saboda halayyar da suke da ita irin ta qwari. A taqaice Bahaushe ya kira waxannan dabbobi da sunan qwaro ne saboda halayyar da suke da ita ta mugunta da qeta irin ta qwaro, amma kuma ba qwarin ba ne.

(3). Mahe (2008) na ganin su qwari:

> *Bahaushe ya fi danganta su da 'yan qananan halittu raunana waxanda ba su fi a a take su da qafa ba, ko a murje su da hannu, irin su kiyashi da tururuwa da fara da quda da buzuzu da sauransu. A cikinsu akwai manya da qanana da masu tashi sama da kuma masu dudduqe a qasa*. (Mahe, 2008:5).

(4). Hassan (1995) ya bayyana kalmar qwari da:

> *Halittu da Allah maxaukakin sarki ya yi waxanda al'adunsu da xabiunsu da halayyarsu ta sha banbam da ta sauran dabbobi kmar tsuntsaye da tsutsotsi da sauransu.* (Hassan, 1995:2).

A wurin mafarauta duk dabbar da ke cikin daji sun xauke ta qwaro. Don haka ne ma idan za su shiga daji suke neman tsari daga qwarin da ke ciki ko kuma su ce "dajin nan akwai qwari da yawa".

A taqaice bisa la'akari da bayanan da suka gabata a iya cewa kalmar qwaro ta qunshi qananan halittu waxanda ba su da qashin baya. Akwai masu tashi sama ta amfani da fukafukai da waxanda ke tafiya a qasa. Ana samun su a gidaje da daji da cikin ruwa".

A nawa ra'ayin na fahimci cewa qwari wasu qananan halittu ce waxanda ke rayuwa bisa qasa. Suna yaxuwa ta hanyar haihuwa, idan rayuwarsu ta qare su mutu. Qwari suna da yawa sosai, don sun fi kowane rukunin halitta da ke bisa qasa yawa, kuma sun fi kowane jinsi watsuwa da sauri, sannan za su iya rayuwa

ko’ina matuqar yanayin wurin ya gamsar da su. An gano masu yawa daga cikinsu sannan kuma akwai miliyoyi da ba a gano ba, kamar yadda East da Iman suka ce a littafinsu mai suna I*kon Allah:*

“*Shaihunan Malamai sun ce wai can asalin qwari daga ruwa ne, daga ciki suka fito suka zo suka mallaki tudu. Ka ga wannan bai ishe su ba, ga su nan har suka koyi dabarar tashi don su mallaki sararin sama. Sun daxe qwarai a duniya*. *Ga su da dabara da iya tsari da tsananin yawa*” (East da Imam, 1949:245)

Daga qarshe dai, kalmar qwaro ta qunshi ‘yan qanana halittu waxanda ba su da qashin baya kamar su kwarkwata da quma da kiyashi da sauro da tsanya da tururuwa da sauransu.

4.4. Muhimman Rabo da Nau’oin Qwari.

4.4.1. Qwari na Tsandauri.

Irin waxannan qwarin su ne waxanda ake samu a bisa qasa. Ana samun waxannan qwarin a saman itace ko cikin ramuka ko cikin abinci ko jikin mutane da dabbobi. Qwarin tsandauri sun kasu zuwa gida biyu, akwai waxanda ake samu a gida akwai waxanda ake samu a daji.

4.4.1.1. Qwari na Gida.

Wannan kashi ya qunshi qwari waxanda ke zaune a tare da mutane a cikin gidaje. Bahaushe ya saba dà su kuma yana zaune tare da su. Irin waxannan qwari su ne waxanda ke zaune cikin gidajen mutane, ko cikin unguwanni, ko cikin garuruwa. Ire-iren wuraren da qwari na gida ke mayarwa muhallansu a çikin gidaje ko unguwanni sun haxa da itace da kusurwar xaki ko taga da

makewayi da sauransu. Wasu daga cikinsu suna zama ne na har abada. Wasu kuma sukan xan ya da zango ne su wuce.

Yawancin qwarin da ke zaune a gidaje ba su da girma sosai, hakan ya jawo rashin damuwa da zamansu a wurare. Misalan qwari waxanda ake samu a gida sun haxa da sauro, amma shi matsala ne tun da yana yaxa cuta. Akwai quda, wanda ya fi matsi da rana. Akwai cinnaka da tsaya da gizo-gizo da kyankyaso, wanda shi ma matsala ne tun da yana kawo cuta.

Waxannan qwari suna zama a kusa da mutane ne sabóda yanayin wurin zaman ya yi masu daidai, kuma suna samun abincinsu daga abincin da mutane ke ci, da qwari ‘yan uwansu da wasu daga cikin kayayyakin cikin gida. Misali idan muka duba kyankyaso ba ya da wani wurin zama sai makewayi tun da a nan yake samun abincinsa. Sauro kuwa ya fi son wuri mai duhu da inda zai sami jinin da zai sha. Wannan shi ya sa ba a raba shi da kasancewa cikin mutane.

4.4.1.2 Qwari na Daji.

Waxannan qwari ne waxanda suka yi nisa da gidaje, wato ba kasafai ake samun su a gidaje ba, sai da wani qwaqqwaran dalili. An fi samun su a dazuzzuka saboda nan ne muhallinsu kuma a nan suke samun abincinsu. Waxansu za a same su a jikin itace, wasu a gonaki, wasu su yi rami a qasa, wàxansu kuma su gina gida su shige. Itacen da ke cikin dazuzzuka na taimaka wa rayuwar qwarin da ke wurin qwarai da gaske don suna samun abinci iri daban-dabam daga gare su kamar itace da ganye da filawa da iri. Kuma suna samar masu da mazauni. Irin waxannan qwarin ba kowa ya saba da su ba sai wanda ke mu’amala da su, misali kamar mutane masu wasa da kunama, ko masu kiwata qudan zuma suna iya kamo su don su killace su wuri guda su rinqa kula da su. Amma idan mutum ya ci karo da su a muhallinsa, nan da nan zai xàuki matakin kawar da su. Daga cikin qwarin da ake samu a daji akwai qudan tsando da kunama da fara da gamaxixi da zirnaqo.

4.5. Qwari na Ruwa.

Wannan gida ya qunshi qwari waxanda ke rayuwa a ruwa, kamar koguna, ko tafukka ko kududdufai ko rijiyoyi ko gavar ruwa ko duk wani wuri inda ruwa ke taruwa, ko kuma duk inda ke da damshi. Irin waxannan qwari suna yin qwayayensu a ciki ruwa ko gavar ruwa.Wasu daga cikin su suna rayuwa ne rabi a ruwa, rabi a tudu domin ko sukan shiga ruwan ne don neman abinci ko don su yi qwai kamar. Misalan qwari na ruwa sun haxa da qaguwa da matsattsaku da sauransu.

4.6. Nau’o’in Qwari.

4.6.1. Qwari Masu Yaxa Cuta.

Wannan nau’i ya qunshi qwari waxanda ke yaxa cuta tsakanin mutane da dabbobi. Irin waxannan qwari suna zaune ne a gidaje da dazuzzuka. Daga cikinsu akwai masu shan jini don shi ne abincinsu. Akwai kuma waxanda ba sa shan jini amma suna watsa cuta. Misalan qwari masu watsa cuta su ne sauro da qudan gida da qudan tsando da kaska da kyankyaso da gizo-gizo da sauransu.

4.6.2. Qwari Masu Zama a Jikin Xan’adam.

Wannan nau’i ya qunshi qwari masu zama jikin mutum ko dabba ko tsuntsu. Yawanci irin waxannan qwarin jini ne abincinsu saboda haka ba a raba su da jiki. Daga cikinsu akwai tunkuyau da jiga da kaska da kuxin cizo da qwarqwata da sauransu.

4.6.3. Qwari Masu Zama a Jikin Dabbobi.

Yawanci irin qwarin da ke zama a jikin xan'adam suna zama a jikin dabba don dukansu jini ne abincinsu. Misali kaska na zama a jikin dabbobi ita ke sakar musu da ciwon kirci. Sai kwarkwata da jiga da tunkuyau da quma.

4.6.4. Qwari Masu Haxa Gari.

Wannan gida ya qunshi qwarin da ke zama tare, suna gama qarfi su taimaki juna don sun gane sai an gama kai ake samun ci gaba da sauqin rayuwa. Daga cikin qwarin da ke irin wannan zama akwai qudan zuma, a tawagar qudan zuma akwai uwa wadda ake kira sarauniya, akwai maza da ma'aikata. Aikin sarauniya shi ne yin qwai. Mazan ko ba su da wani aiki a wanna zama na tarayya. Su ko ma'aikata duk aikin da aka tunkara su ke yin shi (Vines and Rees, 1971:617).

Gara kamar qudan zuma na zama cikin tawaga, a garinsu akwai maza da ma'aikata waxanda suka haxa maza da mata, sannan akwai mayaqa da dogarai da waxanda ke aikin ungozoma. A cikin gidansu akwai wurin renon 'ya'ya da xakunan barci da taskoki na ajiye abinci (Imam, 1944: 40).

Sauran qwari waxanda ke zama tattare kuma suna da jama'a iri-iri sun haxa da tururuwa da cinnaka da qwarqwasa da shazumami da kiyashi da sauransu. Wani abin ban sha'awa game da zaman tare da son juna na waxannan qwari shi ne idan macen zirnaqo na jin yunwa sai ta shafi wadda ta qoshi ita ko sai ta amayo mata vangaren abin da ta ci don ita ma ta samu (East da Imam, 1944:291).

4.6.5. Qwari Masu Vata Amfanin Gona.

Wannan fasali ya qunshi qwari da ke vata shuke-shuke, su cinye amfanin gona. Daga cikinsu akwai gwazarma wadda ke vata saiwar hatsi, sai gamaxixi wanxa ya fi fitowa da damana kuma yana vata auduga da kuvewa da rama da

dawa. Malam-buxe-littafi lokacin da yake tsutsa mavarnaci ne qwarai don idan ya sami ganye sai ya ga bayansa (East da Imam, 1949:275).

4.6.6. Qwari Masu Dafi.

A qamusun Hausa (2006) an bayyana ma'anar dafi da wani ruwa-ruwa da kan fito daga haqoran maciji yayin da ya sari mutun ya jigata shi ko ma ya kashe shi, ko kuma daga qarin kunama idan ta harbi mutum" (Qamusun Hausa, 2006:85).

Wannan gida ya qunshi nau'o'in qwari da ke xauke da dafi wanda suke amfani da shi don kare kansu daga abokan gaba. Qwaranyar da tayi qaurin suna dangane da amfani da dafi ita ce kunama.

4.6.7. Qwari Masu Cin 'Yan'uwansu.

Wannan gida ya qunshi qwari waxanda ke cinye waxansu qwari. Misali daga cikinsu akwai qoqi-qoqi wanda idan ya xaga hannayensa sama duk qwaron da ya gitta wurin ya zama nama. Gizo-gizo ma na cikin wannan gida. Akwai ire-irensu masu yawa a duniya manya da qanana kuma dukkansu suna cin qwari. Idan gizo-gizo zai kama qwaro sai ya lallava ya hau masa, kuma sai ya fitar da wani zare-zare ya yi wa kansa talala ta yadda ko qwaron ya tashi ba zai tafi da shi ba. Wasunsu kuma sai su saqa yana yadda duk qwaron da ya gitta sai dai wani ba shi ba.Wasu qwarin da ke qarqashin wannan gida sun haxa da zanzaro da zirnaqo.

4.7. Siffofin Jikin Qwari.

Qwari halittu ne da ke rayuwa a doron qasa, suna cin abinci, su sha abin sha kuma suna da halaye irin nasu. Suna yin qwai su qyanqyashe su sami 'ya'ya. Haka kuma, wasu daga cikinsu kan reni 'ya'yansu har su girma. Sannan sukan yi rashin lafiya su mutu.

Siffar jikin qwari ta bambanta da ta sauran dabbobi, domin kuwa akwai waxanda jikinsu ya kasu zuwa kashi uku. Akwai kai, sai qaramin ciki wanda ke matsayin qirji, sai gangar jiki. Kamar quda da gungura kashi da zuma. Haka nan akwai waxanda ke da jiki mai xauke da kai da gangar jiki babu wutsiya kamar su kunama da gizo-gizo. A jikin kai akwai idanuwa manya guda biyu, amma kuma ba su amfanar da wasu daga cikinsu sosai wajen gani domin sun fi gane abubuwa ta jin motsi. Kowane qwaro yana da baki wanda ya yi daidai da irin abincin da yake ci.

Qwari irin su fara masu cin ganye da tsiro. Suna da muqamuqi mai qarfi da kaifi wanda suke iya juyawa gefe da gefe saboda tauna abinci. Bakin ta macen sauro na xauke da wata allura wadda ke taimaka mata wajen huda fata ta tsotsi jinni. Bakin malam-buxe-littafi na xauke da famfo dogo wanda ke ba shi damar tsotso zuma daga fure. Gara tana da baki mai tauri wanda ke taimaka mata wajen xibar abubuwa masu qarfi. Shi ko qudan gida bakinsa na xauke da wani soso-soso wanda ke xiga yawu cikin abincinsa, yawun na xàuke da sinadarin da ke sa abinci ya narke ta yadda kawai sai ya tsotse shi.

Wasu qwari na da gashi dogaye guda biyu a bisa kai daga gaba waxanda ake kira dohulu wato antennae da Turanci. Waxannan su ke taimaka wa qwarin wajen ji kamar matsayin kunne, kuma suna amfani da su don tava abu su ji irin sa kamar matsayin hannaye. Haka kuma da shi suke jin qanshin abinci. Qwari dangin tururuwa da qudan zuma na amfani da dogayen gashin (dohulu) wajen gane abokin aurensu da bambance sheqarsu don neman kariya daga duk wani qwaron da zai kutso wurin. Sannan kuma yana amfani gare su wajen samun bayanai game da abincinsu da duk wani abu mai haxari gare su. Ga sauro kuwa, dogayen gashin na amfani gare shi wajen jin qara da qamshi.

Galibi, qwari na da qafafu guda huxu ko shida, amma wasu na da guda takwas. Wasu qwarin duk qafafunsu iri xaya ne, amma wasu siffar kowace ta

bambanta da ‘yar uwarta. Misali qafafuwan qoqi-qoqi na gaba an yi su daidai yadda za ta iya kama da matse abincinta. Qafafuwan fara da quma na da girma da qarfi saboda taimaka masu yin tsalle sosai cikin iska. Shi ko gyare an yi qafarsa ta gaba daidai yadda za ta iya tona qasa. Qirji ke liqe da kai inda qafafuwa da fukafukai ke liqe.

Daga qirji sai ciki inda ke da alhakin narkar da abincin da aka ci da haihuwa. A cikin cikin matan qwari akwai mahaifa wurin da ake adana qwai. Cikin wasu qananan qwari a rarrabe yake gava-gava kamar zobe, inda za a iya samun gavovi daga goma zuwa sha xaya waxanda ke haxe da wata mahaxa mai taushi.Mahaxar ke ba su dama su juya shi yadda suke so. Don haka ne suke iya miqar da xuwawunsu ya yi tsawo idan za su yi qwai, ko kuma su mayar da shi gajere don kare kai. Gavar qarshe da ke jikin gangar jikin wasu qwari na da wani zumvutu wanda ke taimaka masu wajen sansanar abin da ke kusa da su. Wasu kuma yana taimaka masu wajen kariya, amma ga wasu qwarin gavar su ta qarshe it ace wutsiya (Vines and Rees, 1971: 109-120).

4.8. Muhimman Halayen Qwari.

4.8.1. Yaxuwar Qwari.

Qwari suna da saurin yaxuwa qwarai. Bincike ya nuna da a ce babu abin da ke kashe su, da tuni sun gaje duniya. Qwari sun daxe qwarai a duniya. Ga su da dabara, ga tsananin yawa domin an gano cewa kashi saba’in da biyar cikin xari na dabbobin da ke duniya qwari ne. Kuma suna yaxuwa ta hanyar yin qwai su qyanqyashe ko kuma ta hanyar haihuwa. Idan qwai ya gama girma sai ya qyanqyashe a cikin ciki, wasu kuma suna haihuwar ‘ya’ya a zahiri masu kama da su (Encarter Software, 2007).

4.8.2. Barbara.

Barbara na nufin saduwa tsakanin namiji da macen qwaro ko dabba. Dole ne kafin a haihu sai an sami barbara. Qwari na yin qoqari su jawo hankalin junansu ta hanyoyi daban-dabam kafin barbara. Daga cikin hanyoyin akwai fitar da sauti da waqa ko fitar da qamshi da shafar juna ko kuma fitar da haske ga waxanda Allah S.W.T ya ba ikon yin hakan, ko sake launin fata. Misali qwari irin su gyare da fara na amfani da waqa ko sauti. Abin lura a nan shi ne kowane qwaro na da irin hanyar da yake amfani da ita don jawo hankalin juna. Sannan kuma yawanci namiji ke qoqarin jawo hankalin mace, amma kuma ana samun waxanda matan ne ke jawo hankalin mazan.

Kamar yadda yake faruwa ga sauran dabbobi da mutane, maniyyin namijin qwaro na haxuwa da qwan qwaranya a cikin mahaifarta bayan an yi barbara. Lokacin barbara za a ga qwarin su bibiyu harhaxe. Mazan qwarin na amfani da qafafuwansu su rungume matan. Misali qudan gida na yin barbara a qasa lokacin da suke hutawa, kuma sukan xauki ‘yan mintoci kaxàn. Sauro ko suna yi ne lokacin da suke yawo a iska. Macen sauro na shan jini kafin saduwa kuma barbara sau xaya tak take buqata a rayuwarta. Qudan zuma na yin barbara lokacin da suke yawo a sama cikin iska. Idan lokacin saduwar ya zo sarauniya za ta tashi ta yi sama sai mazan qudan zuma su bi ta. Duk wanda ya ci sa’a ya cim mata a qololuwar sama, shi zai sadu da ita. Sarauniyar qudan zuma kamar matar sauro barbara sau xaya tak ta ishe ta a rayuwarta. Shi ko namijin qudan zuma mutuwa yake yi da zarar ya gama saduwa da macen qudan zuma. A sai da rai a samo suna ke nan. Qwari irin su tururuwa kan yi barbara a bisa qasa kuma bayan barbara sai namijin ya mutu. macen kuma ta rasa fukafukanta. Ga jinsin qwari waxanda matansu suka fi mazan girma, mazan na samun kan su cikin haxari lokacin barbara domin matan na iya cinye su. Shi ya sa wasu mazan ke kare kansu daga wannan tsautsayin ta hanyar kawo kyautar xan qaramin qwaro wanda qwaranya za ta ci lokacin da suke barbara. Duk namijin qoqi-qoqi da ya

tinkari matarsa ba tare da irin wannan kyautar ba, idan ya rungume matar sukan daxe tare. Wani lokaci tun da safe har tsakar dare amma kuma tun suna rungume matar za ta fara cin mijin gava-gava, ba ta barin kome sai fukafukai (Kotpal, 2005:604 da 611 da 622 da 651).

4.8.3. Haihuwar Qwari.

Haihuwa na nufin samun xa ko ‘ya. A taqaice dai haihuwa na nufin samun qaruwa ta (mutum ko dabba). Qwari suna qaruwa su yi yawa ta hanyar haihuwa amma savanin sauran dabbobi, kaxan daga cikinsu ke haihuwar xa a zahiri. Yawancin su rayuwa na farawa ne daga qwai. Bayan barbara tsakanin namijin qwaro da qwaranya sai ta yi qwai, kuma yawancin su ba su kwanci kamar yadda tsuntsaye ke yi. Bayan xan lokaci, qwayayen na qyanqyashe kansu. Matar tsando a cikin cikinta take yin qwai kuma ya qyanqyashe. Idan tsutsar ta xan yi girma sai ta haife ta.

Wasu qwarin sukan haihu da yawa a rayuwarsu, misali macen tsando na iya haihuwa har sau takwas zuwa goma a cikin watanni uku. Ke nan tana iya haihuwa bayan kowane kwana goma (Kotpal, 2005: 205).

4.8.4. Qwai.

A qamusun Hausa an bayyana qwai da wata mulmulalliyar halitta da tsuntsaye ke fitowa da ita daga mahaifarsu, wadda kuma bayan wani xan lokaci sai su qyankyashe ta don xan tsako ya fito daga ciki (Qamusun Hausa, 2006: 289).

Mafi yawa daga qwari na haihuwa ta hanyar yin qwai. Matan qwari na yin qwai bayan Barbara. Kowace qwaranya na nasa qwanta a wurin da take ganin zai sami kariya daga haxari ya kuma ya sami reno har ya kyankyashe. Halayya ta kula wajen yin qwai ya bambamta tsakanin qwari daban-dabam. Wasu sukan yi qwan a duk wurin da suka ga dama babu kula, amma mafi yawa

daga cikin su sukan tabbatar da sun adana qwayayensu a wurin da suka san za su sami abinci idan suka qyanqyashe. Misali wasu kan yi qwan a jikin shuka. Wasu kuma a jikin matattun dabbobi. Wasu kamar qazunzumi na manna qwan a bayan mazajensu bayan barbara. Kyankyaso na adana qwansa cikin wani ma'ajiyi mai soso-soso. Fara kuwa tana kare qwanta ta hanyar zuba masu wani sinadari mai kumfa. Macen gizo-gizo na naxe qwayayenta cikin siliki kuma ta yi ta kula da su har sai sun qyanqyashe. Qwarkwata kuwa na liqa qwanta a jikin zirin gashi a bisa kai ta yadda da wuya a iya zare shi.

Wasu qwari na yin qwayaye kaxan a rayuwarsu. Wasu kuwa na nasa miliyoyi, misali matar gamaxixi na iya yin qwai guda xari a lokaci guda. Macen qoqi-qoqi ko na iya yin qwai har xari uku a cikin sheqa xaya, sai ta xaure su ga itace ko ciyawa. Haka kuma gara na iya yin qwai sittin cikin minti xaya. Macen sauro na yin qwai daga xari biyu zuwa xari huxu a lokaci xaya. Sarauniyar qudan zuma ko, na yin qwayaye har miliyan xaya a rayuwarta. A rana xaya tana iya nasa qwayaye dubu xaya da biyar. Macen quda na iya yin qwai daga xari xaya har xari biyu. Wata kan yi qwai xari tara kafin ta bar duniya. Macen kyankyaso da yake qwayayenta cikin xan kwanko take yin su, tana iya nasa guda hamsin kuma kowanne na xauke da qwayaye guda sha biyu zuwa sha huxu. Macen kuxin cizo kuwa na iya nasa qwai guda xari da hamsin a rayuwarta. A rana tana yin guda biyu zuwa uku. Fara na iya nasa qwayaye daga guda sha biyar zuwa xari (Encarter Software, 2007).

4.8.5. Qyanqyasa.

Qyanqyasa na nufin kwanci na wani adadin lokaci da tsuntsaye ke yi don qwai ya fafe 'ya'ya su fito. Qwari ba sa yin qyanqyasa, sai dai kowanne ya san wurin da zai yi qwansa da yadda zai rufe su don su sami reno har su qyanqyashe. Misali idan macen sauro za ta yi qwai ta san ta nemi inda ke da ruwan da ba ya gudu, ko cikin 'yan gurabun da ruwa ke taruwa, ko a cikin

fadamu, da sauran ire-iren waxannan wuraren, domin ta san idan ba nan ba, to qwayayen ba za su qyanqyashe ba. Haka idan macen malam-buxe-littafi za ta yi qwai sai ta sami qarqashin ganye, don kar zafin rana da ruwan sama su halaka su. Idan qudan gida zai yi qwai, sai ya nemi juji. Qudan masai kuwa yana yin nasa qwan a jikin mushe ko bisa xanyen nama, ko a kan najasa. Kowane kwai adadin kwanaki da yake xauka kafin ya qyanqyashe. Wasu na xaukar kwanaki kaxan wasu kuma na xaukar kwanaki da yawa. Wannan ko ya danganta ga jinsin da qwaron ya fito. Misali qwan qudan gida na xaukar kwana xaya. Na sauro kan xauki kwana xaya ko biyu. Qwan gamaxixi na xaukar kimanin kwana biyar. Na qoqi-qoqi ko na xaukar mako uku, qwan matar gungura kashi na xaukar kwana bakwai ko goma kafin qyanqyasa (East da Imam, 1949:254 da 262 da 273 da 280 da 283).

4.8.6. Rikixa.

Rikixa na nufin abu ya canza daga yadda yake tun asali ya sake kamanni. Yawanci idan qwari suka yi qyanqyasa, xan da ke fitowa daga qwan ba ya yin kama da iyayensa kamar yadda na tsuntsaye da sauran dabbobi ke kasancewa. Amma duk da haka akwai jinsin qwarin da ‘ya’yansu ke fitowa da irin siffarsu kamar fara. Yawancin qwari waxanda ke rikixa bayan sun kyankyashe ba su da fukafuki da sauran siffofin jiki irin na manyansu. Wasu ma ko qafafuwa babu. Misalan qwarin da ke bin mataki-mataki na rikixa sun haxa da malam-buxe-littafi, da mageduwa, da zuma, da quda, da sauransu. Irin waxannan qwarin idan aka haifo su sai ka gan su kamar tsutsa, don ga baki xaya ba su kama da iyayensu. Sannan kuma kowanne da irin abincin da yake ci da yanayin da yake buqata don ya rayu. Idan tsutsar ta gama girma sai ta shiga mataki na gaba inda take sakewa cikin kwasfa wadda za ta kare ta, ta yi ta barci. Da zarar kwanakin wannan mataki sun cika sai kwasfar ta buxe. Maimakon a ga tsutsa sai qwaro mai kama da iyayensa ya fito ya ja jini cikin fukafukansa ya shiga uwa duniya. Misali idan qwan malam-buxe-littafi ya qyanqyashe, xan yakan fito wata irin

tsutsa. Idan ta girma sai ta sake kama ta dunqule kamar ta mutu ta naxe kanta cikin wani vargo na audugar siliki ta yi ta barcinta. A cikin wannan barci za ta yi ta rikixa. Da zarar ta gama rikixe-rikixenta sai ka ga malam-buxe-littafi ya fito. Haka idan qwan gungura kashi ya qyanqyashe da farko sai tsutsar ta fito fara, sai ta koma rawaya-rawaya, bayan wata xaya sai ta sake fata ta koma ja da fara daga qarshe sai ta koma qwaro baqi qirin kamar uwarta.

Daga cikin qwari akwai waxanda bayan haihuwa suna yin xan yanayi da iyayensu, yawanci ma ba a cika gane bambancin da ke tsakanin kamannin su da na iyayensu ba. Misali idan ta macen gizo-gizo ta yi qwai sai ta nannaxe su cikin wani zare-zare na siliki ta voye su cikin tsagar vawon itace. Da ‘ya’yan sun qyanqyashe sai su fito kamar iyayensu sai dai ‘yan qanana, su ba su rikixa sai dai su yi ta girma suna sake fata har kusan sau shida. Daga qarshe sai su zama kamar iyayensu. Haka nan idan sarauniyar gara ta yi qwai, da sun qyanqyashe sai su fito ‘yan qananan gara domin su ma ba su bin mataki-mataki kamar yadda mafi yawancin qwari ke bi.

Da zarar qwaro ya zama babba to ba ya qara girma. Sannan kuma duk qarfin da yake da shi sai ya koma ga haihuwa. Yawancin qananan qwari waxanda ke da fata mai tauri idan za su qara girma sai su save fatarsu wadda ta yi kaxan sannan su fito da wata mai girma a madadinta. Saboda haka qwari irin su qaguwa da kunama da gizo-gizo dole ne su yi ta yin sava a kai-a kai a rayuwarsu har sai sun gama girma. Don ta yin hakan ne kaxai suke qara girma. Wani abin al’ajabi game da qwarin da ke bin mataki-mataki na rikixa shi ne yawancin kwanaki daga kwanakin da za su yi a raye na tafiya ne lokacin da suke rikixa. Idan suka gama bin matakan suka fito duniya sai ka tarar kwanakin da suka rage masu a rayuwa ‘yan kaxan ne (East da Imam, 1949:240-241).

4.8.7. Reno.

A Qamusun Hausa an bayyana reno da kula musamman ta yaro ko dabba. Mafi yawancin qwari ba su renon ‘ya’yansu sai dai kafin su yi qwai suna gyara musu wuri, kuma bayan sun yi qwan sai su rufe, su tafi abinsu. Misali daga cikin qwari masu irin wannan hali akwai qoqi-qoqi. Haka kuma akwai nau’o’in qwarin da ke tanadar wa ‘ya’yansu abincin da za su ci bayan sun qyanqyashe. Amma daga ajiye abincin ba su sake kulawa da su, ke nan ba ruwansu da renonsu. Misali kafin macen malam-buxe-littafi ta yi qwai, sai ta nemi karmami ko ganye wanda ‘ya’yan za su ci bayan sun qyanqyashe. Haka nan kafin matar gungura kashi ta yi qwai sai ta haqa rami ta tara abinci a ciki sannan ta yi qwai a bisa ta yi tafiyar ta. Da zarar qwan ya qyanqyashe, tsutsa ta fito, sai ta kama cin abincin.

Akwai qwarin da ke renon ‘ya’yansu tun daga qyanqyasa har sai sun isa neman abinci da kansu. Daga cikin irin waxannan qwari akwai zirnaqo. Da zarar ta macen zirnaqo ta yi qyanqyasa sai ta nemo tsutsa ta harbe ta da qarinta kuma ta tattauna ta sannan ta riqa ba ‘ya’yan suna ci.

Qudan zuma na daga cikin irin qwarin da ke renon’ya’yansu. Idan tsutsar qudan zuma ta fito daga qwai sai ta yi kwanciyarta bisa sheqa. Ma’aikata su rinqa ba ta abinci a baki ta yi ta qara girma har zuwa kwana biyar. Daga nan sai ta shiga kwasfa ta kwanta har zuwa kwana bakwai ko takwas. Daga nan sai a ga sabon ma’aikaci ya fito. Kunama na kula da qwayayensu sannan kuma bayan sun qyanqyashe suna goya su a bayansu don kare su daga abokan gaba. Haka nan wasu daga jinsin qadangaru na kulawa da ‘ya’yansu.

4.8.8. Ire-iren Abincin Qwari.

Abinci shi ne duk abin da ake ci don maganin yunwa kuma shi ke xàuke da sinadaran da ke taimaka wa jiki don ya tafi daidai. Bakin kowane qwaro, ya yi daidai da irin abincin da yake ci don ya rayu. Sauro bakinsa na da wata ‘yar

allura wadda yake huda fata ya tsotsi jini daga jikin xan’adam ko dabba. Dangin malam-buxe-littafi na da wani irin abu kamar famfo dogo wanda suke sawa cikin furen tsiro su tsotso zuma. Dangin su gara kuwa, suna da baki mai tauri wanda ke ba su damar xibar abubuwa masu tauri kamar itace.

Bahaushe na cewa “kowane allazi da nasa amanu”. To haka yake ga ire-iren qwari, domin ko kowane daga cikinsu ya san irin abincin da zai rinqa ci. Sannan kuma kowane ya san irin abincin da zai ba ‘ya’yansa don su rayu. Yawancin qwari suna xiga wa abincin su miyau don ya zama ruwa kafin su tsotsa, saboda ba za su iya cin mai tauri ba. Quda ya san qazanta ita ce abincin ‘ya’yansa, saboda haka idan zai yi qwai dole ne sai cikin qazanta idan dai yana so su rayu. Ga misalan wasu Qwari da nau’o’in abincinsu:

- Daga cikin qwari akwai masu shan jini kamar macen sauro da jiga da kwarkwata.
- Akwai masu cin najasa kamar quda da gungura kashi.
- Akwai masu cin ganyaye da huranni kamar su fara da gyare.
- Akwai masu cin itace da katako kamar gunxa da ja-na-kuka da gara.
- Akwai masu cin kifi da qananan qwarin da ke cikin ruwa kamar qaguwa.
- Akwai masu cin qananan qwari ‘yan uwansu kamar qoqi-qoqi da gara.
- Akwai masu shan zakin fure kamar qudan zuma da namijin sauro. Akwai qwarin da ke cin hatsi irin su gero da dawa da masara da wake da sauran nau’o’in abinci misali tsatso, da kwalkwasa da zago.
- Wasu suna cin tsutsotsi da qwari a matsayin abinci. Daga cikinsu akwai kunama da gizo-gizo.

- Qwari irin su kyankyaso har sabulu ba su bari ba. A taqaice dai, waxannan su ne wasu daga cikin abubuwan da qwari ke ci a matsayin abinci (Hassan,1995: 12 da 17 da 18).

4.8.9. Kariya.

Kariya na nufin yin amfani da wasu hanyoyi ko makamai don kange kai daga abu mai cutarwa. Akwai hanyoyi masu dama da qananan qwari ke bi don su kare kansu daga wasu manyan qwari ko dabbobi, misali idan za su yi qwai sai sun nemi wurin da sun san za su kuvuta daga halaka. Suna kuwa yin hakan ne don neman kariya ga ‘ya’yan kafin qyanqyasa.

- Da yawa daga cikin qwari kan yi sauri su vuya, ko da yake wasu kan yi qoqarin kare kansu ta hanyar harbi da cizo.
- Yawanci idan qananan qwari, suka ga abokan gaba maimakon su gudu sai su lafe jikin qasa kamar sun mutu da zarar haxarin ya wuce sai su yi tafiyarsu.
- Wasu qwari na kare kansu ta hanyar sake kamanni don kada a gane su.
- Qwarin da suka gama girma yawanci suna kama da abubuwa daban-dabam kamar ganye da kashin tsuntsaye. Saboda haka da maqiya sun tinkaro su sai kawai su lafe jikin abubuwan da suke ganin za su kare su.
- Tsutsar malam-buxe-Littafi da faxa wuta na amfani da dabarar sake kamanni don neman tsira saboda ba su iya gudu daga abokan gaba.
- Wasu qwari na da wasu sinadarai a cikin jikinsu wanda ke ba su damar fitar da launi mai haske wanda ke faxakar da maqiyansu xanxanonsu bai da daxi ko kuma suna da guba. Irin qwarin da

ke da irin wannan baiwa ba su vuya don abokan gaba, koyaushe suna ci gaba da kiwo ba tare da tsoro ba.

- Gizo-gizo na da wata dabara ta kariya, da sun ji abokan gaba sai su kwanta shiru su dunqule kamar sun mutu, idan ko rana ta vaci har wani abokin gaba ya kama masu qafa sai su tsinke ta su bar masa guntun su tsere, daga baya sai su tsiro da wata.
- Qadangaru na amfani da irin wannan dabarar, idan abokin gaba ya kama wutsiyarsu sai ta tsinke shi ko ya tsere, daga baya sai ya sake wata.
- Akwai qwarin da ke yin sava, wato vawon jikinsu ya tsage ya fita, sai daga baya sabuwar fata ta fito, misali gizo-gizo da qaguwa da kunama. Sabuwar fatar da ke fitowa da farko taushi gare ta sai sannu a hankali take yin qarfi. Saboda haka idan suka fita daga tsohuwar kwasfar sai su je su vuya cikin wani lungu har sai sun sami wata sabuwar sutura domin a wannan lokacin ba su da garkuwa saboda haka dole ne su nemi kariya.
- Gara na da jiki mai taushi kuma babu abin da ya kare shi, kuma manyan qwari masu yawa na cinye su da sun gan su. Wato dai suna da abokan gaba ko'ina, saboda haka ne suke yin babban gini don ya zama kariya gare su daga macuta. Ganuwar da suke ginawa tana da qarfi qwarai.Sannan kuma a kowace qofa ta birni sai sun aje mayaqa.
- Akwai qwarin da ke cizo da harbi don su kare kansu.
- Akwai salihan qwarin da ke qoqarin su zama kamar masu cuta don su kare kansu.
- Wasu nau'o'in gizo-gizo na yin qoqari su yi kama da irinsu masu cizo.

- Akwai wasu nau’o’in malam-buxè-littafi waxanda ke da guba kuma xanxanonsu bai da xaxi. Daga cikinsu waxanda Allah bai ba wannan baiwar ba sai su yi qoqarin yin kama da masu guba don neman kariya. Waxannan su ne wasu daga cikin hanyoyin da qwari ke bi domin su kare kansu daga abokan gaba.

4.8.10. Zamantakewar Qwari.

Zamantakewa na nufin zama tare da wasu, kuma tana iya zama hulxa ta cuxe-ni-in-cuxe-ka. Qwari ma ba a bar su a baya ba wajen tsarin zamantakewa mai kyau ko mara kyau. Ko da yake kaxan daga cikinsu ne ke son junansu. Da yawa daga cikinsu da zarar uwa ta yi qwai ta rufe sai ta yi tafiyarta, sun rabu ke nan har abada. Idan ma ta gamu da xanta a hanya tana iya cinye shi. Amma duk da haka masu iya magana na cewa “ba duka aka taru aka zama xaya ba” domin ko daga cikin qwari akwai waxanda ke da hulxa ta zamantakewa mai kyau tsakaninsu da ‘yan uwansu. Irin waxannan qwari suna zama tare, wuri xaya don su gama qarfi su taimaki juna.

Kamar yadda Vines &Rees (1971) suka ayyana, daga cikin qwarin da ke irin wannan zama akwai qudan zuma. A garin qudan zuma akwai uwa wadda ake kira sarauniya, sai maza da ma’aikata. Aikin sarauniya shi ne yin qwai. Mazan ko ba su da wani aiki a garin. Su ko ma’aikatan duk aikin da ke gidan suke yin sa (Vines and Rees, 1971: 617).

Mawallafa Littafin *Qaramin Sani* sun bayyana cewa ita gara kamar qudan zuma suna zaune ne tattare. A cikin birninsu akwai maza, sai ma’aikata waxanda suka haxa maza da mata. Sannan akwai mayaqa da dogarai da waxanda ke aikin ungozoma. A cikin gidansu akwai inda suke renon ‘ya’yansu da xakunan barci da taskoki na ajiye abinci (Imam, 1944: 40-41).

Sauran qwari waxanda suke zama tare cikin qungiya sun haxa da tururuwa da cinnaka da qwarqwasa da shazumami da kiyashi da gwano da

sauransu. Wani qarin haske game da zaman tare da son juna na irin waxannan qwari shi ne idan zirnaqo na jin yunwa sai ta matsa ta shafi xayar wadda ta qoshi, ita kuma sai ta amayo mata vangaren abincin da ta ci don ita ma ta samu (East da Imam, 1949: 302).

4.11. Amfanin Qwari.

Zaman tare shi ke kawo cuxanya da juna domin kowane abu mai rai yana buqatar taimakon wani don ya rayu bisa doron qasa. Mafi yawa daga cikin qwari suna da amfani qwarai da gaske domin suna samar da abubuwa masu taimakawa ko kuma su rage waxansu da ke da illa ga rayuwa. Daga cikin amfanin da xan'adam ke samu daga qwari akwai:

- Samar da abinci — xan'adam na samun zuma daga qudan zuma. Sannan yana cin fara da shinge da qaguwa. Don haka ne ma masana kiwon lafiya suka bayyana cewa waxannan nau'o'in abincin na xauke da sinadarai masu gina jiki.
- Wasu qwarin na kawo barbarar furanni, wato su haxà namiji da macen tsiro su yi aure kuma sakamakon haka ne 'yan'adam ke samun 'ya'yan itace iri-iri sai wanda mutum ya zava. Wasu masu zaqi, wasu masu tsami, wasu masu bauri, wasu masu xaci da sauransu.
- Wasu suna cinye miyagu 'yan uwansu. Ke nan suna taimakawa wajen rage yawansu a gidaje da gonaki da lambuna da sauran wuraren da suke rayuwa.
- Wasu qwarin na taimakawa wajen jujjuya qasa a lambuna da gonaki. Yin hakan na sa iska ta shiga ko'ina. Haka kuma suna sa matattun dabbobi su ruve da wuri su koma taki wanda hakan na gyara qasar noma sosai kuma ya haifar da samun kyakkyawar yabanya.
- Qwari na sa xan'adam ya yi tsafta. In dai mutum na son zaman lafiya, to dole ya rinqa tsaftace jikinsa da tufafinsa da abincinsa da muhallinsa kai

da dai sauran wurare da abubuwan da ke tattare da shi. Idan ko ba haka ba, su za su zama aminansa.

- Ana sayar da fara don a samu kuxi. Hakan ya taimaka wajen samun kuxin biyan buqata.
- Ana kiwata da amfani da wasu qwari don samun kuxi kamar qudan zuma.
- Ana amfani da fara a jikin fatsa don a kama kifi.
- Qwari na zama matsayin abinci ga wasu qwari ‘yan’uwansu da tsuntsaye, da sauran halittu masu yawa.
- Qwari na cin tsutsotsin da ke yin varna ga shuke-shuke a gonaki.
- Ana amfani da qwari a matsayin magani. Misali idan mutum ya kamu da ciwon shawara ana haxa masa magani da gwazarma. Haka kuma ana haxa magani da gyare don a sami murya mai qarfi da zaqi. Haka nan ana amfani da zuma a haxa magunguna iri daban-dabam. Ana amfani da tsanya a haxa maganin mayu, sannan kuma tana maganin quraje.

4.12. Illolin Qwari.

Yawancin halitta idan aka bincike ta kuma aka gane tana da amfani, to kuma lalle ne a samu rashin amfaninta. Bincike ya nuna masu yawa daga cikin qwari abokan gabarmu ne, daga cikin su akwai masu cizo da harbi. Ko da yake masana sun nuna cewa suna yin hakan ne a matsayin kariya, ke nan idan mutum bai matsa masu ba, su ma ba za su tava shi ba.

- Babbar illar da qwari ke yi wa xan’adam ita ce kawo da baza cuce-cuce ga mutane da dabbobi. Misali sauro na kawo cutar zazzavi da cutar shawara. Sannan kuma akwai wanda ke kawo cutar tundumi. Qudan tsando na kawo ciwon barci. Qudan gida na yaxa cutar atini da gudawa. Tunkuyau na haddasa ciwon vera da sauran masu yawa waxanda ban ambata ba. (East da Imam, 1949:302).

- Akwai qwarin da ke vata amfanin gona. Daga cikinsu akwai gwazarma wadda ke vata saiwar hatsi. Akwai gamaxixi wanda ya fi fitowa da damina kuma varnarsa ta fi yawa ga auduga da kuvewa da rama da dawa da sauransu. Fara xabi'atu da vata amfanin gona. Akwai wani qwaro da ake ce wa qanjamon yalo wanda varnar shi ta fi ga yalo. (Malam Ado 24-04-2013).
- Wasu qwarin suna vata kayan xaki ta hanyar lalata katakon da aka yi kayan da su, daga cikin irin waxannan qwarin akwai gunxa da gara.
- Akwai qwarin da ke lalata saiwar shuke-shuke. Ga waxanda ke lalata tufafi da litattafai, sannan akwai waxanda ke kashe dabbobi ta hanyar sa masu cuta.

4.13. Kariya Daga Qwari.

Hanyoyin da za a bi don a magance miyagun qwari sun haxa da tsafta, da amfani da magani don a kashe su. Wata hanyar da za a bi don rage miyagun qwari ita ce xaukar duk wani mataki don hana su yaxuwa.

4.14. Naxewa.

A babi na huxu an kawo taqaitaccen bayani kan qasar Hausa da mutanenta. Sai aka koma kan qwari inda aka tava bayani a kan ma'anarsu da rabe-raben su da siffofinsu. Haka kuma an kawo bayani a kan muhimman halayen qwari waxanda suka haxa da yaxuwarsu da yadda suke reno da abincinsu da zamantakewa a tsakaninsu. Babin ya qunshi bayanai a kan amfani da illolin qwari.

BABI NA BIYAR.

QWARI A ADABIN BAKA DA WASU AL'ADUN HAUSAWA.

5.0. Gabatarwa.

Wannan babi zai yi bayani ne a kan tasirin qwari ga adabin baka da al'adun Hausawa. An bayyana ma'anar tasiri da muhimmanci ko dangantaka ko qarfi. Saboda haka a babin za a yi bayani gwargwadon hali a kan dangantakar da ke tsakanin Bahaushe da qwari, wadda ta sa qwarin suka yi naso cikin al'amuransu. Wannan ya ba su damar yin amfani da su wajen gina da qara fito da adabinsu da al'adunsu, ta hanyar sarrafa su cikin kyakkyawan azanci domin inganta rayuwarsu. Bahaushe ya fahimci qwari sosai shi ya sa ya yi amfani da su a vangarori na hikima da sarrafa harshen Hausa.

Bahaushe na shigar da qwari cikin adabinsa ta hanyoyi guda uku. Ko dai ya yi amfani da sunayensu kai tsaye, ko kuma ya yi amfani da qirar jikinsu ko halayyarsu. Ana amfani da sunayensu kai tsaye don a fito da qwarin ko don a ji wata rawa da suka taka. Yawanci amfani da sunayen na yin alaqa da irin hali na qwaron. Ke nan da an ambaci sunan qwaron mai sauraro ko karatu zai qudurta abin da ya sani game da halayyarsa. Haka nan Bahaushe na amfani da halayen da ya fahimta game da qwarin wajen fifita ko qara wa wani daraja ko qasqanta shi. Haka kuma yana duba yadda halittar jikin qwaro take ya shiryar da ita cikin vangarorin hikima don a qwarzanta wani ta hanyar siffanta qirar jikinsa ko halayyarsa da wani qwaro mai kyau, ko kuma don a wulaqanta siffar jikinsa ko halayyarsa da wani mummuna ko macucin qwaro. Ga misalan wasu daga cikin qwarin da Bahaushe ke amfani da sunayensu don su nuna halayya ko siffar jikin mutum na da alaqa da ta qwaron:

- Xan kunama-mugun mutum.
- Gamaxixi-mutumin da ba ya gajiya da jima'i.

- Gyare-mutum mai surutu da yawa.
- Gwano- mutumin da ke da warin jiki.
- Quda- qazamin mutum.
- Kaska- mutum wanda ba ya da aikin yi sai maula.
- Kazunzumi- mutumin da ya dogara a kan samun wasu.
- Sauro- mutumin da ba ya da qiba.

A taqaice dai, babin ya qunshi nason da qwari suka yi cikin wasu vangarorin adabin baka da wasu al'adun Hausawa.

5.1. Ma'anar Adabi.

Ra'ayin manazarta harshen Hausa ya haxu a kan cewa asalin kalmar adabi daga larabci ne wato "adab". Kamar yadda Muhammad (2003) ya bayyana:-

A lokacin jahiliyya kafin bayyanar Musulunci a wurin Larabawa kalmar na nufin "a kira jama'a zuwa ga cin abinci da aka shirya, wato walima ko liyafa". Bayan shigowar addinin Musulunci sai ma'anar ta juya ga addini da abubuwa masu kyau kamar ladabin cin abinci da ladabin zance da sauransu. Da tafiya ta yi nisa kalmar ta faxaxa ta qunshi wasu dangogin ilimi kamar ruwayar labari da tarihin nasaba da waqoqin baka da harshe da nahawu da tasrifi da sauransu. Lokacin da Musulunci ya shigo qasar Hausa tare da harshen Larabci, sai

Bahaushe ya xauki kalmar ya sa ta cikin Hausa ta hanyar sake mata suna ta koma "Adabi" daga baya kuma sai aka faxaxa ma'anar kalmar ta haxa da dukkan wani bayani da ya qunshi wata hikima da aka yi da harshen Hausa. Ke nan ana iya kallon adabi a matsayin sarrafaffen harshen wanda ya qunshi wata hikima ta musamman mai bayyana rayuwar wata al'umma (Muhammad, 2003:1).

A wata faxar kuma an bayyana ma'anar adabi da:

"Zantuttukan da suka qunshi fasaha ko suka bayyana nau'o'in azanci a fannonin rayuwa iri daban-dabam don koya wani darasi ga al'umma walau furuci ko a rubuce. Haka kuma adabi shi ne hoton rayuwar al'umma wanda ke nuna fasahohinsu da qwarewarsu da ci-gaban da suka samu wajen iya sarrafa harshensu da ma rayuwarsu gaba xaya (Xangambo, 2008:2).

5.1.1. Rabe-raben Adabi.

Adabin Hausa ya kasu zuwa gida biyu, adabin baka da rubutacce.

5.1.1.1. Adabin Baka.

Adabin baka shi ne adabin da Hausawa suka gada daga iyaye da kakanni. Irin wannan adabi ana faxar shi da baki ne don haka ne ake kiran shi "adabin

ka” ko “adabin baka”. Amma dai sunansa na yanka shi ne adabin gargajiya, domin adabi ne da ke qunshe cikin rayuwar yau da kullum wanda tushensa ya taso daga kakanni. Misalan adabin baka sun haxa da tatsuniya da karin magana da kirari da almara da waqoqi da sauransu.

5.1.1.2. Rubutaccen Adabi.

Irin wannan adabin shi ne wanda Hausawa ba su gaje shi ba daga iyaye da kakanni. Wato da can kafin zuwan Musulunci da zuwan Turawa babu shi. Da yake wannan adabin ya zo wa Hausawa tare da koyon rubutu sai suka dinga rubuta shi don haka ne ake kiransa rubutaccen adabi amma sunansa na yanka shi ne adabin zamani. Misalan irin wannan adabi su ne rubutattun waqoqi da rubutattun labaran zube da rubutattun wasannin kwaikwayo.

5.2. Qwari a Labarun Zube.

5.2.1. Tasirin Qwari a Tatsuniyar Hausawa.

Tatsuniya abu ce mai muhimmanci qwarai ga al’ummar Hausawa don ta kasance kamar makarantar farko ga yaran Hausawa. Wani abin lura shi ne labarun da ke cikin tatsuniyoyin ko sun kasance na ‘yan’adam ne, ko na aljannu ko na dabbobi, ko na qwari, ko ma dai na wace irin halitta ce suna nuni ne ga halayya ta gari ko mummuna. Bugu da qari kuma ana bayar da tatsuniyar ne don a xebe kewa kuma a koyar da darussan rayuwa masu amfani ta hanyar horo da hani.

Tatsuniya wata hanya ce ta dabara wadda ake

Sarrafa harshe tare quqqulla wasu magaganu

Na basira cikin azaci don a isar da wani saqo

Ko cimma wani buri (Muhammad, 2003:6).

A ra'ayin Yahaya (1974)

Tatsuniya dai labari ne wanda tsofaffi suke yi wa yara da fatar baki. An fi yin ta da dare, bayan cin abinci yara sukan taru a gida wata tsohuwa ko amarya mai iya bayar da labari. A wasu lokuta akan haxa sauraron tatsuniya da wasu ayyuka kamar saqa ko xura dutsen wuya ko varar gyaxa ko kaxi da sauransu (Yahaya, 1974:1).

Tatsuniya kamar yadda Nata'ala (2010) ya nuna ,

"labari ne qagagge wanda ake amfani da mutane ko dabbobi ko tsuntsaye ko qwari a matsayin taurari don fitar da darasin da ake son fitarwa (Nata'ala, 2010:172).

Shi ko Usman (2005), cewa ya yi

Tatsuniya labarai ne da ke xauke da wasu halaye nagari da hanyoyin warware wasu matsaloli na rayuwa da yin ishara game da wasu abubuwa da sukan faru ga masu aikata munanan halaye kamar mugunta da qwaxayi da wulaqanci ko zalunci ko kishi ko sata da cuta da sakarci da qarya. Ko kuma ga masu aikata

kyawawan halaye kamar aikata alheri da nuna

mutunci da soyayya da ladabi da biyayya da

riqe amana da sada zumunci (Usman, 2005:2).

A al'adance kuwa, tatsuniya labari ne mai xan tsawo da ake qagawa cikin azanci don biyan wata buqata da isar da saqo zuwa ga yara qanana don koya masu tarbiyya da ilimin wasu sana'o'i na vangaren al 'ummarsu.

Yawanci mutane sun xauka tatsuniya qarya ce, labarun ba su tava faruwa ba qago su ake yi, kuma ana yin ta ne kawai don nishadi. To wannan gaskiya ne don labarun ba su tava aukuwa ba. Amma idan aka duba abin da ke qunshe cikinta za a ga cewa labarun suna koyar da halayen zaman duniya. Ke nan ilimin zaman duniya ne zalla cikin tatsuniyoyi.

Tatsuniya tana da matuqar muhimmanci a cikin al'adu da hikimomin Hausawa na gargajiya domin baya ga nuni ga kyawon halayen kirki da munin halayen banza tana nuna adabi da al'adun Hausawa. A cikin tatsuniyoyin, akan siffanta waxansu dabbobi, da tsuntsaye, da qwari da wasu halaye da suka dace da su. Wannan na nuna irin nason da halittun suka yi cikin tatsuniyoyin Hausawa. Akan qaga labarai a kan qwari na gida da na dawa, a ba su matsayi irin na mutane a ce suna magana ko tafiya ko wani aiki irin na mutane. Daga cikin qwarin da ake yawan amfani da su cikin tatsuniyoyi akwai gizo da qoqi da kunama da quda da tururuwa da sauransu.

Akwai tatsuniyoyi masu yawa waxanda ake amfani da gizo wurin shirya su, kuma a yawancinsu akan nuna cewa yana da wayo qwarai da gaske, wayon nasa ya yi yawa har yakan yi amfani da shi ya cuci matarsa qoqi da sauran dabbobi ko waxansu mutane da ke cikin tatsuniyar. Sai dai wasu masana misali Vavura (2008) a maqalar da ya rubuta mai suna "Ceto Gizo daga Gizo-gizon Al'adun duniya", da Qaraye (1978) a maqalar da ya rubuta mai suna "Beyond

the Illusive Cobwebs of the Spider", sun bayyana cewa gizo-gizo ba shi ne gizo ba, amma kuma marubuta labaru da tatsuniyoyin Hausawa sun nuna cewa gizo-gizo shi ne gizo, misali a litattafan da Ibrahim Yaro Yahaya ya rubuta musamman waxanda suka shafi labarin gizo da matarsa qoqi ya suranta gizo da yin kamanni irin na gizo-gizo (spider) a zanen ya yi masa fuska irin ta xan'adam da qafafu irin na gizo-gizo da zanen gidansa a bayansa, qila hakan ba ya rasa nasaba da irin wayo da dabara da gizo-gizo ke da shi.

A nawa ra'ayin na kawo misalan tatsuniyoyin da aka yi amfani da gizo domin ina ganin shi ne gizo. Saboda daga bayanan da na samu game da gizo-gizo na gano lalle shi halitta ne mai gwaninta da wayo da dabara. Haka kuma a yawancin misalan gizo na fitowa a matsayin mai wayo da dabara kuma a kullum shi gani yake dabararsa za ta fitar da shi daga haxarin da ya jefa kansa.

To ko dai me ke nan, gizo ya fito cikin labaru da tatsuniyoyi masu yawa. Misali idan muka duba tatsuniyar gizo da vaure, inda sarki ya nemi wanda zai tsinke nunannen vauren da ke gonarsa ba tare da ya sha ba, idan ya gama zai ba shi auren 'yarsa tare da gararta. Gizo ya ce shi zai iya, sai ya hawo itaciyar ya tsinke vauren duka amma kuma sai da ya sha iyakar shansa. Daga qarshe dai asirinsa ya tonu don yana ji yana gani ga amarya an kawo tare da gararta wata tsuntsuwa ta tona masa asiri ta hanyar rera wannan waqa:

"Kai gizo, kai gizo,
a can ka ci vaurenka,
har ka kurkure bakinka,
har ka manto jallonka (Yahaya, 1971:1-12).

Jigon wannan tatsuniyar shi ne munin rashin gaskiya da cin amana. A cikinta mun ga rashin gaskiyar da gizo ya yi, tun da an ba shi amana amma bai riqe ba kuma a sakamakon haka sai ya rasa amarya da gararta wadda sarki ya yi alqawarin zai ba shi idan har ya tsinke vauren bai sha ba. Tsuntsuwa kuma ta

faxi gaskiya don ta tona wa gizo asiri ta hanyar rera waqar da ta yi. A tatsuniyar an fito da halayyar gizo ta zahiri ta wayo da dabara don a ganinsa zai ci riba biyu, ga vaure ya sha ya qoshi sannan kuma ga amarya har da gararta za a kawo masa. Saboda wayonsa ne ya yi amfani da ruwa ya wanke bakinsa kuma har ya yi ta zubar da miyau don ya nuna wa mutane cewa bai sha vauren ba.

Haka kuma akwai tatsuniyar da aka nuna gizo ya yi amfani da irin dabararsa ya ceci wani yaro daga hannun dodo. Misali daga tatsuniyar Xankaxafi. A tatsuniyar an nuna cewa wata mata ba ta tava haihuwa ba sai ta roqi Allah ya ba ta xa ko da xan kaxafi ne. Da wahala ta ishe ta sai ta je wurin malami ta nemi ya ba ta maganin yadda za ta rabu da yaro. Ta sami nasara don ta rabu da yaro ta hanyar ba shi nama ta kai shi dokar daji ta yar, sai dodo ya xauki yaro ya aza bisa doki. Da gizo ya gan su sai ya yi amfani da dabararsa ya sauke yaro daga doki shi ya haye. Daga qarshe dai kurciya ta kuvutar da gizo ta hanyar xauke shi a fukafukanta (Yahaya, 1971:19-25).

Tatsuniyar na nuna mana idan mutum zai yi roqo ya bar wa Allah zavi. Matar da ba ta tava haihuwa ba ta cikin tatsuniyar da ta haqura da hakan da ta zauna lafiya. Haka kuma an fito da illar qwaxayi tun da kwaxayin ne ya sa kura ta goya xankaxafi saboda ya ba ta nama amma daga qarshe sai da kyar aka raba shi da ita. Gizo ya xauke yaro ya haye dokin dodo shi kuma kurciya ta cece shi.

A nan an fito da halayyar gizo ta yadda ya yi dabara har ya ceci yaro daga wurin kura, don bayanai sun nuna cewa shi qwaro ne mai dabara. Idan zai kama qwaro sai ya fitar da wani zare-zare yayi kamar ya yi wa kansa talala. Idan qwaron da ya kama ya yi qoqarin ya tashi ba zai iya tafiya ba saboda ya xaure shi. A tatsuniyar an koya darasin da ke nuna taimako abu ne mai kyau, kuma duk wanda ya taimaki wani Allah zai taimakesa.

Bahaushe ya yi amfani da gizo wajen aiwatar da tatsuniyoyi. A ciki an fito da halaye daban-dabam waxanda aka alaqanta da shi kamar wayo, da

dabara da cuta. Sannan Gizo na iya fita daga kowane haxarin da ya shiga da sauransu. Alaqanta gizo da wayo da dabarun da yake yi wajen kuvuta daga halaka da Bahaushe ya yi ba abin mamaki ba ne. A cikin babi na huxu qarqashin kariya mun ga yadda gizo-gizo ke qoqarin kare kansa daga abokan gaba ta hanyar dunqulewa wuri xaya, ko kuma idan abin ya vaci sai ya valle qafarsa ya ruga don neman tsira. A taqaice, idan mutum ya duba yadda gizo-gizo ke saqa gidansa, ya san Allah ya yi masa baiwa da wayo da basira.

Akwai tatsuniyoyi masu yawa waxanda a ciki Bahaushe ke nuna mutum ya rikixe ya koma quda don ya bi wani ko wata zuwa wurin da ba a so ya je. Qila wannan bai rasa nasaba da qarantarsa da halayyarsa ta naci da manne wa abu. Misali cikin tatsuniyar yarinya da dodanni, a cikin tatsuniyar wata yarinya mai tsananin kyau ta ce ba ta son kowa sai maras tabo. Da ta sami miji sai aka ce za a ba ta qanwarta ta taya ta zaman xaki, sai ta ce ba ta so. Da aka yi, aka yi su tafi tare ta qi, sai qanwar ta rikixe zuwa quda ta maqale mata, daga qarshe kuma sai ga shi qanwar ce ta taimaka mata suka gudu, bayan sun gane mutumin da yar ta aura, dodo ne ba mutum ba (Yahaya, 1971: 34-35).

Abubuwan da tatsuniyar ke koyarwa sun haxa da illar taurin kai rashin gaskiya da yaudara don abin da dodanni suka yi yaudara ce ita kuma yarinyar don ta ga tana da kyau shi ya sa ta ce ba ta son mai tabo. Kuma ta ce ba ta son qanwarta ta raka ta, da ma Hausawa na cewa “wanda bai ji bari ba ya ji hoho”. Haka kuma tatsuniyar na xauke da jigon kyawun yin taimako. A tatsuniyar an nuna cewa an rikixar da yarinya zuwa quxa saboda sanin halayyar shi ta idan ya ga abin da yake so sai ya manne masa, a yi ta kora amma yana komawa ya manne. A tatsuniyar an yi amfani da sunan quda kai tsaye sannan kuma an fito da yadda qirar jikinsa ke bashi damar maqale wa abu ta amfani da qafafunsa. Ina ganin saboda haka ne qudan ya taka rawa cikin tatsuniyar.

Saboda sanin halayyar quda da qazanta, Bahaushe na amfani da shi a duk wuraren da yake son ya nuna abu mara kyau ko mai qasqanci ko wanda ba ya da tsafta. Misali a tatsuniyar Ruwan Bagaja, Bora ta kora ‘yarta don ta samo arziki kamar yadda ‘yar mowa ta samo. Amma da yake ba ta da xa’a kamar ‘yar mowa, da aka ce kar ta fasa qwan da aka ba ta sai ta je wurin da ba kowa, sai ta qi. Tana zuwa wurin da ke da jama’a sai ta fasa. Taa fasawa sai ga taron kutare sun baibaye ta, suka raka ta ga qudaje na bin ta buu (Yahaya, 1971:32-33).

Dangantakar tatsuniyar da qudan da aka yi amfani da shi shi ne don a fito da halayyar quda da alaqar shi da qazanta. Domin a zahiri ba a raba shi da wurin da wari da najasa ta ke. An nuna cewa abin da ‘yar mowa ta yi ba mai kyau ba ne sakamakon haka ne abu mara kyau ya same ta. Duk abin da a ka ga quda na biye da shi to abin ba mai kyau bane. A tatsuniyar an yi amfani da sunan quda kai tsaye. Sannan kuma an fito da halayyarsa ta bin abu mai qazanta.

A cikin tatsuniyar Nagoma qwari sun kasance abincin dodanni.A tatsuniyar mun ji yadda dodanniya ta ce ba za ta bayar da shi ga ‘yan’uwansa ba sai sun kai mata fansar shi. Sai baban Na goma ya ce a kai mata buhunnan hatsi, wato irin abincin da mutane ke ci a matsayin fansa. Amma da aka kai mata sai ta ce:

“Ba ci na ba,
Na goma ba ci na ba.
Je ka ku canzo,
Na goma, je ka ku canzo”.

Saboda haka sai baban Na goma ya sa aka kai mata taikin quda xari da gomiya bakwai, taikin tsutsa xari da gomiya bakwai, taikin kyankyaso xari da gomiya bakwai, taikin gwano xari da gomiya bakwai, taikin tururuwa xari da gomiya bakwai, taikin kiyashi xari da gomiya bakwai. Ai da dodanniya ta ga wannan gara na irin abincin da take so nan da nan sai ta ce:

“Ga ci na nan Na goma,

ga ci na nan” (Yahaya, 1971: 34-45).

A tatsuniyar an yi amfani da sunayen qwari. An jero sunayensu aka nuna su aka kai wa dodanniya a matsayin fansar Nagoma. Haka nan an nuna cewa qwarin su ne irin abincin da dodanniyar ke ci domin da aka kai mata hatsi sai ta nuna ba irin wannan abincin take so ba. Saboda haka a madadinsu sai aka kai mata qwari. Tatsuniyar ta fito mana a zahiri cewa dodo da mutum ba xaya suke ba, haka nan abincinsu ma ba xaya ba.

Bahaushe ya san halin kunama saboda tasirin da ta yi a rayuwarsa, ita qwaranya ce mai saurin fushi da cuta, a dalilin haka ne aka yi wata tatsuniya ta maciji da kunama inda aka nuna halayyar kunama ta saurin fushi da cuta. A tatsuniyar, kunama ta je wurin maciji ta nemi ya ba ta dafi. A qarshen tatsuniyar maciji bai ba kunama dafi ba don shi kansa sai da ta harbe shi, da ya haye ta bai sani ba. (Ka yi ta Karatu, 1971:32).

A tatsuniyar an yi amfani da sunan kunama kai tsaye sannan kuma an fito da halayyarta ta qeta da saurin fushi da harbi. Tatsuniyar na koya mana cewa saurin fushi ba ya da amfani sannan yana sa mutum ya aikata abin da zai sa ya yi da na sani. Wannan ya nuna mana gaskiyar maganar nan ta Hausawa da ke cewa “saurin fushi shi ke kawo da na sani”. Idan da kunama ba ta yi sauri fushi ta harbi maciji ba, da ya ba ta abin da ta je nema.

Bahaushe na amfani da gara cikin tatsuniya. Misali a tatsuniyar gizo da hankaki an nuna yadda kura ta roqi gara ta tsinka mata igiyar da aka xaure ta. Gara ta ce wa kura “ai ku ne in an yi maku rana sai ku yi wa mutum dare”. Sai kura ta ce “Allah ba zan yi miki ba”. Sai gara ta bi vawon kalgon da aka xaure kura ta taune sarai, amma da yake kura ba ta da alqawari da ta ga ta kuvuta, sai ta tashi ta lashe garar ta tanxe baki ta je ta sami gindin wata kanya ta kwanta abinta (Yahaya, 1974:10).

Bahaushe na amfani da gara cikin tatsuniyoyi. Yawanci ana nuna ta yi wani aiki har ta gama ba a ga tana yi ba. Wannan ko ya samo asali saboda yadda halittarta take. Tunda za ta yi ta yin varna ba tare da an san tana yi ba.Haka nan an bayyana cewa gara tana da baki mai tauri wanda ke ba ta damar xiba da tauna abubuwa masu tauri saboda yadda yanayin abincinta. A tatsuniyar an yi amfani da sunan gara kai tsaye da yadda qirar bakinta ke bata dammar tauna abubuwa masu tauri. Tatsuniyar na koya wa yara kada su rama alheri da mugunta kamar yadda kura ta yi. Ga shi gara ta taimake ta amma da ta ga ta kuvuta sai ta lashe ta.

A wasu tatsuniyoyin an yi amfani da qwari don a yi wa mutane hannunka mai sanda a nuna masu ya kamata kowa ya tsaya matsayinsa don wuce gona da iri ba abu ne mai kyau ba, kuma yana iya jawo halaka. Ga misali daga tatsuniyar qadangare da abokansa. A tatsuniyar da qadangare da quda da gishiri da man kaxanya suka yi abota. Wata rana suka yi shiri suka tafi yawon neman arziki ganin cewa fatauci na jayayya da su sai sauran maqwabtansu suka riqa yi masu dariya da kallon hadarin kaji. Suka yi sammako suka fita gida, can zuwa rana tsaka sai zafin rana ya kama man kaxe nan take ya narke, sauran abokan tafiyarsa suka yi ta yi masa dariya suna cewa tasa ta qare. Jim kaxan sai ruwan sama ya kufce, nan take sai gishiri ya narke kamar da xai duniya ba a tava yin sa ba. Da quda da qadangare suka yi dariya suka wuce gaba. Ba a daxe ba sai suka tarar da wani majemi an kawo masa abinci mai zafi yana jiran ya sha iska sannan ya ci, sai quda da ma “wajen qwaxayi yake mutuwa” ya yi suka ya faxa cikin abincin ya mutu. Sai qadangare ya yi ko oho da abin da ya faru ga quda yana ganin laifinsa ne. Qadangare ya shiga duniya neman arziki ya ko samo sa’a don ya samo abinci iri-iri waxanda za su ishe shi tsawon rayuwarsa kamar su shinge da kiyashi da shazumami da sauransu. Sai da ya gama wahalar xauko kaya ya kawo gida sai ya tarar da wani qasaitaccen muzuru yunwa ta

koro shi daga gidansa bai yi wata wata ba sai ya dafe qadangare ya cinye (Nata'ala, 2010:173).

A tatsuniyar an yi amfani da sunan quda kuma an fito da halayyarsa ta kwaxayi. Domin quda duk inda ya ga wani abinci ko wani abu da yake so sai ya baibaye shi. A tatsuniyar halayyarsa ta kwadayi ta kai shi ga halaka. Haka kuma an ambaci sunayen wasu qwari waxanda aka ce qadangare ya samo a matsayin abincinsa, da ma qwari abincin qadangaru ne. Tatsuniyar na koya wa yara idan wata masifa ta faxa wa wani na kusa da su kar su yi murna. Don su ma tana iya faxa masu. Wannan labari ya yi daidai da karin maganar Hausawa mai cewa "idan ka ga gemun xan'uwanka ya kama wuta, shafa wa naka ruwa".

Daga qarshe saboda muhimmiyar alaqa ko tasirin da qwarin suka yi ga tatsuniyoyin Hausawa, kafin a fara ba da tatsuniya dole ne sai an xaure gizo, idan ko ba haka ba mutum zai yi makuwa, haka kuma wajen rufe tatsuniyar ma ga abin da ake cewa: "Kurungus kan xan vera, ba don gizo ba da na yi qarya da ma qaryar na giggilla. Ba don qarya, qarya ce ba, qadangare ya yi kashi ya ce mata su sai alli kiyashi ya ce uwaka ba ta kaxi ne".

5.2.2. Tasirin Qwari a Hikayar Hausawa.

Hikaya kalma ce ta larabci, Hausawa suka aro ta suka saka ta cikin kalmominsu, kuma suka bar ta a yadda take ba tare da yi mata sauyin qira ko ma'ana ba.

A lugga, kalmar tana nufin ciratowa ko

naqaltowa, ko kwaikwayo, ko kuma ba

da bayanin abu amma a fannin ilimi.

Hikaya ta qunshi labaran da ake ba da wa

na abin da ya faru dangane da mala'iku

ko aljannu ko rauhanai ko mutane ko dabbobi ko tsuntsaye ko qwari da sauransu. Tun asali

> *Hausawa suna da labarai na hikaya waxanda suke bayarwa amma kuma akwai wasu da dama waxanda suka samu daga Larabawa. Saboda haka ana iya cewa tasirin al'adun gargajiya da hulxa tsakanin al'umomi, da shigowar addinin musulunci da karatun litattafai su suka haifar da samuwar hikaya* (Yahaya, 1998: 14-15).

Haka nan Muhammad (2003) ya bayyana cewa:-

> *Akan bayar da hikaya a lokacin hira don hana qosawa da samun nishaxi da jin daxin zama. Haka nan kuma ana bayar da hikaya a lokacin da ake karatun litattafai a zaure ko lokacin neman wani magani a wajen bokaye, ko kuma idan an yi kicivis da wani abu da ke buqatar kawo misalai. A dangane da haka, yawanci malamai musamman na zaure da manyan mutane da bokaye, da samari ne suka fi yin hikaya* (Muhammad, 2003:23).

Hikaya tana isar da saqonni daban-dabam kuma mafi yawancin saqonnin isharori ne ga jama'a don su kyautata halayyar rayuwarsu ta duniya da ta lahira, kuma tana kawo nishaxi da raha da hana zaman banza.

Akwai hikayoyi da dama waxanda akwai qwari cikin tubalan gininsu, kuma idan mutum ya nazarci wuraren da aka yi amfani da qwarin da irin rawar da suka taka cikin hikayoyin, za a tarar cewa rawar ta dace da irin halayyarsu a zahiri.

Hikaya ta farko da za a kawo a matsayin misali ita ce mai suna "Wasiyyar Uba cikin Hikima". Wannan ta qunshi labarin wani mutum wanda kullum yakan riqa yi wa xansa wa'azi kan sha'anin zama da mutane. Kafin uban ya rasu sai ya ce wa xansa akwai wasiyyoyi da yake so ya gaya masa amma zafin ciwo ba zai bar shi ba. Saboda haka sai ya umurce sa da bayan ya rasu ya je wajen tsohon doki da kiyashi da kumurci da kare za su gaya masa abin da ya so ya gaya masa. Bayan uba ya rasu sai yaro ya je duk wuraren da mahaifinsa ya bar masa wasiyyar ya je. Da ya je wurin kiyashi sai ya ce masa lalle ko akwai wasiyya ya biyo shi ya ga abin da babansa yake nufi. Suna cikin tafiya sai suka yi kicivis da mushen kyankyaso. Sai kiyashi ya ce masa "ka ga wannan mushe ba shakka ya raba ni fiye da xari a girma, saboda haka ba zan iya jan shi in kai rami na ba ga shi kuma ina so saboda abinci na ne. Sai kiyashin ya kirawo kiyasai rututu suka ja mushen kyankyaso cikin raminsu. Daga qarshe dai kiyashi ya faxa wa yaro cewa komi zai yi kada ya yi shi kaxai sai da jama'a (Kano, 1979:16-18).

A wannan hikaya an yi amfani da kiyashi, kuma an fito da halayyarsa ta yin komi a tattare domin idan ya ga abincinsa nan da nan za ka ga sun taru da yawa sun dabaibaye. A hikayar an yi amfani da hikimar kiyashi ta eman taimakon juna idan buqatar haka ta taso don a koya wa yara darasi. Hikayar na jawo hankali da koya wa mutane muhimmanci taimako da haxin kai.Idan aka yi la'akari da ximbin hikimomin da ke cikin hikayar za a ga cewa an yi amfani da

kiyashi ne don a koya wa mutane yadda za su ingata rayuwarsu da yadda za su warware matsaloli tare da samun rayuwa mai inganci.

Hikaya ta biyu da za a kawo misali wadda aka yi amfani da qwari wajen gina ta ita ce mai suna “Zaman Sauro tare da Kunne da Hannu”,

Sanannen abu ne sauro ko da yaushe yana zuwa wajen kunnen mutum yana kuka kamar zai shige ciki kuma ko yaushe hannun na kai kora. To game da wannan, masu hikima sun ba da labarin cewa dalilin wannan shi ne, akwai lokacin da sauro, da kunne, da hannu suke zaune a gida xaya.Wai wata rana sauro ya kama hannu ya shiga xakin kunne ya xebo gari. Sai ya roqe shi da ya ya rufa masa asiri, kada ya gaya wa kunne abin da ya faru. Wata rana sai husuma ta tashi tsakanin sauro da hannu har hannu ya yi wa sauro ba’a, shi ne sauro ya fusata ya ce wa hannu sai ya tona masa asiri. Wannan dalilin ya sa kullum sauro ya tafi ya gaya wa kunne wannan magana sai hannu ya kai masa duka (Kano, 1979: 32-33).

A hikayar an yi amfani da halayyar sauro inda aka nuna yadda yake da nacin bin mutun duk inda yake ya yi ta bin kunne yana kuka. Haka kuma an fito da sifar shi ta qanqanta ta yadda zai iya shiga kunne ba tare da wata wahala ba. Kuma a koda yaushe hannu bai iya kyalewa sai ya kori sauro idan ya kai ga kunne ko wani vangare na jiki. An yi amfani da sauro ne don a koya wa mutane cewa cin amana da sata ba su da kyau.

5.3. Tasirin Qwari a Zantukan Hikima.

Zantukan hikima sun qunshi ‘yan guntayen maganganu ne ko zantuka da ke zuwa gava-gava ko gunduwa-gunduwa domin isar da wani saqo na musamman waxanda ake tsarawa da ka. Zantukan hikima al’ada ce ta Hausawa daxaxxiya wadda ba za a iya cewa ga lokacin da aka fara ko aka qage ta ba. Hausawa na aiwatar da su ne saboda nishaxantarwa da ban dariya tare da havaka harshe da koyar da darussan zaman duniya daban-dabam da nasihohi da

isharori da hannunka mai sanda da sauran hanyoyin faxakarwa. Wanan rukuni na adabi ya qunshi karin magana da kirari da kacici-kacici da sauransu.

5.3.1. Tasirin Qwari a Karin Maganar Hausawa.

Karin magana yana xaya daga cikin maganganun azanci na Hausa, kuma ‘yar guntuwar jimla ce ta hikima mai faxakarwa a kan zaman duniya.

> *Karin magana wata yar gajeriyar jimla ce ta hikima wadda ta qunshi ma’ana mai yawa in Za a yi bayaninta* (Muhannad, 3003:59).
>
> *Karin magana tsararren zance ne wanda yake zuwa a gajarce na hikima da zalaqa tare da bayar da ma’ana gamsasshiya mai faxi da yalwa musamman idan aka tsaya aka yi bayani daki-daki. Ashe ke nan, karin magana taqaitacciyar magana ce ‘yar qil wadda ta qunshi hikima da zantuttuka masu ma’ana* (Yahaya, 1992:30).

Ta hanyar karin magana mutum na bayyana abin da ya dame shi, kuma idan aka fexe ta dalla-dalla tana qunshe da magana mai ximbin yawa. Sannan kuma ga nuni zuwa ga horo da hani nagari waxanda kan qara wa mai yi da saurare hikima da basira da fasaha mai tarin yawa. Ta hanyar karin magana ana iya nuna wa mutum kirki ko rashin kirkinsa maimakon a fito qarara a faxa masa. Wato dai ana iya faxakar da mutum a yi masa nuni ko hannunka mai sanda ko habaici ko gori ko shakiyanci ko sharri da sauransu. Kuma saka ta a cikin zance na qara wa zancen armashi, sai mai sauraro ya ji maganar ta yi kyau da ma’ana.

Wata karin maganar na sa a yi dariya da farin ciki amma wata idan aka ji ta sai rai ya vaci.

Karin maganganu sun fito ne daga cikin rayuwar al'umma shi ya sa suka qunshi yawancin abubuwa da suka shafi vangarorin rayuwa. Yana da wuya a ce ga mutumin da ya qago ta, amma ana iya cewa naso ne na al'adu da xabi'un Hausawa ya haifar da ita. Sannan kuma karin magana kan zo cikin labaru da zantuka da waqe-waqe da sauransu. Mutanen da suka fi amfani da karin magana cikin zantuttukansu sun haxa da mata da 'yan daudu da mawaqa da maroqa da sauransu. Karin magana a mafi yawan lokuta tamkar kukan kurciya ne. Tana sa magana ta yi armashi da daxi kuma tana nuna gwanintar iya maganar mai magana kuma ta sa mai sauraro rashin qosawa da maganar da ake masa.

Kamar yadda aka bayyana a baya karin magana ta tavo vangarori na rayuwa masu yawa. Wannan ta sa ko ga halittu daban-dabam ba a bar ta a baya ba domin kuwa akwai karin maganganu masu yawa waxanda aka yi amfani da qwari wajen tsara su, kuma yawancinsu idan aka yi nazari ko sharhi a kansu za a tarar an duba halayya ko siffar qwarin ne aka gina su. Hakan ba zai rasa nasaba da irin tasirin da qwarin suka yi ba ga al'ummar Hausawa. Daga cikin karin maganganun da qwari suka yi tasiri ciki akwai:

(1). Qwaron da ya jaraba da wake tare akan dafa su.

Wannan karin magana na nufin duk wanda ya cika naci, qwazzaba da qwaqwa to qarshe yakan yi da na sani. Domin za a kai shi ne a baro, Idan mutum ya nace wa abu aka yi iyakar qoqari a hana shi abin ya ci tura to sai a sa masa ido, wahala za ta raba su. Sannan idan har mutum zai nace wa abu ya dinga bin sa yana matse masa duk da irin wulaqanci da hantara da ake yi masa to babu shakka sai ya yi nadama. Haka kuma karin maganar na nufin kada mutum ya kasance tamkar kaska ko da yaushe yana nan liqe da mutane don neman abin hannunsu kamar yadda halayyar qwaron wake take wanda saboda

nacinsa ba a tava raba su da wake. A qarshe ma sai dai a dafa su tare da waken. A karin maganar an lura da halayyar qwaron wake wanda kullum yana ciki wake aka alaqanta shi da mutum mai naci da qwaqwa.

(2). An ce da qwaxo ba ka cizon kowa, shinge ya ce “ai shi ne shegen”.

Wannan karin magana na nuna mai kirki a wajen wani shi ne macuci a wajen wani. Abin nufi a nan shi ne wanda ake gani ba ya cutar kowa tsakaninsa da al’umma sai alheri, to a wajen wani gwanda kunama da shi. Ba wanda zai taso ya ce kwaxo azzalumi ne ko macuci. Kusan babu ruwansa da kowa. Amma shinge ya san ko wane ne kwaxo domin tsakaninsu tamkar Annabi ne da kafiri wato babu jituwa ko ta sisin kwabo. Domin da sun ci karo sai ya haxiye shi. Ke nan duk irin yadda sauran qwari za su yabi kwaxo, shinge kallonsu kawai yake domin tsakaninsu babu jituwa. Saboda haka karin maganar na nuna duk yadda aka samu mutum na kirki mai halin qwarai, dole ne a samu wanda tasu ba ta zo xaya ba. Wato ba wanda ba ya da masoyi kuma babu wanda ba ya da maqiyi.

(3). A ci qungurguma a ci buzuzu.

Karin maganar na xauke da ma’anar a gudu tare a tsira tare. Wato idan daxi ya zo a ci shi tare idan kuma wahala ta zo a ci ta tare. Ko kuma duk abin da ya faru to a gudu tare a tsira tare. Kuma tana iya xaukar ma’anar duk abin da aka samu babu zavi, sai a yi amfani da shi. Ta wata fuskar kuma ana iya bayyana wannan karin maganar da ya ki halal, ya ki haram wato duk abin da ya zo hannu to ya zama nama. Da qungurguma da buzuzu duk qwari ne kuma suna kama da juna. An alaqanta karin maganar da su don a nuna cewa kamar yadda suke kama da juna, haka duk abin da ya zo a xauke shi a yadda ya zo.

(4). Idan tururuwa ta kusa lalacewa sai ta yi fiffike ta tashi.

Wannan karin magana na nuna cewa duk irin matsayi ko muqami ko daraja ko xaukaka da mutum ke da shi da zarar ya aikata wani abu yana iya zubar masa da mutuncinsa. Haka kuma ana iya danganta karin maganar da cewa idan aka turke mutum sai ya kama ‘yan kame-kame don ya samu ya tsira da mutuncinsa. Ta wata fuskar kuma sharhin karin maganar na iya kasancewa idan ka ga mutum na aiwata wasu halaye ko xabi’u to lalle ya xauki wani sabon salo na lalacewa.

(5). Da sauran rina a kaba.

Wannan karin magana na nuna cewa lalle akwai sauran magana a voye. Kuma tana nuna da sauran zance a baya. Wato akwai abin da ba a warware ba. Ana amfani da ita idan ana son a nuna magana ba ta qare ba. Wato mutum bai yi haquri da abin da ya faru ba ke nan qila gaba akwai yiwuwar xaukar fansa. “Da sauran rina a kaba” na nuna cewa, abu bai kai qarshe ba, domin rina ba ta barin kaba ga baki xayanta sai dai wata ta tashi ta bar wata. Haka nan wani kan riqe abu a zuciyarsa ko da za a yi shekara ba zai manta ba bare ya yafe. Yana nan yana jiran damar da zai xauki fansa.

(6). Wuta-wuta haxiyar kunamar qwaxo, tun ba a haxe ba kai ya yi zufa.

Wannan karin magana na nufin duk wanda ya xauko aikin da ya san ba zai iya yin shi ba ya kuma nace lallai sai ya aiwatar, to ko shakka babu zai sha wahala. Wato mutum ya xauko abin da ya fi qarfinsa ko kuma abin da ba zai yiwu ba, ya ce shi zai iya. Ko kuma gabatar da aikin da ke cike da tashin hankali da rashin tabbatuwar aikin saboda tsanani da wahala tare da girmansa ta yadda ba zai haxu ba. A karin maganar an nuna cewa qwaxo zai haxe kunama ga zafin harbi wanda ya haddasa masa yin zufa. A nan mun fahimci cewa, gaba kura baya sayaki. Saboda an fara aiki amma tsakiyarsa ba daxi, ga azaba, ga wahala, ga shi kuma an

nace sai an idar da shi. An danganta karin maganar da kunama saboda halayyarta ta azaba da harbi da ba sani ba sabo.

(7). Ba banza ba quda da warki.

Karin maganar na nuna lallai akwai wani dalili wanda ya sa aka aikata abu. Misali mutumin da kullum cikin qazanta ya ke rannan sai aka gan shi ya yi wanka da wanki ya fito tsaf to ko ba a gaya maka ba ka san lalle ba banza ba, kuma ruwa ba ya tsami banza. Haka kuma ana iya amfani da wannan karin maganar idan aka ga mutum da ba ya da alaqa da wuri ko wani abu sai kawai aka ga ya yi ruwa ya yi tsaki a hidimar wurin to ana iya cewa “ba banza ba quda da warki” da muka ga wane a waje kaza.Ta wata fuskar kuma karin maganar na nuna faruwar wani abin mamaki wanda ba a yi tsammanin faruwarsa ba. An alaqanta Karin maganar da quda da warki tun da abin mamaki ne ko abin al’ajabi. Wato dai idan har aka ga haka ta faru to akwai dalili tun da shi warki ba wurin zaman quda ba ne sai idan akwai wani qwaqqwaran dalili.

8. Xan kunama ne ba don mutum xaya ya ajiye qarinsa ba.

Wannan karin magan ana yin ta ga mugun mutum wanda kowa ya samu yana iya cuta.Wato shi ba ruwansa da ya kamata ko bai kamata ba, duk inda ya ga dama sai ya yi cutar. Ana alaqanta karin maganar da kunama saboda sanin halayyarta ta cuta da mugunta kuma kowa ta samu tana iya harbi.

9. Take taken da ake a gdan galla ba za a yi shi ba a gidan rina.

Wannan Karin maganar ana yin ta don a kwatanta mutane biyu masu halayya daban-dabam. Misali idan ana so a nuna cewa abin da aka yi wa wani mutum mai haquri ko da wasa ba za a iya yi wa mutum mai fushi ba a zauna

lafiya. An kwatanta waxannan qwarin biyu ne saboda halayyarsu ta sha banbam. Rina qwaraya ce mai faxa ita ko galla qwaranya ce wadda ba ruwanta da faxa.

10. Idan kace qananan matsaloli ba wani abu ba ne, to ka kwana xaki xaya da sauro.

Ana yin wannan karin maganar ga mutumin da ake ganin salihi ne ba ya da wata matsala a zahiri amma a baxini mugu ne tunda yana iya jawo wa mutum matsalar da ta fi qarfinsa. Ko kuma wani al'amarin da ake ganin ba na damuwa ba amma daga qarshe ya zama babba. An alaqanta karin maganar da sauro saboda sanin halayyarsa, domin duk wanda ya kwana a xakin da ke da sauro to lalle sai ya yaba wa aya zaqinta.

5.3.2. Tasirin Qwari a Kirarin Hausawa.

Kirari na xaya daga cikin rassan adabin gargajiya, abu ne daxaxxe kuma mai matuqar muhimmanci a qasar Hausa domin ko yana nuna balagar harshe kuma ya zame wa wasu tamkar sana'a. Kirari ya daxe qwarai da gaske don haka ne ma masana daban-dabam suka yi qoqarin bayyana ma'anarsa. Daga cikinsu akwai ma'anar da Muhammad (2003) ya ba da, inda ya ce:-

Kirari wata sarrafaffiyar magana ce wadda

akan yi da baki domin kambama ko kururuta

wata halitta ko wai abu. A nan za a iya yi wa

wani kirari kuma zai iya yi wa kansa.

(Muhammad, 2003:26).

Abdulqadir Umar K/Hausa ya fassara ma'anar kirari da Bergery ya bayar cikin qamus din sa mai suna A Hausa-English Dictionary and English Hausa vocabulary da:-

Kirari waxansu irin maganganu ne da ake yi wa sarakuna ko muhimman mutane da ake bayyana halayensu da kamanninsu ta hanyar kambamawa.

A ra'ayin Galadanci (1993) kuwa:-

Kirari wata tsararriyar magana ce da akan yi don a yabi wani mutum ko a bayyana halayyar wani abu ko yaayinsa ko siffarsa. Akan yi wa mutane da dabbobi da waxansu abubuwa kirari.

(Galadanchi, 1993: 8).

Babu shakka waxannan ma'anoni sun fito da ma'anar kirari a sarari, domin ko sun nuna cewa akan yi kirari ne don yabo ko muzantawa ko kuma don a nuna muhimmancin abu. Amfanin kirari ga mutum shi ne zuga, wato don a ta da masa tsiga yadda zai tashi ya yi wani abin bajinta. Kirarin da ake wa qwari ma mutane ake qwarzantawa, ta hanyar alaqanta halayya ko siffar jikin wanda ake yi wa kirarin da wani qwaro. Su kuma masu yin kirarin suna samun abin kashewa. Su ko sarakuna da sauran mutane waxanda ba masu wasanni ba, kirari na sa su ji wani irin daxi su yi ta fara'a har tsigar jikinsu ta tashi kuma su yi wa maroqan kyauta mai yawa. Masu talla suna yin kirari ga kayan tallarsu, inda suke bayyana wa mutane irin abubuwan da suke sayarwa, musamman irin abubuwan da ba buxe suke a fili ba. Amfanin kirarin sauran abubuwa kuwa kamar su dabbobi da tsire-tsire shi ne yana qarin bayani dangane da halaye ko siffofinsu yadda mutane za su san su, kuma su san yadda za su zauna da su.

A taqaice dai, kirari yana da matuqar muhimmanci, sosai domin kuwa yana adana tarihi da tsofaffin kalmomi. Sannan yana koya wa al'ummar Hausawa qarfin hali da dauriya da jarunta.

Qwari sun yi tasiri sosai cikin kirarin Hausawa domin sun yi wa masu yawa daga cikinsu kirari, kuma kirarinsu na jawo hankalin mutane ne game da halayyarsu ko siffofinsu. Misali a yayin da ake yi wa sauro kirari ana ce masa:-

(1).Kirarin Sauro.

"Lange-lange mai ramar qeta,

Ramamme haukata qato,

Sa mutum ya mari jikinsa,

Mugu hana barci'.

Sauro xan mitsitsin qwaro ne mai zafin cizo da nacin kuka, mai kawo zazzavi ta hanyar zuba wa mutum qwayoyin cuta cikin jininsa. Kirarin na nuna cewa shi sauro duk da qanqantarsa da rama, macuci ne domin baya ga hana barci da yake yi, yana sa mutum ya rasa zama lafiya. Ga shi ya qware wajen baza cuta. Wannan kirarin ana yin sa ga mutumin da yake xan firit amma sai azaba da masifa da kawo tashin hankali. Haka kuma ana yi wa mutumin da ya shahara wajen iya qeta. Ana danganta qananan mutane da sauro ne domin a nuna ba girma ne azaba ba, ana samun mutum xan firit fasa taro, wanda da ka gamu da shi gara ka yi karo da kura goma. Saboda halayyar sauro ta mugunta da fitina da yadda mutane suka san shi, makaxa Babangida Kakadawa ya yi waqa kan sauro inda ya fito da halayyarsa. Matasa da mawaqa ne suka fi yin wannan kirarin.

(2). Haka nan a yayin da ake wa malam-buxe-littafi kirari akan ce:-

"Ya kai mai walkiya,

Ya littafin Allah,

Buxe littafinka”.

Malam-buxe-littafi wani irin qwaro ne mai kyawun gani. Akwai su iri-iri masu launi daban-dabam sannan kuma shi mumini ne. Ba ya yin wata varna idan ya girma. Fukafukansa na da xan faxi kuma suna da launuka daban-dabam masu ban sha’awa. Idan ya buxe su kamar an buxe littafi. Ana yin wannan kirari ne ga malamai, haka kuma ana yin shi ga mutumin da ke neman ilimi wanda a ko da yaushe ba ya da aiki sai zuwa neman ilimi da koyar da shi. Kirarin na nuna girman malanta. Sannan ana kiran shi da “mai walqiya” saboda hasken da ke cikin ilimi. Matasa da yara ne suka fi yin wannan kirari.

(3). Shi ma qudan masai Hausawa ba su bar shi haka nan ba, sai da suka yi masa kirari kamar haka:

“Idrisu babban kuje,

Na masai da wayo ka ke”.

Quda xan qaramin qwaro ne mai tashi, yana da qafafu shida kuma ya fi zama a wuri mai qazanta. A iyakar binciken da na yi ban samu hujja a kan dalilin da ya sa ake kiran quda da sunan Idrisu ba. Kirarin na nuna lalle a ko da yaushe qudan a masai yake. Nan ne mazauninsa saboda a nan abincinsa yake. Wannan kirari ne da ake yi wa mutumin da ke da tsananin wayo na a ci bilis. Abin nufi a nan shi ne duk mutumin da ke da kwaxayi, wanda ke bin hannu mai romo da miya don ya lasa amma ba ya son a ci nashi. Kullum shi qoqarinsa ya hau ba a hau shi ba. Shi ake yi wa wannan kirari. Manya da matasa suka fi yin wannan kirarin.

(4). A yayin da ake wa rina kirari ga abin da ake cewa:

“Rina uwar faxa”.

Rina wata irin qwaranya ce mai kama da zanzaro. Shi zanzaro wani baqin qwaro ne mai siririn jiki da qaton ciki. Rina tana yin gida mai kama da saqar zuma a bisa bishiya. Tana harbi mai zafi kamar zuma. Rina tana da faxa qwarai da gaske. Idan za ta yi harbi sai a fuska ko a kai. Wannan kirari ne da ake yi wa mutumin da ya cika faxa da masifa ko tijara ta ba gaira ba dalili. Da zarar an tavo shi to ba sauran zaman lafiya. Kirarin na bayyana mutumin da ke da faxa kamar dage ga saurin fushi da saurin mayar da martani wanda ba ya barin sai ta kwana da zarar an yi mashi abu. Ana yin wannan kirarin ne idan an haxu da mai irin wannan halin ko kuma aka same shi yana aikata masifa.

(5). Shi ko Zanzaro ga yadda kirarinsa yake:

“Zanzaro sarkin aiki,

Akwai gini ba ruwa”.

Zanzaro wani baqin qwaro ne mai siririn jiki da qaton ciki wanda ke gina gidansa shi kaxai ba tare da ‘yan taimako ba. Yana gina gidan ne da tavo mai qwari a jikin bango ko wani abu. Wannan kirarin ya nuna mana saboda qwarewarsa, idan zai gina gidansa ba ya sa ruwa. Ana yi wa mutum kirari da zanzaro sarkin aiki idan ba ya da hutu a rayuwarsa ko wane lokaci cikin aiki yake. Idan aka gan shi cikin hanzari ko yayin da yake ta kai komo. Kirarin na nuna wanda ke zama sarkin aiki har abin da ke da wuya yana iya aikata shi shi kaxai ko da kuwa zai wahala. Domin gina gida ga zanzaro shi kaxai kuma ba ruwa na nuna cewa lallai aikin ba qarami ba ne. To idan aka sami wanda ke aiwatar da aiki mai wuya shi kaxai kuma ba ya gajiya sai a rinqa yi masa wannan kirari.

(6). Idan za a yi wa qaguwa kirari ga abin da ake faxa:

“Qaguwa tafi karkace”

Qaguwa wata irin qwaranya ce ta ruwa mai siffa irin ta kunama, sai dai ta fi kunama girma, a karkace take tafiya, fuskarta na kallon wuri dabam, sannan hancinta na kallon wuri dabam, wato tana tafiya kwan gaba kwan baya. Abin nufi a nan shi ne duk mutumin da ba ya da matsaya guda, ko wanda ba ya da alqibla shi ake yi wa wannan kirari. Haka kuma duk mutumin da ba ya da tsayayyiyar fuska wato yanzu yana farin ciki da anjima kuma ya murtuke, wanda ba a qiyasta yadda za a same shi ko abin da zai yi ana iya yi masa wannan kirari. Babu wani takamaiman lokacin da wannan kirarin ya kevantu da shi illa dai kawai faruwar wani abu da mutum ya aikata ke ba da damar yin kirarin. Haka nan kuma akan ce “Aiki yana tafiyar qaguwa”.

(7). Kirarin Jiga.

“Jiga cimarki mutane”.

Jiga wata qaramar qwaranya ce da aka fi samu a kurmi wadda jini ne abincinta, kuma ta fi son wuri mai taushi. Wannan ya sa take samun qarqashin farce ta liqe. A nan take rayuwarta har ta mutu. Ana iya yi wa mutum mai naci da qwaqwa wannan kirari.

(8). Haka kuma ga irin kirarin da ake wa kazunzumi.

“Kazunzumi hana barci.”

Ana alaqanta wannan kirarin da kazunzumi ne domin yana da fitina qwarai da daddare, da rana sai ya vuya a jikin katifa ko a tsagar bango. Amma da zarar dare ya yi, sai ya auka wa mutum da cizo kamar ba zai bar shi ya kai safiya ba. Wannan kirari ne da ake yi wa duk wani abu da zai tsaya maka a rai ya dame ka ya sa ka kasa aikata kome har sai ka warware. Haka kuma ana yin wannan kirari ga ’yan qananan mutane masu fitina da cika-ciki. Masu hana a zauna lafiya.

(9). Kirarin zuma.

“Zuma sai da wuta”

“Zuma ga zaqi ga harbi”

Zuma wata qwaranya ce dangin quda, sai dai ta fi quda girma. Launin jikinta fatsi-fatsi kuma tana fitar da wani ruwa mai zaqin gaske wanda ake sha kuma a yi magani. Zuma tana da gida na musamman. Tana da qari da take harbi da shi kuma idan ta yi harbi akwai zafi da raxaxi da zogi. Idan masu xibar zuma suna son su kore ta daga kogonta, sai sun yi mata hayaqi don ta fita. Wannan ya sa ake yi mata kirari da zuma sai da wuta. Idan ba a yi hayaqi ba, ba za ta fita ba. Ana yin wannan kirarin ga mutumin da ke da kyauta amma kuma yana da cin fuska da wulaqanci da nuna isa, ko kuma wanda ke da kyauta da alheri amma kuma idan aka taka shi ko aka yi masa ba daidai ba to zai ci maka mutunci kamar bai tava saninka ba. Wannan kirari na nuna mana cewa ba a samun abu haka nan, dole ne sai an sha wahala an yi zufa kafin a dace

(10). Kirarin qwarqwasa.

“Qwarqwasa fid da mai gida daga gidanshi”

Qwarqwasa qwaranya ce mai naci da qwace abu daga hannun mai shi ta hanyar dabaibayewa da cizo har sai mai abun ya kai ga barin abin gareta. Ita qwalqwasa tana korar duk wani azzalumin qwaro, ta hanyar liqe masa ga jiki ta yi ta cizo. Saboda haka ake mata wannan kirarin, misali in da maciji zai yi rashin sa’a ta shiga raminsa, to sai ta koro shi daga ciki ta hanyar 1iqe masa a jiki. Ana iya yi wa mutum wannan kirari idan ya kasance mai naci sannan kuma idan ya ga abu yana so to dole sai an ba shi idan har ana son zaman lafiya.

(11). Kirarin cinnaka.

“Cinnaka ba ka san na gida ba.”

Cinnaka wani qaramin qwaro ne baqi mai cizo da zafi, ga shi a gida yake tare da mutane amma kuma ko mai gidan sai ya ciza, bai san kara ba kuma kome kusancinka da shi babu ruwansa duk abin da ya kama yai maka ba zai kauda kai ba. Wannan kirari ne da ake yi wa mutumin da yake yanke hukunci tsakaninsa da Allah babu nuna bambanci, idan ana kuranta shi ko ana yi masa kirari sai a rinqa kwatanta shi da “cinnaka” wanda ko da wuri xaya kuke kwana da shi yana iya cizonka.

Wannan kirarin ana yin sa ga wasu kevantattun mutane waxanda suke da kishin qasa da rashin nuna bambanci a tsakanin mutane.

(12). Kirarin Tsirya.

“Tsirya sa baki mai abu bai sa ba”.

Tsirya wani qwaro ne mai vata kayan marmari irn su lemu da ayaba. Idan ya sami kayan marmari sai ya shiga ya huhhuda, ke nan kafin mai kayan ya kai ga ci, har ya sa baki.Wannan kirari ne da ake yi wa masu shaida ‘yan haxa husuma, ko masu neman fada ga wanda aka yi wa wani abu, ko masu shiga sharo ba shanu. Masu shiga maganar da ba ta shafe su ba, ko ‘yan hana ruwa gudu waxanda burinsu su ga an vata wani ko an ci wa wani mutunci.

5.3.3. Tasirin Qwari a Kacici-kacici.

Kacici-na zuwa ne a fasalin tambayoyi tare da amsoshi na biye da su, maganganun kacici-kacici sun qunshi siffofin waxansu abubuwa a cikin tambayoyi kuma amsar tambayar ita ce qwayar abin da ake nufi a cikin tambayar. Yawanci kacici-kacici qalubale ne ko wasa qwaqwalwa ko qarfafa tunanin mai sauraro.

Yara da tsofaffin mata ne suka fi yin kacici-kacici a lokacin da suke tatsuniya da daddare ko wani lokaci na musamman. Sannan yana koyar da tunani ga masu yin sa domin ko sai an yi tunani sosai kafin a samo amsar

tambayar da aka yi, kuma yana qara masu sanin ma’anar harshen su ta yadda za su qara qwarewa da shi su sarrafa shi cikin magana. Yana yawaita musu rumbun kalmomi da nuna dabara da hanyoyin kwarewa da harshe.

A fagen kacici-kacici ma akwai wasu waxanda aka yi amfani da qwari wajen haxa su. Ga misalin wasu daga cikinsu:

(1). Tambaya- Faifaina xinkin marido.

Amsa- zuma.

(2). Tambaya- Makaranta a dokar daji.

Amsa- Gidan tururuwa.

(3). Tambaya- Qarya qarya ce amma tawa ta fi ta kowa.

Amsa- Kiyashi ya naxa gammo zai xauki duniya.

(4). Tambaya- Takalmin kitse maxauki na wuta.

Amsa- Kunama/mai qari.

(5). Tambaya- Xillin bisa xillin.

Amsa- Kunama bisa gyambo.

Idan aka duba misalan da aka yi amfani da su za a ga cewa an yi amfani da halayen qwarin ne aka bayar da amsa daidai da yadda tambayar ta zo.A wasu kuma an dubi siffar wurin zamansu.

5.4. Qwari a Waqoqin Baka.

Waqar baka waqa ce da ake aiwatarwa cikin harshen Hausa kuma ana sadar da ita ta hanyar rerawa. Abu ce daxaxxiya wadda aka fara tun lokaci mai nisan gaske. Ana zaton xan’adam ya qagi waqa ne tun lokacin da ya fara neman

abinci ta hanyar farauta daga nan sai ta yi ta bunqasa saboda noma da yaqe-yaqe.

Masana sun yi qoqarin bayyana fahimtarsu dangane da ma'anar waqar baka, misali a wurin Xangambo:-

Waqa wani furuci ne cikin azanci da ake

isarwa ta hanyar rerawa da daidaita

kalmomi cikin tsari ko qa'ida da daidaita

sautin murya da amfani da dabarun ko salo

mai armashi da sauransu.

(Xangambo, 1986:2)

Gusau (2008) na ganin:-

Waqar baka wani zance ne shiryayye cikin

hikima da azanci da yake zuwa gava-gava

bisa qa'idojin shiryawa da daidaitawa a rere

cikin sautin murya da amsa amon kari da

amshi da kixa (Gusau, 2008:6).

Akwai waqoqi na baka masu yawa waxanda mawaqa suka yi amfani da sunayen qwari ko halayensu ko sifofinsu a ciki. Yawanci suna amfani da sunayen ne don su kambama ko kururuta ko muzanta ko qasqanta wanda ya yi hamayya da ubangidansu wajen neman sarauta, ko wanda bai yi masu daidai ba. Ga misalan wasu daga cikinsu:

Waqar kunama ta Garba Maitandu.

Amshin waqar: Kunama zan wa kixi,
Zama ciwo ag gare ta,
Ta halban jiya.

A cikin waqar makaxa Garba Maitandu ya bayyana kunama tare da sababin da ke tattare da ita, kunama ta yi tasiri cikin zukatan mutane don da wuya a sami wata qabila da ba ta san da ita ba tare da irin sababin da ke tattare da ita, don haka ne mawaqin ya kawo sunayen wurare daban-dabam inda mutane daban-dabam ke tsammanin ake samunta. Makaxin ya faxi irin sababin da ke tattare da harbinta da irin hali na ruxani da mutum ke shiga idan ta harbe shi.

Misalin wata waqa da Salihu Jankixi ya yi wa Sarkin fawa Xandago Tsafe, ga gindin waqar:

Ya fi sarfa kyauta,

Dogo mai lihidin fawa,
Ya da qashi ka huta da quda.

A nan mawaqin ya kwatanta wani wanda ya matsa wa sarkin fawa da quda. Kamar yadda aka sani quda qwaro ne mai naci da bin abubuwa saboda qwaxayi. Shi ya sa ma akwai wata faxa ta Hausawa da suke cewa “a ya da qashi a huta da quda” ko “a ya da qwallon mangwaro a huta da quda”. Suna faxar wannan maganar idan suna so su nuna cewa ya kamata a rabu da abu ko a yar da wani abu wanda ba ya da amfani ga mutum, ko kuma a gama wani abu don a huta.

Ga wani misali daga waqar da Salihu Jankixi ya yi wa Sarkin Musulmi Abubakar na 3, ga gindin waqar:

Gwarzon Galadima xan Shehu,

Gaba da kai ab ba daxi.

Jagora-Xan su ikon ka tsaya ga ruwa,

Daga biki sai ko qwaxxuna,

An san asalin xan mai homa,

Qwaguwa kahwahunta karkace,

Ta hwarma laka sun dame,

Shi tukulu ba mu shiga batun shi ba,

Qusumbi garai mun ga ya zuqe,

Mai bixar ya sawo ya sayar,

Ya iske mutane sun tashi,

Ka ga kunkuru an zama utel.

A nan Mawaqin ya yi habaici inda ya nuna lallai ko wane mutum ya tsaya ga matsayinsa kuma ya tsaya cikin sa'o'insa tun da an san asalinsa. Haka nan ya kwatanta wanda yake yi wa habaicin da qaguwa. Ya siffanta tafiyar shi da irin tafiyar qaguwa kamar yadda Bahaushe ke mata kirari da "qaguwa tafi karkace" saboda yadda take tafiya. Wannan ya nuna Mawaqin ya qasqantar da mutumin ta hanyar kwatanta shi da qaguwa. Bahaushe kan kwatanta mutum da wani qwaro ko wata xabi'a ta sa don ya qasqanta ko ya kuranta shi.

Ga wani misali daga waqar da Jankixi ya yi wa Sardaunan Sakkwato firimiyan jihar Arewa Alhaji Ahmadu Bello.

Gindin waqar:

Allah taimaki mai gaskiya,
Ahmadu Bello irin Shehu na,
Mai ja ma dole ya saki ma.

Jagora-Zamanin jikan Bubakar,

'Yan amshi- Qwarin da ka yawo bisa qasa,

Ko su ma jam'iyya sukai,

Duk dai N.P.C sun ka bi.

Wato saboda gaskiya da riqon amana da qwarjinin Sardauna har qwarin da ke yawo bisa qasa duk Jam'iyyar da yake suke bi. A nan Mawaqin ya mutuntar da qwari domin ya danganta su da yin irin aikin da sai mai hankali ne kaxai zai iya yi. Tun da ya ce su ma qwari suna da Jam'iyyar da suke bi.

Haka nan a waqar da Buda Xantanoma Argungu ya yi wa Sarkin Kabin Argungu Muhammadu Sani an yi amfani da qwaro a matsayin tubalan ginin ta. Ga gindin waqar:

- Gagara qarya sadauki,
  Jagwarzon Alqali.

Jagora: Zanqalolo kama da hwara yayyo,

‘Yan amshi: Bai yi awa hwara ba.

Makaxin ya yi wa wani zambo inda ya kira shi da Zanqalalo, wataqila mutumin tsawo gare shi sosai, shi ya sa ya kira shi Zanqalalo. Sai kuma ya kamanta shi da fara, wai ya yi kama da fara sannan kuma ya qasqanta shi da cewa bai kai fara ba.To a nan dai Mawaqin ya yi wa mutumin kamanci na qasqanci saboda da ma ya qasqanta shi ta hanyar kamanta shi da fara kuma ya qara qasqanta shi ta nuna fara ta fi shi daraja.

Ga wani misali daga waqar da Abubakar Akwai Sabon Birni ya yi wa Sarkin Gobir Umaru Shawai mai suna Fadamar Kanwa. Ga gindin waqar

Gindin waqar: Dum mai sarqafa sai ya dangana Gobirawa,
Fadamar kanwa xakinsa a can ad da girma.
Jagora: dibi mahaukacin qasa mai damqar maciji,
‘Yan amshi: Tava qasa ta sare ka ba a da magani.
Jagora: Xan kurtcattcaki xan kuta mai katce kanu,
‘Yan amshi: Xan bakuje xan quje jinga tai anini.

A waqar mawaqin ya bayyana cewa duk wani mai naci da sarkafa daga cikin Gobirawa wanda ke son ya ja da sarki ya dangana domin al’amarin ya fi qarfinsa, ya kwatanta abokin hamayyar sarki da mahaukaci da quje (quda). Mawaqin ya qasqantar da shi ta hanyar kiran shi xan quda domin kowa gudun quda yake saboda halayyarsa.

Ga wani misali daga waqar da Abdu Kurna Maradun ya yi wa jikan Hassan xan Iro.Ga gindin waqar:

Jikan Hassan xan Iro,

Sarkin qaya mai gayya,
Na Magaji ba togewa,
Shi yay yi damben girma.
Jagora Tuji yana son hwara,
'Yan amshi: Amma ganin qwanjin xan kare
Ya hana mai qoshi.
Jagora: Xan sarkin ga mai qwaxai da yawa ,
'Yan amshi: Ci burqunquma ci buzuzu,
Ya tsare ni yana vaci,
Ban ga nai mashi laihi ba.

A waqar marigayi Abdu Kurna ya kira wanda abokin hamayyar sarki tuji, sannan ya nuna lallai xan sarkin ya cika kwaxayi kuma komi ya biyo hannunsa, sai ya cinye shi. Mawaqin ya yi amfani da karin maganar Hausawa da suke cewa "A ci burqunquma a ci buzuzu". Idan suna son su nuna mutum mai handama da babakere ne wato kome ya zo hannunsa to ya halaka. Da burqunquma da buzuzu duk 'yan qananan qwari ne.

Waqar da Alhaji Muhammdu Xanbunguxu ya yi wa Sarkin Musulmi Alhaji Muhammadu.

Gindin waqa: Xangalin maza jikan shehu sarkin kudu,
Ka haxe maza sun muzanta duk sun saki.
Jagora: Qazunzumi da sabro,

Sharri suke taqama,

'Yan amshi Mu ko akwai hwarin shaltos,
Mun bixa mun aje.
Jagora Aibin baqin maciji
Tahiya cikin duhu
Ba shi hita da rana
'Yan amshi don illa garai ya sani.

Makaxa Alhaji Muhammadu Xanbunguxu ya yi wa wasu habaici ta hanyar kiransu qazunzumi da sauro. A nan ya qasqanta su domin qazunzumi da

sauro duk qwari ne masu halayyar cuta. Sai ya ci gaba da cewa amma sun tanadi shaltos abin da za su yi maganinsu da shi. Shaltos wani magani ne wanda ake amfani da shi don a kashe qwari. A nan mawaqin na nufin sun riga sun tanadi abin da za su yi maganin waxannan abokan hamayyar Sarkin.

Wani misali daga waqar da makaxa Abu xan kurma ya yi wa Mai Kano Sabon Garin Mayanci. Ga gindin waqar:

Gindin waqa: Mai halin mazan jiya,
Xan Abdu jikan Muhamman,
Xan Marafa mai Kano,
Kai ad da halin Abarshi.
Jagora: Ji man kunkuru ana son ai dambe
'Yan amshi: Hannuwa sun gaza sai a sake dubara,
Jagora: Qaqa gara ta kan yi da dutsi,
Sai ta yi lasa.
Don babu riba gare ta.

Makaxa Abu xan kurma ya kwatanta waxanda ke hamayya da Maikano da gara, Sarkin na shi kuma ya kwatanta shi da dutse. Domin kowa ya san dutse ya fi qarfin gara sai dai katako. A taqaice dai mawaqin ya nuna cewa Maikano ya fi qarfin waxannan mutane domin ba su da yadda za su yi da shi ya riga ya sha gabansu.

Misalin wata waqa wadda aka yi amfani da qwari wajen gina ta ita ce waqar da Babangida Kakadawa ya yi ta gidan haya. Gindin waqar shi ne:

Gidan nan ba gida ba ne
Matsala dai ne gidan haya.
Jagora: Tun farkon asalatun,
Duk tsuntsun da yake sama,
Ya gina gida nai ya shige,
Qwarin da su ke tudu,
Kowane ya yi gidanai ya shige.
Qwarin da suke ruwa,
Har da qwarin da suke tudu,
Kowanne ya yi gida nasa ya shige,
Misali tun ga zanzaro,
Ga shi abi ne xan qarami,

Ya je daji ya ja qasa,
Ya xebo ruwa nana ya haxa
Ya gina gidansa yana shiga…….

Makaxa Babangida Kakadawa ya jawo hankalin mutane da su guji zaman gidan haya. Ya nuna masu hatta qwari waxanda mutane sun fi su hankali nesa ba kusa ba sun san su gina gida su shige don su sami kwanciyar hankali. To kai ga ka xan'adam ya za ka tsaya a gidan haya. A waqar ya kawo rabe-raben qwari wato na tudu da na ruwa inda ya nuna kowanensu na yin muhallinsa don ya shiga. Ya kawo misalin yadda zanzaro ke gina gidansa ya shige. Mawaqin ya nuna muhimmancin muhalli saboda, haka ya ja hankalin mutane su yi qoqari su guji zaman gidan haya.

Wani misali daga waqar da Alhaji DR. Mamman Shata Katsina ya yi wa Alhaji Sani Audi Jami'in kwastan.

Gindin waqa: Mai daga magajin mamman,
Sani Audi mai ban tsoro.
Jagora: Wata murna wurin katsinawa,
An ce sani na hanyar nan,
Sai murna suke sai dole,
Wai na gida yana hanyar nan,
Sun ji qanensu na hanyar nan,
Kuma wansu na hanyar nan,
Ga kuma xansu na hanyar nan.
Cinnaka bai san na gida ba
Has shata yana dubawa.
'Yan amshi: mai daga magajin mamman,
Sani Audi mai ban tsoro.

A waqar Alhaji Mamman Shata ya kwatanta halayyar Sani Audi da halayyar cinnaka. A nan mawaqin ya nuna cewa Sani Audi ma'aikaci ne mai gaskiya da riqon amana tun da idan ya tashi aiki ba ruwansa da son kai tun da bai bari a yi abin da bai dace ba. Mawaqin ya yi amfani da kirarin da Hausawa suke wa cinnaka "bai san na gida ba".

5.5. Qwari a Wasu Al'adun Hausawa.

5.5.1. Ma'anar Al'ada.

Kalmar al'ada kalmace Balarabiya wadda Hausawa suka aro kuma suka Hausance, suka sa mata ma'anar da ta dace. A luggar Larabci al'ada na nufin wani abu da aka saba da yi ko ya saba wakana ko aka riga aka san da shi.

Al'ada na nufin dukkan rayuwar xan'adam tun daga haihuwa har zuwa mutuwa. A ko ina mutum ya sami kansa tun farkon rayuwarsa, duk wata xabi'ar da ya tashi da ita ko ya tarar a wurin da ya rayu ko yake rayuwa ita ce al'adarsa. Babu wata al'umma da za ta rayu a doron qasa face tana da al'adar da take bi kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata da ba ita ba. A ra'ayin Sallau (2008) ya bayyana cewa:-

> *Al'ada ita ce duk abin da mutum ya tashi ya ga al'ummarsa na aikatawa.Kuma shi ma ya ginu a kan sa yana mai gamsuwa da abin tare da qoqarin havaka shi. Al'ada wata riga ce da kowane rukunin mutane masu aqidu da yanayi suke da ita, wadda take zamarmasu tamkar tsani na giuwar al'ummarsu ko kuma fitila ta haskaka wannan al'umma*. (Sallau, 2008:2).

A ra'ayin Bunza (2006):-

> *Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar xan'adam tun daga haihuwarsa har zuwa kabarinsa. A*

ko'ina mutum ya sami kansa duk wata xabi'a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu, ko yake rayuwa. Ita ce al'adarsa da za a yi masa hukunci a kai. Babu wata al'umma da za ta rayu a doron qasa face tana da al'adar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata da ba ita ba. (Bunza, 2006:xxxii)

5.6. Tasirin Qwari a Camfin Hausawa.

Camfi wata daxaxxiyar al'ada ce ta Hausawa. Masana da manazarta Hausa sukan yi wa camfi kallo iri biyu. Wasu na ganin camfi al'ada ce kawai kamar kowace al'ada, amma wasu na ganin abin ya wuce haka, ya kai matsayin addini daga cikin addinin gargajiyar Bahaushe.

A fahimtar wasu masana, misali Yahaya (1992) ya bayyana camfi da:-

Wata hanya ta qudurce aukuwa ko faruwar wani abu da sakamakonsa zai iya zama mai kyau ko mai alheri ko mai muni. Ya danganci yarda ko amincewa da ke xarsuwa a zuciya bisa wata manufa da aka qago (Yahaya, 1992:18).

A ra'ayin Umar (1977) kuwa

Camfi wani qagaggen bayani ne a kan wani abu da za a yi ko kuma zai faru da ya qunshi sakamakon aikin, ko abin in ya faru (Umar, 1977:2).

A taqaice, camfi a qasar Hausa kamar yadda Bunza (2006) ya nuna shi ne:-

Wani abu da aka gada daga magabata bisa gai irin kallon da suke yi wa wasu abubuwan duniyar mutane ta fuskar amfaninsu da illolinsu. Magabatan sun xora wannan fahimtar tasu a kan tabbatattun hujjojin da suka bayyana gare su suka shaide su ko da ido, ko aka labarta masu da baki kuma suka ga gaskiyar abin ga irin rayuwar da suke ciki. A zuci sun gaskata shi, a aikace ko ta sigar lafazi sun kiyaye shi. Kuma sukan xauki kowane irin mataki na ganin ba su ci karo da hane-hanensa ba, kamar yadda suke xaukar matakan ganin sun yi canjaras da umurce-umurcensa (Bunza, 2006: 60).

Dangantakar da ke tsakanin Bahaushe da wasu halittu na qasar Hausa, ta sa shi ya nazarci yanayi da halayyarsu sosai saboda zaman tare. Wannan ya ba shi damar gina wasu camfe-camfe da suka shafi waxannan halittu gwargwadon abin da ya hanga. Daga cikin waxannan camfe-camfe akwai masu dama waxanda suka shafi qwari, misali:-

1. Ba a kashi ko fitsari a gindin shuri.

Shuri gida ne da wasu nau'o'in qwari ke ginawa da qasa, Bahaushe ya camfa shi cewa iskoki na zama wurin, to ina ganin wannan dalilin ne ya sa suka camfa shi don nuna horo da hani da tsoratarwa, don an nuna idan mutum ya kuskura ya aikata abin da aka hana shi a wurin, akwai abin da zai same shi.

2. Barin kwarkwata a qasa na sa girgizar qasa.

Wannan camfi na da alaqa da koya tsafta kuma yana jawo hankalin Bahaushe ne ga kada ya sake ya yi qazantar da zai bari kwarkwata ta cika masa jiki har ta dinga zuba qasa, idan kuma har ya bari, to za a yi girgizar qasa wadda kowa ba zai so a yi hakan ba don ya san abin da za ta haifar.

3. Duk mai sarar kashe tururuwa babu dalili zai ci karo da matsala a rayuwarsa.

Game da wannan camfin ina ganin qila dai Bahaushe ya gwada ya gani domin ko akwai labarai masu yawa waxanda ke nuna mutum ya kashe ko share gidan tururuwa ya haukace, ko kuma ya gamu da wani ciwo mai wuyar magani. Misali akwai wata mata da ta gamu da ciwom tavin hankali a sanadiyyar share gidan tururuwa da ta yi bayan an sa magani. Ina ganin wannan camfin ba ya rasa nasaba da yardar da Bahaushe ya yi cewa aljannu na zama a gidan tururuwa

4. Cin naman gyare na sa zaqin murya.

Wannan camfin bai rasa nasaba da murya da gyare yake da ita don kuwa yana da murya mai zaqi da qarfi, domin a baya an ambata cewa Bahaushe na amfani da gyare wajen haxà maganin zaqin murya.

5. Taka ko yin fitsari a bisa gidan tururuwa na sa a haukace.

Wannan camfin ba ya rasa nasaba da yadda Bahaushe ke alaqanta tururuwa da gidanta da qwanqwamai. Saboda haka ake tsoratar da mutane da umurtarsu da su guji yin alaqa da tururuwa da gidanta.

6. Hausawa sun camfa qwalqwasa da cewa tana korar duk wani azzalumi.

Wannan ya nuna ke n an duk inda aka ga qwalqwasa azzalumin qwaro ba ya iya zama saboda haka ne suke mata kirari da ‘qwalqwasa fid da mai gida daga gidansa’.

7. Idan aka zubar da vawon gyaxa ko ina a gida za a jawo kunama.

Camfin ba ya rasa nasaba da qoqarin Hausawa wajen koyar wa yaransu tsafta. Don haka sai aka alaqanta abin da kunama, don a tsoratar da su cewa idan suka zubar da vawon gyaxa ko’ina kunama za ta zo.

8. Ba a faxar sunan kunama tsirara. Idan aka faxa ana iya cin karo da ita nan take ta cuci mutum. Saboda haka ne Bahaushe ba ya faxar sunanta sai dai ya saya da wasu sunayen domin yin hakan na iya zama kariya ga cutarta. Misali maimakon a ce kunama sai a kira ta da “mai qari”.

5.7. Qwari a Ququwar Hausawa.

Ququwa kamar yadda Bunza (2006) ya bayyana ita ce:-

> *Buwayar abu ta ba a iya a cuta masa, balle a ce*
> *sai bayan an yi cutar a ga sakamakon qohi.*
> *Ququwa buwaya ce ta kowace irin fuska.*
> *Mai ququwa ba a ma kai ga jikinsa bale a cuta masa.*
> *Ko da an yi niyyar a cuta masa da asiri da sihiri ko*
> *tsafi ya riga ya shirya yadda zai fuskanci duk abokin*
> *gaba yadda ba a cin nasara gare shi*. (Bunza, 2006: 217).

A ganin Bahaushe ququwa tana da alaqa da iskoki don da su ake amfani a nuna ququwa ko ququwa ta bayyana.

Qwarin da ke da ququwa sun haxa da Tururuwa da kunama. Ququwar da Tururuwa ke yi ita ce kome daven da aka yi aka gina gida a kan ta sai ta sake bayyana ko bayan an shiga gidan. Ko kuma idan aka sa mata magani, wuta za ta tashi ko dai ta qona mai sa maganin, ko ya haukace ko kuma ya mutu. Kunama kuwa ququwarta ita ce idan ta yi harbi aka kashe ta sannan aka qona ta da wuta dafinta zai dinga yawo a jikin wanda ta harba ya yi ta ihu kamar shi ake qonawa.

5.8. Naxewa da Sakamakon Bincike.

A taqaice, qwari sun yi tasiri qwarai da gaske a rayuwar Hausawa. Bahaushe na da alaqa da qwari shi ya sa ya fahimce yadda suke ta fuskar halaye da dabaru kuma ya san siffofinsu. Saboda qarfin tasirin ne Hausawa ke yin amfani da sunayensu kai tsaye, qirar jikinsu ko wata halayya tasu cikin vangarorin adabinsa na gargajiya. Misali ana amfani da su cikin labarai waxanda ake qirqirawa a dangantasu gare su domin nuni da ilmantar da jama'a a cikin gudanar da rayuwarsu ta yau da kullum. A labarai ana kawo hoton abubuwan da ake bayar da labarinsu ta yadda mai sauraro zai iya kallon abun da idanunsa na zuciya ya riqa ganin kamar ga abin nan yana faruwa a gabansa.

Tasirin ya yi nisa qwarai da gaske wadda har ta sa Bahaushe ke amfani da yadda qirar jikin qwaro ta ke ya shiryar da ita cikin vangarorin hikima don a qwarzanta wani ta hanyar siffanta qirar jikinsa ko halayyarsa da wani qwaro mai kyau ko kuma don a wulaqanta siffar jikinsa ko halayyarsa da wani mummuna ko macucin qwaro. Idan muka dubi nason da qwari suka yi a tatsuniyoyi, za mu ga cewa da ma can tatsuniya ta kasance makarantar farko ga yaran Hausawa inda ake koya masu darussa waxanda za su yi amfani gare su, misali suna amfani da tatsuniya don jawo hankalin yaransu zuwa ga aikata ayyuka masu kyau da yadda za su guji aikata munanan ayyuka. A

tatsuniyoyin Hausawa akan qaga labarai a kan qwari a ba su matsayi irin na mutane, a ce suna magana ko aikata wani aiki wanda sai mutane kaxai za su iya aikatawa. Haka kuma ana amfani da qwari a koya wa yara wayo da dabara da illar qarya da cuta da baqin ciki da kuma kyawon aikata gaskiya da abin kirki da riqe amana.

Idan muka koma kan hikaya, akwai wasu waxanda qwari ne tubalan gininsu kuma wuraren da aka yi amfani da su da rawar da suka taka cikin hikayoyin suna dacewa da irin halayyarsu ta zahiri, yawanci ana amfani da qwarin domin isar da isharori ga jama'a domin su kyautata halayyar rayuwarsu ta duniya da lahira.

Qwari sun yi tasiri qwarai a karin maganar Hausawa domin kuwa akwai karin maganganu waxanda aka yi amfani da qwari wajen tsara su, kuma yawancinsu idan aka yi nazarí ko sharhi za a tarar an duba halayya ko siffar qwarin ne aka gina su. A taqaice dai hakan ba zai rasa nasaba da irin tasirin suka yi ba ga al'umma. Haka nan kuma an yi amfani da qwari daban-dabam wajen gina karin maganganun misali rina da kiyashi da fara da shinge da kunama da sauransu.

A vangaren kirari kuwa, qwari sun yi tasiri sosai saboda Hausawa sun yi wa masu yawa daga cikinsu kirari. Amma kirarin ba wai qwarin ake kurantawaba, mutane ake ya mawa. Kalmomin da ke cikin kirarin na nuna siffofi ko halayyar qwari sai a qwatanta su da wani. A taqaice dai duk waxannan alaqa da aka samu tsakanin Hausawa da qwari ta samu ne saboda zaman wuri xaya.

Idan muka xauki camfi wanda daxaxxiyar al'ada ce ta Hausawa, saboda halayyar zamantakewa akwai camfe-camfe masu yawa da

Bahaushe ya yi amfani da qwari wajen gina su. Yawancin su suna horo ne da hani da tsoratarwa da nuna wa mutane kada su kuskura su aikata abin da aka hana su. Idan kuma suka aikata to akwai abin da zai same su.

Adabin baka na Hausa ya daxe a bisa qasa don shi ne adabin da Hausawa suka gada daga kaka da kakanni, kuma adabi ne da ke qunshe cikin rayuwar yau da kullum. Wannan aiki ya kalli nau'o'in qwari daban-dabam waxanda ke rayuwa a qasar Hausa da tasirin da suka yi ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa. An duba yadda yanayin zamantakewa ya sa aka sami alaqa mai qarfi tsakani. Wannan ya sa qwarin suka yi tasiri cikin al'amuran Hausawa har suke amfani da sunayensu ko siffofinsu ko halayyarsu cikin kyakkyawan azanci don su bayyana al'amuran rayuwarsu.

Mutane da dama sun xauka cewa qwari ba su da wani amfani, sai dai cutarwa ga mutane da dabbobi da amfanin gona. Wannan ya sa ba a cika mayar da hankali a kansu ba, ballantana har a binciko baiwar da ke tattare da su. Amma kuma ina ganin dangantakar da ke tsakanin Bahaushe da qwari ita ta sa Bahaushe ya lura da irin yanayin rayuwar qwari har ya fahimce su. Wannan dalili ne ya ba shi damar sarrafa halayya da siffa ta qwarin cikin kyakkyawan azanci da ban sha'awa don qara fito da adabinsa da al'adunsa na gargajiya.

Wannan haske da aka samu shi zai qara bayyana wa mutane cewa lallai akwai alaqa tsakanin Bahaushe da qwari. A qoqarin bayyana hakan wannan binciken ya kawo abubuwa waxanda suka danganci qwari. Misali nau'o'insu, yadda su ke yaxuwa, yadda suke renon 'ya'yansu da abincinsu da yadda suke zamantakewa tsakaninsu da amfaninsu da illolinsu da sauransu. Binciken ya duba tasirin qwari ga adabin baka da wasu al'adun Hausawa na gargajiya. Ta hanyar duba yadda yanayin zama ya sa aka sami alaqa kuma wannan ya sa qwarin suka yi tasiri a al'amuran Hausawa. Akwai magunguna na gargajiya waxanda ake amfani da qwari wajen haxa su. Misali ana amfani da su a haxa kafi a gidaje ko ganaki, kuma sun kasance matsayin abinci da sauransu.Saboda

haka ina kira ga mutane da su riqa tausayawa da nuna jin qai ga qwari. A guji cutarsu ko kashe su idan ba da wani qwaqqwaran dalili ba.

5.9. Matsaloli da Shawarwari.

Kowane bincike aka gudanar ba yadda za a ce an kammala shi ba tare da samun wasu ‘yan matsaloli ba. A qoqarin gudanar da wannan bincike an fuskanci matsaloli da dama daga cikinsu akwai ta neman bayanan da suka shafi qwari, don su qananan halittu ne da mutane ba su cika kulawa da su ba saboda haka sai bayanai game da su ya yi qaranci sosai. Wani ma idan aka tambaye shi sai ya ce bai san komai game da qwari ba. Haka kuma sanin sunayen qwarin da samun haqiqanin siffofinsu daga waxanda aka yi hira da su ita ma wata matsala ce da aka fuskanta a lokacin gudanar da aikin.

Samun misalai a kan vangarorin adabin baka da al’adu waxanda suka shafi qwari ma sun wahalar saboda sai mutum ya kawo misalai guda ashirin ba tare da an sami xaya wanda ya danganci qwari ba.

Daga qarshe ina son in jawo hankalin manazarta da ba su qarfin guiwa cewa su yawaita yin bincike a fannin da ya shafi qwari don aikin da aka gudanar a fannin ya yi qaranci, sannan kuma duk wanda ya binciki fannin zai gane cewa halittu ne waxanda ke da tsarin rayuwa na musamman mai ban mamaki da

al'ajabi. Ina fatan wannan aikin za ya amfanar da duk wanda ya karanta shi kuma zai zama jagora ga masu sha'awar zurfafa bincike a kan wannan fanni.

MANAZARTA.

Adamu, M.T. (1997) *Asalin Hausawa da Harshensu*, Kano: Xan Sarkin Kura Publishers.

Alhassan, H. da Wasu. (1982) *Zaman Hausawa*, Lagos: Islamic Publications Bureau.

Bamalli, N. (2007) *Bala da Babiya 'Lafiya Uwar Jiki'*. Zariya: N.N.P.C.

Bargery, G.P. (1934) *A Hausa-English Dictionary and English Hausa Vocabulary*. Zaria: Ahmadu Bello University Press, Limited.

Birnin Tudu, S.Y. (2002) "Jigo da Salon Rubutattun Waqoqin Furu'a na Qarni na Ashirin", Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Boorman, J. (1981) *The West African Insects*, Hong Kong: C &C Joint printing Company.

Buniya, Y. (1971/72) "The Phenomena of Kirari in Hausa Society", B.A. Dissertation. Kano: A.B.C/A.B.U.

Bunza, A.M. (1990) "Hayaqi Fid da na Kogo: Nazarin Siddabaru da Sihirin Hausawa", Kundin Digiri na Biyu a Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Bunza, A. M. (2006) *Gadon Fexe al'ada* Lagos: Tiwal Nigeria Limited No.16 Akinbaruwa Street.

Bunza, A. M. (1999) "Raxaxi da Zogin Cuta a Ma'aunin Bahaushe "tsokaci Cikin waqar kunama ta Garba Maitandu'' in *Readings in Hausa Studies Language, Literature and Culture*. Sokoto: Usman Xanfodiyo University.

Bukar, U. (2005) *Taskar Tatsuniyoyi*, Littafi na 1-6: Kano, Gidan Dabino Publishers, Nigeria.

Vavura, H.S. (2008), "Ceto Gizo daga Gizo-Gizon Al'adun Duniya", 2nd International Confrence on Hausa Studies: African and European Perspectives, Italy: Universita Degli Studi Di Napoli Orientale.

CSNL (2003), *Sababbin Kalmomi: Ingilishi zuwa Hausa.* Littafi na xaya, Cibiyar Nazarin Harsunan Nigeria, Kano: Jami'ar Bayero.

CSNL (2006), *Qamusun Hausa*, Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero.A.B.U Press.

Daba, H.A. (1997)." Linguistic Taboos and Animal Categories as verbal Abuse Or Compliment in Hausa" cikin *Harsunan Nijeriya* vol.xviii Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya Kano: Jami'ar Bayero.

Xangambo, A. (1986), "Tarihin Ginuwar Rubutattun Waqoqin Hausa da Havakarsu" Takardar day a gabatar a Bikin Makon Hausa na 14, Kano: Jami'ar Bayero.

Xangambo, A. (2008), *Rabe-Raben Adabin Hausa* (Sabon tsari) Kano: Amana Publishers Limited.

Xanyaya, B.M. (2007) *Karin Maganar Hausawa*, Sokoto: Makarantar Hausa.

Dogara, l.A (1992) “Namun Daji a Qasar Hausa: Ire-Irensu da Magungunan da Ake Samu Daga Gare Su”.Kundin Digiri na xaya Kano: Jami’ar Bayero.

East, R.M. da Imam, A. (1949) *Ikon Allah*, Littafi na 3 &4 Zariya: N.N.P.C.

Encarter Premium (2007), D.V.D. Soft Ware.

Encyclopedia Britannica (1998), Chicago:H.I. J. Standard Educational Corporation.Volume Seven.

Gora, Y.C. (1989), “Camfi a Al’ummar Hausawa”, Kundin Digiri naBiyu (M.A Hausa) Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Kano: Jami’ar Bayero.

Gusau, S.M. (1996), *Makaxa da Mawaqan Hausa*, Kano: Usman Al-Amin Publishing Company.

Gusau, S.M. (2008), *Waqoqin Baka a Qasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2008), *Dabarun Nazarin Adabin Hausa*, Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2009), *Diwanin Waqoqin Baka. Zavavvun matanoni na waqoqin Baka na Hausa* Kano: Century Research and Publishing Limited.

Hadiza Salisu Koko. (2009), *Jagoran Nazarin Tatsuniya*, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Sakkwato: Kwalejin Ilimi ta Shehu Shagari.

Hassan, M. M. (1995), “Ire-iren Qwari da Muhimmancinsu ga Rayuwar Al’umma”, Kundin Digiri na Xaya (B.A Hausa) Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Kano: Jami’ar Bayero.

Ibrahim, M.S. (ba shekarar wallafa), “Adabin Gargajiya na Hausa Kafin da Kuma Bayan Musulunci”, Sashen Harsunan Nijeriya Kano: Jami’ar Bayero.

Ibrahim, M.S. (1982) “Dangantakar Al’ada da Addini: Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa na Gargajiya”, Kundin Digiri na Biyu (M.A. Hausa),

Sashen koyar da Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Imam, A. (1944), *Qaramin Sani Ququmi ne*. Littafi na 4. N. N.P.C.

Isa, S. (2009) "Evaluation of Antimicrobial Synergistic Effects of Black Cumin (Nigella Sativa) Seed Extracts and Honey on some Clinical Bacterial Isolates". M. Sc Microbiology, Kano: Bayero University.

Kano, A. (1979), *Hikayoyin Kaifafa Zukata*, C.S.N.L, Kano: Jami'ar Bayero, Thomas Nelson Nigeria Limited.

Qaraye, M. (1978) "Beyond the Illusive Cobwebs of the Spider", In Studies in Hausa Language, Literature and Culture. Centre for the Study of Nigerian Languages, Kano:Bayero University.

Kotpal, R.L. (2005). *Modern Text Book of Zoology*: Invertebrates, India: Shivaji Road.

Madauci, da Wasu. (1968) *Hausa Customs*, Zariya: N.N.P.C

Mahe, A. (2008), "Duniyar Dabbobi a Cikin A1'adun Hausawa", Kundin Digiri na Biyu (M.A Hausa), Kano: Jami'ar Bayero.

Muazu, A.H. (2009), "Gurbin Dabbobi da Qwari a cikin Waqoqin Baka na Hausa" Takardar share fage domin ci gaba da rubuta kundin digirin M.A Hausa Sokoto: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Muhammad, H. da Wasu. (2004) Kirari a Qasar Hausa, Kundin Shaidar Diploma Katsina: Hassan Usman Polytechnic.

Muhammad, Y.M. (2003), *Adabin Hausa*. Zariya: Ahmadu Bello University Press.

Ndu, F. da Wasu. (2001) *Round up Biology for West African Senior School Certificate Examination*. A Complete Guide.

Obidikwe, J.B.C. (2000.). *Biology for the Certificate Year*.

Sakina Adamu Ahmad (2011) "Gurbin Qwari a Magungunan Gargajiya na Hausawa", Kundin Digiri na Biyu (M.A Hausa), Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Sallau, B.A.S. (2000). "Wanzanci: Matsayinsa na Al'ada da Sana'a a Qasar Hausa, Kundin Digiri na Biyu (M.A Hausa), Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero.

Sallau, B. A. S. (2008). Tasirin al'adu a cikin Kasuwanci da Zamantakewar Hausawa ta Jiya da Yau, Takardar qara wa juna sani. Katsina: Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua.

Sharifai, B.I. (1990)." Take da Kirarin Sana'o'in Gargajiya, Ma'anarsu da Muhimmancinsu ga Rayuwar Hausawa'' Kundin Digiri na Biyu (M.A Hausa), Kano: Jami'ar Bayero.

Tudun- Wada, Y.Y. (1981) "Tsari da Ma'anar Karin Maganar Hausa" Takardar Da ya gabatar a Taron Qara wa Juna Ilimi. Kano: Jami'ar Bayero.

The New Standard Encyclopedia (1980) Volume Seven, Chicago: Standard Educational Corporation.

Stone, R.H. da Wasu. (1985) *The New Biology For Senior Secondary Schools* Hongkong: Longman Group.

Umar, M.B. (1982) *Waqoqi don Yara.* Zariya: N.N.P.C.

Umar, M.B. (1977) *Camfe- camfen Hausawa 360* Kano: Shonuga Commercial Press.

Umar, M.B. (l982) *Dangantakar Adabin Baka da Al'adun Hausawa na Gargajiya* Kano: Shonuga Commercial Press.

Usman, B. (2005) *Taskar Tatsuniyoyi*. Kano: .Gidan Dabino Publishers, Jakara.

Vines and Rees. (1971) *Plant and Animal Biology*. Ibadan University Press.

Yahya, I.Y. da Wasu (1978) *Darussan Hausa don Manyan Makarantun Sakandare* Littafi na xaya Ibadan University Press.

Yahya, I.Y. (1971).*Tatsuniyoyi da Wasanni*, Littafi na1 Ibadan University Press.

Yahya, I.Y. (1974) *Labarun Gargajiya,* Littafi na 1 University Press P.L.C.

Yunusa, Y. (1977) *Hausa a Dunqule* Zariya: N.N.P.C.

Yeodeowei, A. (1975) *Our Common Insects*, Ibadan University Press.

Zarruk, R.M (1986) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa don Kananan Makarantun Sakandare*, Ibadan University Press.

Waxanda Aka Yi Hira Da Su.

Malam Ado a garin Ajiwa a ranar 24-04-2013.

Malama Binta Kanti Kankiya a ranar 13-02-2013.

Malam Garba a kasuwar Tashar Mangwaro a ranar 06-02-2013.

Malama Hassatu a unguwar Qofar Qaura Katsina ranar 04-04-2014.

Malam Lawal Rimaye a garin Rimaye a ranar 03-07-2013

Malam Muhammadu Tukur a garin Vatagarawa a ranar 05-02-2014

Malam Nata'ala a F.C.E. Katsina a ranar 04-03-2013.

Mr. Okeke a F.C.E. Katsina a ranar 04-04-2014.

Hajiya Rabi Liadi a ranar 12-05-2014.

Malam Yakubu Safana a garin Safana a ranar 07-03-2014.

Malama Umma Nura a unguwar Sabuwar unguwa Katsina a ranar 13-4-2014.

Hajiya Aisha a qofar Kabuga Kano a ranar 16-09-2015.

1. RATAYEN WASU TATSUNIYOYI.

TATSUNIYAR ZARUMI.

Gata gatanan ku.

An yi wani mahaukaci wanda ake kira Zarumi. Shi wannan mahaukaci ba ya bugu kuma ba ya zagi. Shi dai kawai yana tsince-tsincensa a bola kodayaushe. Zarumi yana da suma mai yawa kuma duk ta mummurxe saboda dauxa, a cikin wannan sumar akwai kwarkwata da yawa, idan yana kwance kwarkwata xaya ta faxo sai ya xauka ya mayar da ita cikin sumarsa.

Wata rana yana kwance cikin bola sai ya ga wani wake ja mai kyau, sai ya xauka ya je gida ya shuka. Kullum idan zai fita sai ya ba wannan wake ruwa. Ana nan ana nan har wake ya girma ya yi ‘ya’ya sosai. Shi ke nan, rannan da safe bayan Zarumi ya gama ba wake ruwa sai ya ce “oh ni Zarumi ga shi zan fita neman abinci amma ban san wanda zan bari tsaron wakena ba, don kada in tafi a shigo a yi mani varnar wake ga shi ya qosa sosai”. Sai ya yi shiru yana tunani, can daga cikin sumarsa sai ya ji ana cewa “ni zan tsare maka gidan”. Ko da Zarumi ya duba sai ya ga ashe kwarkwatar da ke kanshi ce ke magana. Sai

Zarumi ya ciro ta daga sumarsa ya ce “to na ba ki amanar gidana.” Sai kwarkwata ta ce, “Allah ya dawo da kai lafiya”.

Bayan Zarumi ya wuce sai gizo ya zo bara gidan Zarumi, da ya yi bara bai ji an amsa ba sai ya ce, bari in qara shiga ko a ji ni. Ko da gizo ya shigo sai ya ga babu kowa a gidan kuma ga wake an shuka ya yi kyau sosai, sai gizo ya ce tun da ba kowa a gidan kuma ga wake an shuka ya yi kyau sosai bari in xan xibi waken nan in je gida in dafa jimviri. Ko da gizo ya tava wake sai ya ji ana waqa:-

“Ku ku kar ku tava,

Waken Zarumi ne,

Shi ya bar ni tsaro,

Ya ce kar a tava,

Kukunjarmana,

Kataka jarmana,

Titi zunqui zunqui”.

Sai ya tsaya bai ga kowa ba ya kuma qara tavawa ya ji an yi waqa kuma bai ga kowa ba, sai ya fara rawa. Yana ta rawa bai ankara ba har marece ya yi. Ko da gizo ya ga marece ya yi sai ya sheqa sai gidan sarki ya faxi ya yi gaisuwa ya faxa wa sarki cewa ya je wani gida bara ya ga wake mai kyau ya sa hannu zai xiba sai ya ji waken na waqa mai daxi, ya kamata sarki ya je ya ga wannan wake mai waqa.

Da sarki ya ji wannan bayani sai ya aika fadawansa su je su xebo masa wannan wake, ko da fadawan sarki suka sa hannu su xebo wake sai suka ji ana waqa mai daxi sai suka kama rawa har rana ta faxi. Ko da sarki ya ga basu dawo ba sai ranshi ya vaci ya hau doki da kansa domin ya je ya ga abin da suke yi.

Da isarsa ya hasala ya kama yi musu faxa, ya sauko ya sa hannu zai xebi wake sai wake ya kama waqa, sai sarki ya kama rawa tare da fadawansa da gizo har Zarumi ya dawo daga wajen tsince-tsincensa, ko da ya dawo sai ya iske gida ya cika da mutane har da sarki. Sai ya tambayi dalili aka gaya masacewa wakensa ke waqa mai daxi, sai Zarumi ya ce ba wake ba ne kwarkwata ce sai sarki ya ce yana so ya sayi kwarkwatar. Ya ba Zarumi bawa goma da dinari dubu don a ba shi kwarkwatar, sai Zarumi ya xauko kwarkwata ya ba sarki ya ce masa abincinta shi ne man shanu. Sarki ya yi godiya ya koma gida ya sa kwarkwata a cikin kwalbar zinari da auduga da man shanu ya rufe ya rataye a kan gadonsa. Duk lokacin da ransa ya vaci sai ya zo ya tava kwalbar sai kwarkwata ta fara yi masa waqa har sai ransa ya yi fari.

Rannan sarki ya je yaqi aka kashe masa xa, kuma aka ci shi yaqi. Sarki ya dawo ransa a vace, ya shigo gida bai ce wa kowa kome ba. Sai ya wuce turakarsa ya xauko kwalbar kwarkwata ya tava amma bai ji ta yi waqa ba sai ransa ya qara vaci ya fito tsakar gida ya tambaya, “lokacin da ba na nan wa ya shiga xakinnan?’ sai amaryarsa wadda yake ji da ita ta ce” ni ce na shiga kuma na ga kwarkwata a cikin kwalbar zinare shi ne na kashe ta gudun kada wata rana in zo kwaciya a xakin in kwashe ta”. Ko da sarki ya ji haka sai ransa ya qara vaci ya hasala sai ya saki amaryarsa kuma ya ce mata ta kwashe kayanta ta bar masa garinsa. Qungurus kan kusu.

A wannan tatsuniyar an fito da kyawon riqe amana da cika alqawari. Kwarkwata ta yi alqawarin tsare waken zarumi kuma ta cika alqawarin don ko har zarumi ya dawo gida ya iske wakensa ba wanda ya tava duk da gidan ya cika maqil da mutane masu son xibar waken. Zarumi ya kyautata wa kwarkwata ta hanyar sayar da ita a hannun qwarai inda za ta ji daxi, saboda maimakon ta koma bisa kansa ta ci gaba da cin dauxa sai ya ce man shanu take ci don ya kyautata abincinta, kuma aka saka ta cikin kwalbar zinare tana hutawa.

TATSUNIYAR MUGUN BAFADE.

Gata nan gatanan ku.

A wani gari wai shi Katano an yi wani Sarki daWazirinsa. Wannan Wazirin Bafillace ne kuma maqetaci, a kusa da fadar Sarki akwai wani gida na wani attajiri a bayan gidan attajirin akwai wata qatuwar itaciyar kuka wadda ke da kogo. A cikin kogon akwai tururuwa da maciji da shamuwa da aljani da shaho. Kullum da safe sai attajirin ya je su gaisa da waxannan abubuwa kuma ya ba su abinci.

Waxannan qwarin sun nemi attajirin da su riqa yi masa bauta amma ya ce “a’a”. Ana nan ana nan sai wata rana Wazirin Sarki ya kai sukar attajiri ga Sarki kuma ya rinqa qulla masa makirci kala-kala. Rannan sai Waziri ya ce wa sarki ya kamata a nuna wa attajirin nan cewa shi ba kowa ba ne. Sai ya qulla cewa a harhaxe buhuhuwan gero da dawa da masara da wake waje xaya a ce wa attajirin nan ya rarrabe su kafin safe. Sarki ya sa aka aiwatar da haka kuma aka umurci attajirin da ya rarrabe su, sai ya je gida yana zullumin wannan abu. Sai ga tururuwa ta zo ta iske shi cikin wannan hali ta tambaye shi sai ya shaida mata abin da ya faru, sai ta ce ya kwantar da hankalinsa za ta zo da jama’arta su yi wannan aliki da dare. Dare na yi tururuwa ta ci gaba da rarrabe hatsi daban-daban kafin safe sun qare.

Ko da safiya ta yi Waziri ya ga attajirin nan ya yi aikin da aka umurce shi sai ransa ya vaci. Daga nan ya sake qulla wata cewa ya kamata a ce attajirin ya samo zangarniyar tumu ga shi lokacin rani ne, sai attajiri ya koma gida yana tunanin yadda zai samo tumu a wannan lokaci. Sai ga shamuwa ta tambaye shi abin da ke faruwa ya gaya mata, sai t a ce masa kada ya damu za ta je wata qasa ta samo masa. Shamuwa ta tashi ta je wata qasa inda ake damina ta samo tumun gero ta kawo wa attajiri ya je ya kai wa sarki. Da waziri ya ga bai ci nasara ba

sai sai ya sake qulla wa Attajiri wani shiri ya ce wai a voye zoben Sarki a ce ya je ya nemo shi duk inda yake. Aka yi haka sai aljani ya je ya xauko zoben ya kawo wa attajiri ya ce gobe ka kai wa sarki. Haka kuwa ta kasance sai Waziri ya rasa abin da ke yi masa daxi.

Daga qarshe dai maciji da ke cikin kogon nan ya je ya sari ‘yar sarki ya ce wa attajirin idan aka tambaye shi magani ka ce da hantar Bafillace ake haxin, haka ko ta kasance Waziri ya ce a kirawo attajiri ya faxi inda za a sami magani, sai ya ce akwai magani amma da hantar Bafillace ake haxi. Da jin haka sai hankalin Waziri ya tashi, aka je aka nemi bafillace ba a samu ba har tsawon kwana uku. Daga qarshe Sarki ya ce ga abu gida ana faman wahala? Saboda haka sarki ya ba da umurni a yanka Wazirinsa domin yi wa ‘yarsa magani, hakan kuma aka aiwatar. Qurungus kan vera.

Tatsuniyar gamin gambiza ce tana xauke da mutane da tsuntsaye da qwari da aljannu. Babban jigon tatsuniyar shi ne karin maganar nan ta Hausa mai cewa “sharri kare ne mai shi yake bi”, to haka ta faru ga waziri don ya qulla wa attajiri sharri saboda ba ya qaunar sa, sai ga shi daga qarshe sharrin ya yi sanadiyyar rayuwarsa.Tatsuniyar ta qunshi jigon zamantakewa domin an nuna cewa saboda kyauyatawar da attajiri yake yi wa qwarin da ke cikin kogon itaciyar gidansa ya sa suka taimaka masa lokacin da waziri ya so a quntata masa.

TATSUNIYAR GIZO DA QOQI.

Gata nan gata nan ku.

Gizo ne dai wata rana ya je cikin gari ya ciwo bashin sa qato ya zo da shi gidansa yana ‘yan waqe-waqensa, ranar da ya yanka san sai da ya ja wa qoqi kunne sosai wai kada ta kuskura ta ci naman nan, kai ko ma qanshinsa ta ji bai yafe mata ba, qoqi ta ce “to, ba komai.” Sai gizo ya sami babban kasko da manyan itace da murhu qoqi ta ci gaba da yankan nama. Ta hura wutar da za ta

fara suyar nama sai gizo ya ce mata “chaya chaya” sai ya toshe mata hanci da auduga ya kuma cusa mata ita a baki wai don kada ta ji qamshi ko ta ci bai sani ba, miyonta na ta kawowa tana haxewa.

Abinka da qaddara ashe gizo bai yi nisa ba yana nan makewayi ya lave yana kallonta riqe da qaton jallonsa na hurar da ta sha zuma. Sai ga dila yayi sallama, qoqi ta yi sauri ta cire audugar da ke bakinta ta bi shi can waje ta amsa sallama. Sai dila ya ce mata wai abokin cinikin gizo ne ya aiko shi, ta ce mashi “halan cinikin ya tashi? ga shi bashin an yi a kan biya biyu zai yi”. Gizo da ke lave sai kawai miyau ya riqa zubo nasa ga kwaxayi ga rashi saboda an tafi da nama. Ko da aka ji abin da ya yi wa qoqi sai aka raba nama kashi biyu aka ba qoqi ladar gyaran naman, shi ko gizo aka qyale shi.

Wannan tatsuniyar na nuna rashin kyawon cin amana, gizo ya sami nama sai ya qi matarsa qoqi duk da cewa ita ce za ta yi wahala wajen gyara naman, don xaukar alhaki ma har da toshe mata baki da hanci da auduga don kada ta ji qamshi amma daga qarshe sai ga gizo ya rasa nama qoqi kuma ta samu.

ABOTAR KWAXO.

Da kwaxo da gishiri da quda suka yi abota wata rana sai suka tashi za su je jeji suna cikin tafiya sai suka iske gulbi ya gitta masu sai quda ya tashi sama ya qetare ruwa shi ko kwaxo ya shiga ciki ya wuce, gishiri da ya shiga sai ya narke suka wuce abinsu. Ana nan sai suka iske abinci mai zafi bisa hanya sai quda ya yi farat ya fara ci yana faxawa sai ya mutu, shi ko kwaxo wajen dariyar qeta sai ya kumbura ya fashe. Qurungus kan xan vera.

Tatsuniyar na koya wa yara cewa qeta ba ta da kyau, kuma ana son abokai su riqa taimakon juna a duk halin da suka sami kansu. Saboda rashin taimakawa da quad da kwaxo suka yi wa gishiri ya sha tun tashin farko ya shiga

ruwa ya narke, shi kuma kwaxo ya qi ya taimaka wa quda lokacin da ya faxa kan abinci mai zafi har ya mutu. Haka kuma tatsuniyar na koya wa yara su guji duk wani abu da zai cuce su don da gishiri ya qi shiga ruwa da bai rasa ransa ba.

CIN KASUWAR SAMA.

Gata nan ga ta nanku.

Da zanzaro da baragunxa suka qulla abota, wata rana suka je cin kasuwar sama da nufin su dawo da yamma. Da suka je suka dawo sai suka tarar gizo ya fito ya kame a kan kujera yana shan iska, da ya gan su sai ya tashi yayi musu maraba suka amsa masa har suka ba shi tsarabar kasuwa.

Gizo da matarsa qoqi suka ji daxin tsarabar, sai qoqi ta shawarci gizo da ya bi su ko shi ma ya samo kayan daxi. Gizo ya je da dare ya roqe su, da su taimake shi su je tare, sai zanzaro ya ce “kai gizo al’amarinka fa da wuya, don ka cika fallasa.” Gizo ya yi ta rantse-rantse yana cewa “ai na bar halin da kuka san ni da shi a da.” Da kyar dai suka amince suka ce gobe ya shiya za su tafi tare.

Da tsakar dare gizo ya je wurinsu ya nemi ya tashe su daga barci wai asuba ta yi, suka far masa da faxa cewa ya ya zai zo musu da tsakar dare haka? To idan haka zai musu su ba za su je tare da shi ba, domin har ya fara halinsa na zumuxi. Gizo ya dai haqura ya koma gida amma ya kasa barci ya lave a hanya har asuba ta yi, sai ga zanzaro da baragunxa suka ce masa “to gizo, ka ga za mu da kai amma ka wa Allah da annabi kada ka yi mana irin halinka gama ba ka rabuwa da lalata”, sai ya ce “wallahi tallahi ba zan yi lalata ba”. Sai kowanne daga cikinsu ya figo lili xaya daga fuka-fukansa ya xafa wa gizo suka rankaya sama. Da tafiya ta yi tafiya sai gizo ya yi kuwwa yana cewa, “wayyo Allahna yau na halaka”, suka ce “Ashsha, gizo me ya faru?” gizo ya ce “yunwa za ta

halaka ni.” Sai baragunxa ya ce da shi, ya shiga hancinsa ya sami abinci a kasuwa ya ci, saura kuma don Allah kada ya yi na ‘yan duniya ya faxi. Gizo ya ce “na sha aradu ba ni faxi” sai ya abka hancin baragunxa sai ya tarar da wata babbar kasuwa da mutane maqil ta cika, ya ci abinci har ya qoshi. Daga nan sai gizo ya karvi tallan qosai a cikin kasuwar. Can bayan wani xan lokaci sai baragunxa ya ce ”kai gizo wace irin shegantaka ke nan? Fito da lalatarka da ka saba yi, ai yanzu ka qoshi”, sai gizo ya tsaya kai da fata ya qi fitowa, da baragunxa ya harzuqa sai ya yi atishawa sai gizo ya faxo tare da faifan tallar qosan sai baragunxa ya ce masa ya koma cikin hancin ya mayar da shi. Nan da nan gizo ya shiga ya mayar suka ci gaba da tafiya. Can kuma ba gaira ba dalili sai suka ji ihu da aka tambaye sai ya ce qishin ruwa ke damun sa. Zanzaro ya ce “to shiga marata ka kashe qishinka kuma kada ka fasa ja’ircinka da ka saba”, nan ma ya rarrantse ba ya sake yin lalata. Da gizo ya kutsa kai ya shiga marar zanzaro sai ya sami ruwa irin na daxi ya kwankwaxa, ai sai ya fanxare ma zanzaro ya ce ba ya fita, bari ma ya xauraye jikinsa wai zufa ta ishe shi. Da dai zanzaro ya ga abin na gizo na rashin arziki ne sai ya matso shi ya fito ba shiri. Sai suka ce da shi “to gizo ka fa san sarkinmu sarai, don Allah sa manzonsa kada ka tona mana asiri”, gizo ya ce babu wanda zai ji ta.

Gizo fa ya kalallame su da dadaxan irin lafazozinsa har suka kai shi kasuwar sama suka ajiye shi a wata rumfa su kuma suka shiga nasu hulxoxi suka ce masa ya zauna nan har su zagayo. Tafiyarsu ke da wuya sai gizo ya shiga tara yara, kamin a yi haka ya tara yara kimanin xari ya ce wa yaran “ku zo mu tafi cikin kasuwar nan mu yi takai irin na garinmu” yara suna ta murna za su ga wani irin sabon wasa daban da nasu. Gizo ya shiga gaba yara na biye har suka kai tsakiyar kasuwa sai ya ce masu “to ni ne ma ba da waqa ku kuma ku ne yan amshi in nace maran zanzaro na sha ruwa sai ku ce hancin baragunxa da kasuwa.” Shi ke nan gizo ya xauki xan guntun sanda ya riqe a hannunsa yana rawa yana juyi yana tsalle a tsakar fage yara ko sun masa zobe yana ta faxin

“marar zanzaro na sha ruwa” yara na amsawa “hancin baragunxa da kasuwa”, sai al’amarin ya kai kunnen zanzaro daga nan ya kira baragunxa suka maqe waje xaya suna jin fallasar da gizo yake masu sai suka ce “bar shi kawai ma gamu”. Gizo yayi wasa har ya gaji sai ya kwanta yana hutawa sai barci ya share shi da suka zo suka ga yana barci sai suka ce “madalla Allah ya kama ka munafuki.” Ba su yi wata-wata ba sai suka cire fuka-fukansu da suka ara masa suka tafi abinsu.

Da gizo ya farka sai ya ga ba fuka-fukai ba dalilinsu ya yi ajiyar zuciya ya shara da gudu ya dudduba su amma bai ga ko qeyarsu ba abin duniya duk ya dame shi yana ta kuka sabili da rashin ganinsu, sai ya fara cewa “wane ne zai kai ni garinmu wo Allahna.” Sai yaran suka ce kai gizo sha’aninka da wuya ba don rashin mutuncinka ba da sai mu yi dabara mu sadar da kai da garinku, sai ya marairaice masu ya lallashe su ya ba su magana har suka yarda suka ce masa “oho in ka yi halinka da ka saba yi sai ka kuka da kanka amma ba da mu ba”.

Sai yara suka suka yi azargagiya da igiyar ramar turawa suka zarga wa ganga suka ba gizo makaxi suka gaya masa ya riqe ya xankware wa gangar idan ya isa gida ya kaxa gangar da ke riqe a hannunsa domin idan sun ji sun san ya sadu da qasa.Sai suka riqe bakin igiya suna sakin gizo da ke xankware da gangar yana nufowa qasa sai gizo ya ce a cikin zuciya “ ni na qosa in ji irin amon gangarnan ko da zaqi, lallai domin qeta shi ya sa suka ce mani kada in kaxa sai na isa qasa, ni zan kaxa ne. sai ya sa makaxi ya kaxa ta . Da yara suka ji amonta sai suka xauka ya kai qasa ne daga nan sai suka fizga igiyar ganga suka ja, gizo ko da bai kai qasa ba sai ya kufto ya sulmiyo zuwa qasa ya faxo ya kare, muguwar karaya ba don qoqi matarsa da ta cigito mai xauri ba kuma abin ya zamo akwai sauran shan ruwa a duniya da shi ke nan. Mai xori ya xora gizo ya yi ta jinya da haka ya sami ransa.

TATSUNIYAR GIZO DA VAURE.

Sarki ya nemi wanda zai tsinke nunannen vauren da ke gonarsa ba tare da ya sha ba, idan ya gama zai ba shi auren xiyarsa tare da gararta, gizo ya ce shi zai iya, sai ya hawo itaciyar ya tsinke vauren duka amma kuma sai da ya sha iyakar shansa. Shi ke nan ashe bai sani ba wata ‘yar tsuntsuwa na kallon sa .Da ya gama tsinkar vauren tas ya sauko zai tafi gida sai ya xauko jallon ruwansa ya kurkure bakinsa ya xauko madubi da tsinken sakace duk ya ciccire vauren da ya maqe masa a haqorinsa, bakinsa ya yi tas kamar bai ci kome ba, sai sarki ya aiko mutane don su xebe vauren da gizo ya tsinke suka zo suka sami gizo suka ce “sannu da aiki gizo”, yace,”yauwa”, suka ce “har ka gama?” Sai ya ce “i, amma da qyar na gama kamar na yi amai saboda warin vaurennan, warin duk ya cika mani ciki”. Sai suka zuzzuba vauren a buhunhuna suka tafi su kai wa sarki. Da suka je gida sai sarki ya tambaye su labarin gizo da tsinkar vaure sai suka ce “ai yallavai gizo bai sha vauren nan ba domin mun ga muna zubawa a buhu yana tofar da yawu kuma da muka ce da shi me ya sa yake tofar da yawu sai ya ce warin vauren ne ya cika masa ciki.

Sun gama faxin haka ke nan sai ga gizo ya iso gidan sarki, sarki ya ce da shi”to gizo ka yi aiki mai kyau sai kuma ka je gida ka gyara za a kawo amarya da gararta”. Shi ke nan gizo ya je gida ya gyaggyara sarai, aka xauko amarya da gara aka zo da ita gidan gizo, kafin ‘yan xaukar amarya su tafi sai suka ji tsuntsuwa tana waqa tana cewa:-

“Kai gizo, kai gizo,

a can ka ci vaurenka,

har ka kurkure bakinka,

har ka manto jallonka.

Tana ta faxar haka sai mutane suka ce kai ku tsaya mu ji abin da tsutsuwar can take faxa sai gizo ya ce da su “kai ku rabu da ita don Allah

shirmen ta take yi”. Sai mutanen suka ce” wane irin a rabu da ita?, kai mu tsaya mu ji” shi ke nan sai ‘yan kawo amarya da gara suka ji tana cewa:-

“Kai gizo, kai gizo,
a can ka ci vaurenka,
har ka kurkure bakinka,
har ka manto jallonka”.

Sai suka ce, “la’ila, ashe ka ci vauren ka ce ba ka ci ba?” sai suka yi ta surutu da hayaniya shi ke nan sai suka mayar da amarya da gararta gida suka gaya wa sarki abin da ya faru. Shi ke nan qurunqus.

TATSUNIYAR GIZO DA GIWA.

Ga ta nan ga ta nan ku.

Wani mutum ne dai ya ba wani malami kuxi don a yi masa asiri, sai malamin ya ce sai an samo hauren giwa domin ya haxa maganin da shi.

Sai mutumin ya je cikin jama’a ya ce, “wa zai iya samo min hauren giwa in ba shi kuxi?. Aka rasa wanda zai iya sai gizo ya ce shi zai iya. Sai mutumin ya ce “to shi ke nan sai ka samo ka kawo”.

Shi ke nan sai gizo ya je gida ya daka nakiya mai zaqin gaske sai ya je gidan giwa da xan qunshin nakiya a hannunsa, ya ce “gafaya dai”, sai giwa ta ce “maraba da gizo” y ace” yauwa, wata nakiya ce na kawo maki da na samo a pa”. Shi ke nan sai giwa ta ce,” to”. Ta gutsuri nakiya ta kai bakinta, da ta ji zaqin nakiyar sai ta ce, “don Allah gizo ni ma ka raka ni in je in samo”, sai ya ce “haba yaya me zai hana?, ki zo gobe in kai ki”.

Shi ke nan sai ta zo washegari suka je wajen kan pa, sai ya ce da ita”idan kika doka bakinki sau xaya, kika doka sau biyu, a na ukun za ki ga nakiya ruvus a bakinki”.Sai giwa ta doka bakinta sau xaya fas a kan pa, ta kuma dokawa da ta doka na ukun sai haqorinta ya valle ya faxo qasa sai jini shar, sai gizo ya ce, “assha, assha, ya ya aka yi haka kuma?” ya yi maza ya xauki haqorin giwar ya sa a aljihunsa ita ba ta gani ba tana ta kanta. Sai gizo ya bar giwa a nan ya yi sauri ya kai wa mutumin haqorin, shi kuma ya ba shi ladansa.

Sai gizo ya je jeji ya tattara namun daji suka je gidan da giwa ta ke a kwance, suka tarar kanta ya kumbura suntum. Sai gizo ya gaya wa namun dajin “in na ce babbanmu da givi ku ce vurum vavurka”.

Sai ya fara waqa:

Babbanmu da givi,

Sai suka amsa:

Vurum vavurka.

Shi ke nan sai suka gama, suka koma gizo ya bar giwa da wahala shi kuwa ya karve kuxinsa.

TATSUNIYAR XANKAXAFI.

Ga ta nan ga ta nan ku. Wannan ce dai ba ta tava haihuwa ba tun da ta ke. Sai ta ce “Allah, Allah ba ka ba ni xa ba ko da Xankaxafi ne?’, sai Allah ya karvi roqonta ta haifi xanta namiji.. Shi ke nan yaro yana nan yana girma sai rannan ta goya shi, da ta gaji da goyo sai ta ce da shi ‘to sauko ka kwanta xan inna’. Sai ya ce “mhn a baya”. Sai rannan ta ce “kai ni dai na gaji, gun malami za ni ko yana da abin da zai yi mini in rabu da xan nan, na gaji”. Sai ta je wajen malami, malami ya ce “duk abin da aka gaya miki kya iya?”, sai ta ce “i, zan iya”, sai ya ce”to sayo sa guda ki kawo mini”, sai ta sayo sa ta kai wa malami. Sai ya ce “to biyu zan raba, ki xauki rabi in xauki rabi”, sai ta ce “to”. Aka raba

naman sa kashi biyu malami ya xauki rabi ta xauki rabi. Sai ya ce “ki soya wannan ki tafi da shi daji ki haxa da majanyi da zane in kin sauko yaron yana cin naman sai ki gudo ki baro shi can”. Ta je gida ta soya nama ta tafi daji da shi ta ce “xan inna xan inna sauko ka ci nama”, sai ya ce “mn a baya”, sai tace “ga naman naka nan sauko ka ci”, sai ya sauko yana cin nama sai uwar ta waiga ba ta ga kowa ba sai ta gudu ta bar shi da majanyi da zane, fatar bayanta har ta kwaye saboda goyo.

Shi ke nan sai ga kura ita da ‘yan uwanta suna wasa sai ta ce, “xan qanena sam min nama in ci in goya ka”, da ya ba ta sai ta xauke shi ta goya,da ta ce “sauko in huta ” sai ya ce “mn” a baya. Kome ta ce sai ya ce “mn” a baya, daga qarshe dai ta kira ‘yan uwanta suka cire mata shi da qyar har fatar bayanta ta ciro, suka gudu suka bar shi nan. Can sai ga dodo, ya xauke shi ya xora bayan dokinsa. Suna cikin tafiya a daji sai gizo ya ga dodo da yaro, saboda shiga uku da ya saba sai kawai ya sauke yaron qasa, shi ya haye dokin dodo. Suna cikin tafiya sai kurciya ta ga gizo a kan dokin dodo sai ta ce da gizo” ku ne a yi muku rana ku yi wa mutum dare”, gizo ya ce “ba zam yi miki ba”. Shi ke nan sai kurciya ta xauke shi a fiffikenta. Qurungus.

TATSUNIYAR MACIJI DA KUNAMA.

Wata rana kunama ta je wajen maciji tace ya ba ta dafi wanda in ta harbi mutum ya mutu. maciji ya ce, “ke kunama ba na ba ki, don na san fushi gare ki, in kika sami wannan magani za ki qare dukkan mutane.” Kunama ta ce, “a’a a hankali zan yi.” Maciji ya ce, “to na ji, je ki sai gobe idan na yi shawara ki komo.” Da gari ya waye maciji ya tafi shan iska sai kunama ta zo ba ta same shi a gida ba, sai ta shige raminsa ta lave. Da ya komo garin shiga sai ya danne kunama,da ta ji zafi sai ta harbe shi. Zafi ya kama shi ya yi nan, ya yi can, ya rasa inda zai sa kansa ya ji sanyi. Sai kunama ta ce masa “me ya same ka?” maciji ya ce “mai baka yaushe aka sauka?”. Ta ce “tuni na zo, ban cim maka

ba”. Maciji ya ce, “haba rabu da ni, wani abu ya harbe ni cikin xakina.” Sai kunama ta ce “ni ce da ka zo shiga ka taka ni, da na ji zafi qarina ya soke ka.” Maciji ya ce, “haka ne, to fita ki ba ni xakina, na fasa baki maganin, im baki kawai ki qare mutane? ’ Sai kunama ta fita ta bar maciji yana mirgine-mirgine.

TATSUNIYAR QADANGARE DA ABOKANSA.

Qadangare da quda da gishiri da man kaxanya suka yi abota. Wata rana suka yi shiri suka tafi yawon neman arziki ganin cewa fatauci na jayayya da su sai sauran maqwabtansu suka riqa yi masu dariya da kallon hadarin kaji. Suka yi sammako suka fita gida, can zuwa rana tsaka sai zafin rana ya kama man kaxe nan take ya narke, sauran abokan tafiyarsa suka yi ta yi masa dariya suna cewa tasa ta qare. Jim kaxan sai ruwan sama ya kufce, nan take sai gishiri ya narke kamar da xai duniya ba a tava yin sa ba, da quda da qadangare suka yi dariya suka wuce gaba. Ba a daxe ba sai suka tarar da wani majemi an kawo masa abinci mai zafi yana jiran ya sha iska sannan ya ci, sai quda da ma “wajen qwaxayi yake mutuwa” ya yi suka ya faxa cikin abincin ya mutu, sai qadangare ya yi ko oho da abin da ya faru ga quda yana ganin laifinsa ne. Qadangare ya shiga duniya neman arziki ya ko samo sa’a don ya samo abinci iri-iri waxanda za su ishe shi tsawon rayuwarsa kamar su shinge, da kiyashi da shazumami da sauransu. Sai da ya gama wahalar xauko kaya ya kawo gida sai ya tarar da wani qasaitaccen muzuru yunwa ta koro shi daga gidansa bai yi wata wata ba sai ya dafe qadangare ya cinye.

Wannan tatsuniyar na nuna idan wata masifa ta faxa wa wani na kusa da kai kar ka yi murna don kai ma tana iya faxa maka.

.

2. RATAYEN WASU HIKAYOYI.

Wasiyyar Uba cikin Hikima.

Wannan hikayar ta qunshi labarin wani mutum wanda kullum yakan riqa yi wa xansa wa'azi kan sha'anin zama da mutane. Kafin uban ya rasu sai ya ce wa xansa "wataqila wannan ciwon nawa ba na tashi ba ne, saboda haka akwai wasiyyoyi da nake so in gaya maka amma zafin ciwo ba zai bar ni ba, don haka idan na rasu ka je wajen tsohon doki da kiyashi da kumurci da kare za su gaya maka abin da zan gaya maka. Bayan uba ya rasu da yaro ya je wurin kiyashi ya faxi masa dalilin zuwansa, sai ya ce "lalle akwai wasiyya kuwa, biyo ni ka ga abin da yake nufi", suna tafiya sai suka yi kicivis da mushen kyankyaso. Kiyashi ya ce, ka ga wannan mushe ba shakka ya raba ni fiye da xari a girma saboda haka ba zan iya jan shi in kai ramina ba, ga shi kuma ina so saboda abincina ne. Yaro ya ce "i, gaskiya ne" kiyashi ya ce "tsaya ka gani" nan take sai ya kirawo kiyasai 'yan uwansa rututu, nan da nan suka gewaye mushen kyankyaso suka ja giriri, har cikin raminsu. Yaro ya ce "to me ke nan", kiyashi

ya ce “komai za ka yi kada ka yi kai kaxai sai da jama’a, jama’ar kuma taka, wannan ita ce wasiyyar mahaifinka”. Sai ya nufi neman kumurci, da qyar ya same shi a cikin kogon kuka, ya faxa masa abin da ke tafe da shi. Sai kumurci ya ce masa, “babu shakka babanka mutum ne mai tsinkaya, yanzu ka ganni nan a voye ba na fita da rana, kuma ko da daddare sai an yi barci domin in ba haka ba da an ganni sai a bi ni da duka a kashe ni. Ka san dalili? yaro ya ce a’a, sai kumurci yace “harshena da bakina suka jawo mani wannan bala’i don haka ka kiyayi harshenka da bakinka, abin da babanka yake son ya gaya maka ke nan”, yaro ya yi godiya yai sallama ya tafi.

Zaman Sauro tare da Kunne da Hannu.

Sanannen abu ne sauro ko da yaushe yana zuwa wajen kunnen mutum yana kuka kamar zai shige ciki kuma ko yaushe hannun na kai kora. To game da wannan, masu hikima sun ba da labarin cewa dalilin wannan shi ne, akwai lokacin da sauro da kunne da hannu suke zaune a gida xaya, kullum da safe sai kowannensu ya tafi wurin sana’arsa. Wata rana hannu ya tashi ba lafiya sai bai je wurin sana’a ba, da rana ta yi sai ya fara jin yunwa kuma ga xakinsa ba komi. Saboda haka da ya leqa xakin kunne ya hango gari, sai ya shiga ya xebo. Yana fitowa sai ga sauro ya dawo. Hannu ya roqi sauro ya rufa masa asiri, kada ya gaya wa kunne abin da ya faru. Wata rana sai husuma ta tashi tsakanin sauro da hannu. Har hannu ya yi wa sauro ba’a, sauro ya fusata ya ce wa hannu “Tun da ka zage ni sai na gaya wa kunne kai ne ka sace masa gari”. To shi ne kullum sauro ya tafi ya gaya wa kunne wannan magana sai hannu ya kai masa duka, har yau xinnan dai abin da ake ciki ke nan.

3. **Ratayen Wasu Karin Maganganu**.

1. Take-taken da ake yi a gidan galla ba za a yi shi ba a gida rina.

2. Kiyashi ya ce inda mutum ya zauna ya yini ya fi inda giwa ta shekara.

3. Zuma ga zaqi ga harbi.

4. Xan kunama ne ba don mutum guda ya ajiye qarinsa ba.

5. Daji bai gama ci da wuta ba, fara ba ta yi wa ‘yar uwarta fara barka da arziki.

6. Biyan buqata ya fi rai, in ji quda, da ya hango abinci mai qyau da zafi ya yi suka ya buxe bakinsa ya lasa, amma ya mutu.

7. Wurin bin zaqinnan aka kai mu guri aka kashe”, in ji shazumami.

8. Qwarin qasa sun ce ba zama wuri xaya da kaza ke yi musa ciwo ba, yawan tone-tone.

9. Idan ka ce ‘yan qananan matsaloli ba kome ba ne, to ka kwana xaki xaya da sauro

10. A bugi juji don a ji qarar gwazarma.

11. An yi gudun gara an faxa gidan zago.

12. Ba ba’a ce ta kashe uwar gizo ba, sarautar Allah ce.

13. Idan mutum bai fi ka tsumma ba, ba zai sa mata kwarkwata ba.

14. Tatsuniyar gizo ba ta wuce qoqi.

15. Allah mannanu, quda ya faxa qwaryar alewa.

16. Wane xan kunama ne ba xan goyo ba.

17. “Ana shaggu a qasa”, in ji raqumi da ya taka kunama.

18. “Shegen ko motsi ba a yi”? kunama ta harbi kasko.

19. Ba a shan zuma sai an sha harbi.

20. “Biyan buqata ya fi rai, in ji quda.

21. Idan dare ya yi dare buzuzu ma nama ne.

22. Ina qudan ya ke ballantana romonsa.

23. Kai kuma waye? kiyashi a jirgi.

24. Kara da kiyashi xaukar marar sani.

25. Kowa ya raina gajere bai taka kunama ba.

26. Quda ba ya bin kayan gawayi.

27. Me gara takan yi da dutse.

28. Me ya gama kifi da kaska.

29. Mu ga ta faxi, kuxin cizo ya kada kyankyaso.

30. Rai dai, an cire wa fara kai.

31. Shashanci, roqo gidan babe.

32. Gyangyaxin kunama, kowa ya tava ya sha kashi.

33. Mahauta biyu, vata hankalin quda.

34. Gwano ba ya jin warin jikinsa.

35. Gurguwar tsanya da wuri takan fara haqai.

(4). Ratayen Wasu Camfe-Camfe.

1. Idan kunama ta harbi mace marar ciki, to lalle a wannan watan za ta sami ciki.

2. Wai idan mutum ya qetara gidan tururuwa, zai xauki aljannu.

3. Wai idan mutum ya yi birgima a gidan tururuwa, zai zama mace.

4. Idan aka rusa shuri, za a kamu da ciwon qafa ko ciwon hannu.

5. Hausawa sun camfa cewa jan kiyashi yana kawo alheri, amma baqin kiyashi ba ya da wani amfani.

6. Rozozi (dangwalin goro) wani qwaro ne mai baki biyu. Hausawa sun camfa shi da cewa idan har ya ciji mutum, to wannan cizon sai ya jawo asarar dukiya ko rai ga shi wanda aka ciza, ko wanin shi.

7. Hausawa sun camfa qwalqwasa da cewa tana korar duk wani azzalumi. Wannan ya nuna ke nan duk inda ka ga qwalqwasa, to azzalumi ba ya iya zama. Saboda haka ne ma suke mata kirari da “qwalqwasa, fid da mai gida daga gidansa”.

9. Idan aka zubar da vawon gyaxa ko ina a gida za ya jawo kunama.

10. Barin kwarkwata a qasa na sa girgizar qasa.

11. Duk mai sarar kashe tururuwa babu dalili to zai ci karo da matsala a rayuwarsa.

12. Duk wanda qwaguwa ta ciza, idan bai lashi takashin makeri ba, ba za ta sake shi ba.

13. Yawan kwarkwata ga yaro na nuna alamun arziki in yaron ya girma.

14. Ganin gwano ga matafiyi alamar ce ta sa’a.

15. Ganin tururuwa a lokacin da ake kai amarya gidan mijinta alama ce da ke nuna sa’a ga amaryar, kuma zata samu duniya.

16. Ganin tururuwa ga matafiyi alama ce ta samun nasarar tafiya.

(5). Ratayen Wasu Waqoqin Baka.

1. Waqar Sauro ta Babangida Kakadawa.

Gindin Waqa: Sauro uban tsarguwa,
Sauro da mugun hali.
Jagora: Mhn amman da mugun hali,
Abu ga shi xan qanqani,

Amman da mugun hali,

Wannan qwaro akwai tsarguwa,

Sauro uban tsarguwa,

Sauro da mugun hali.
Idan dare yai dare,
Da ka ji cizo a dama,
Ko ka ji cizo a hagu,
To kar dai kai tambaya,
Wannan qwaro akwai tsarguwa,
Sauro da mugun hali.
Shi za ya tashi sama,

Ya xebi jinin marar lafiya,
Ya kai wa mai lafiya kuma sai ya sanya ciki.
Likitota abin taimako ku ba mu medicin cizon sauro da Poison ciki.

Mai sa malariya,

Sauro uban tsarguwa.
Turawa da sun kai mitin,
Fulani ma da sun kai mitin,
Hausawa ma da an kai mitin,
Sun ce ba cizon ba ne tsarguwa,
Kukansa ne tsarguwa.
Kuma bai tashi cizon ba sai a tsakiyar dare,
Don dai hana ai barci.

Gwamnoni da jiniya ba su kamar tsarguwa.

Sauro da mugun hali.

'Yan road safety da jiniya ba su kamar tsarguwa,

Sauro da shegen hali.

Shugaban qasa da jiniya babu kamar tsarguwa.

Sauro da shegen hali.

Ya Allah ka kare mu dai, cizon sauro da poison ciki.

Idan dare yai dare kan ga qato fahim, kan ga qato zuru,
Shi yai hana yai barci.
Mai sa qato ya mari kansa, kuma can a tsakiyar dare.
Na gaida shegen xiya sauro uban tsarguwa.
Bai kyale yara ba bai kyale manya ba, kowa ma cizo yake,
Bai bar amarya ba, kuma bai kyale angonta ba.
Sauro uban tsarguwa, Ya Allah ka kare mu dai,
Cizon sauro da poison ciki.

2. Waqar Gidan Haya ta Babangida Kakadawa.
   Jagora: Gidannan ba gida ba ne,
   Matsala dai ne gidan haya.
   Sai kana can gefen gari,
   Jibi ka je bixar wuri,
   Don kana gudu a yi ma notis.
   Jagora: Tun farkon asalatun,

Duk tsuntsun da ya ke sama,
Ya gina gida nai ya shige.
Qwarin da su ke tudu,
Kowane ya yi gidanai ya shige.
Qwarin da suke ruwa,
Har ta qwarin da suke tudu,
Kowanne ya yi gida nasa ya shige.
Misali tun ga zanzaro,
Ga shi abi ne xan qarami,
Ya je daji ya ja qasa,
Ya xebo ruwa nana ya haxa,
Ya gina gidansa yana shiga.
To kai matsayinka na xan'adam,
Ya za ka tsaya a gidan haya.
Gidannan ba gida ba ne,
Matsala dai ne gidan haya.

3. Waqar Ina Bakin Kogi Kada na dibi na. Ta Babangida Kakadawa.
   Jagora: Ina bakin kogi kada na dibi na.
   Yana ta harara na.
   Jagora: Sai na tambaye shi,
   Mene ne nai ma,
   Ashe wasu masunta,
   Suka kashe mai xa,
   Sai na ce mai,
   Ko tsari ba na ci,
   Bare in kashe ma xa.
   Ya kyale ni na faxa gulbi.
   Na cika gora na.
   Na cika tumbina..
   Jagora: Ni dai Babangida,
   Rannan na tafi ina kamun kifi,
   Na iske qwaguwa,
   Sai nac ce qwaguwa ina kwaxxo yay yi,
   Sai tac ce min,
   Qwaxxo na can tudu,
   Yana kama tururuwa,
   Qwaxxo mai zafi ya kaxa bakinai,
   Da ya xau mai zafi,
   Ya sa bakinai,
   Sai ta halbali na xai,
   Sai yai tuma tuma tuma sai yai shiru,

Sai ta qara main a biyu,
Sai yai tuma tuma tuma yai shiru,
Da ta qara mai na uku,
Ya watse kaca-kaca.

4. Waqar Kunama ta Garba Maitandu Shinkafi.
   Amshi : Kunama zan wa kixi
   Zaman ciwo ag gare ta.

Uban waqa: Na ga gidan Takulbi.

Amma jiya na ji Sakkwatawa sun ce
Gado ruhewa nan na ta ke.
Kanawa sun ce haba
A gindin dutse ta ke.
Su ko 'yan Hausa sun ka ce
Ga ciyawa ta ke.
Buzu ya ce gali
Ga gindin rogo ta ke.
Xiyan yarbawa suna faxin mololni haba ga gindin kwakwa ta ke.
Hillani na faxin cikin darme ta ke.
Maraxawa na faxin haba basu gane ba
Duk ga tankan xaki ta ke.
Buzu ya ce bari-tani-bakekemba.
Ko'ina dai xakinta ta.
Turawa na faxin sukopiyo 'yar baya ce.

Uban waqa: Sarkin noma ya na noma nai.

Ya gama noma nai kunyar da za ta tashi.

Yas sha qari,

Da ta halbai ya aje kalme.

Sai yaz zuba yana ta gudu,

Yab biyo wajen Alhaji ya ishe shi.

Yac ce mai lahiya,

Kai dai ce in ban mace ba yau ban mutuwa.

Uban waqa: Alhaji ya ce Isya ka daina raki.

Sarkin rawa ya ce,

In ka zo gida,

Ka shaida wa manyan gari.

Su sa wani Sarkin rawa,

Zaman ni kan na wuce.

Uban waqa: Shin ina zancen guxa,

Wanda ab bakin kasuwa,

Tsoho mai lailaya,

Ashe tsoho bai sani ba,

Ya dahi mai gadon qari,

Da yaz zo ya ce ya yunqura,

Tac ce ba zuwa,
Da jan gindi na da rarrahe,
Sai yak kai xaka,
Da yaz zo yac ce.
Tasalla ba ni hura in haxa.

Uba da yara: Yawanci raina iyaci nai yau,
Gobe ke kina girki,

Ni ina qiyama,

Kowam mace,

Bai rasa'yam maishe-maishe,

Zawo ko bai yawa ba,

Bakin da mai cikin kwatami,

Sai na yi shi.

Amshi: kunama zan wa kixi,

Zaman ciwo ag gare ta,

Ta halban jiya.

Uba: yaro xa xan gidan malamai,

Da tah kahwa mai bindi,

Ya aje littafi yai yi kwance yac ce,

Yo na mace bixo allo,

Garba na ji ya ce qul'auzu ba ta fid dani,

Sai in na samu ta yi sauqi,

Mugun dahinta ya kammin.

Uba da yara: 'Yar kazan uba, yar danqon uwa,

Ta kulva ta sa malam gudu,

Ya bar allo nai qasa.

Amshi: kunama zan wa kixi zama ciwo ag gare ta,

Ta halban jiya.

Tambayoyin Bincike.

1. **Mene ne Qwaro?**
2. **Gida nawa suka kasu?**
3. **Waxanne daga cikinsu ne ke yin qwai?**
4. **Waxanne ke Haihuwa?**
5. **Ina ne mazauninsu?**
6. **Me ce dangantakarsu da Bahaushe?**
7. **Ta yaya suke lalata amfanin gona?**
8. **Ta yaya suke cutar da dabbobi manya?**
9. **Ta yaya suke cutar da xan'adam?**
10. **Wane amfani qwari ke yi wa Bahaushe?**
11. **Kawo misalan qwari a adabin baka.**
12. **Kawo misalan qwari a al'adar camfi.**

RATAYEN HOTUNAN WASU QWARI

Tururuwa

Kunama

Gyare

Qudan Zuma

Gidan Zuma

quda

Qwazaza

Bobo

Malam Buxa Littafi

Kyankyaso

Qwaguwa



Shinge

Kunama

Kaska

Qoki-qoki

Fara

Gungura kashi